*🎋✨ZUMA DA MAD'ACI🎋✨*

Na
*Maman teddy🧸*

*ALHERI WRITERS ASSO.*

*A.W.A*

https://www.facebook.com/100186388252056/posts/100188104918551/

```Kungiya masu aiki da nazaru da ilimi,Alheri sai dan Alheri```

________________________________

*Episode 1&2*

~Happy sallah to  muslim Al'ummah,Allah kabamu falalar watan ramadan Ameen summa Ameen....~

*ABIN ALFAHARI NA*
Gare ku iyaye na,Abin Alfahari na,ina matuk'ar godiya abisa tarbiyan da ku ka bani,Allah yak'ara nisan kwana Ameeen ya Rabil Alameen.

Wannan littafin sadaukar wane ga duk wani mai kaunar labrn Mmn teddy🧸, wannan yar k'aramar kuma Babban su,wanda ta saba nishad'antar daku da dadad'an littafan ta,mai sanya ku nishad'i da faranta ranku don nasan tabbas baxaku manta da littafin ta mai suna. *YAR AIKI* ba, Ga kuma uwa uba *DIJAMA Y'AR FULANI* Hmmm ummmm ga kuma *BINTOTO* Hmm wannan shiru xanyi don nasan bakwa buk'atar sharhi dan gane ga wannan book d'in... To a yau ita ta taho maku da sabuwa mai dauke hankali da kuma sanyaya xukatan ku, wato *ZUMA DA MAD'ACI* Dajin sunan kunsan da badak'ala, labrn da ya xo maku da sabon salon,don Alkalamin ba irin tasu bace, ku dai keep following💃. Don tabbas xuma da Madaci shidin ko a littafan wannan marubuciya na daban ne📘❤️.

wannan book kaman yanda kuka sani ta kudi ce labarin,Zaki turo #200 VIP, #300 SPC,#100 NORMAL. Duk ta k'ark'ashin wannan number 08081202932/ 09137392680.

*________________________________*
```

*بسم الله الر حمن الر خنم*

⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜⚜

Tafe nake ina mai yin wani irin sauri kaman zana tashi sama,ta kalmin k'afa ta ko wato slipers tuni suka sid'e kasan ya cinye,amma saboda tsantsan rashi da talauci ya hanani siyan wasu. babu muryan wanda t
nakeji yana mani amo a kunnen na irin na Oum Rabi. K'wallah ne ya fara xubo wa a kan fuska ta,ina mai tunanin abun da xan tadda a cikin gidan namu. bana ko iyah kallon gaba na,buri na shine na ganni a k'ofar gida kawai.
Ga kuma tunanin Hajiya Zaituna da ya dame ni,don nasan yau tabbas zan fuskan ci hukunci a bangaran aiki na dana saba yi mata a cikin gidan ta.
Da wannan tunanin na riski gida, bin gidan namu nayi da kallo, a raina ina cewa" Allah sarki marayun Allah kenan,ko mu duniya ya xata kasance damu. tsayawa nayi ina mai kare ma gidan kallo,kaman wannan shine ganina na farko da shi. Wasu bulo suna mai gab da watsowa garun ya rushe,ga shi ko ina na garun ginin k'asa ne. bin kofar gidan namu nayi da kallo,abun ma anan tafi lalacewa don k'ofan falangyene,shima ya rabu da jikin shi,amma har ilah yau Ankasa gyara shi. girgixa kai nayi kurum ina mai sharan gwallah,sannan na kutsa kai ixuwa cikin tsakar gidan namu. Komai tsaf kaman ba mune muke cikin tsantsan ta lauci ba. Saurin shigewa Daki na nayi,ina mai godiya ga Allah da yasa Ban had'u da Zaid ba. da6e k'afata take a tur6ayan dakin da nake kwana,don ko arxikin Siminti babu,can gyefen yar filangyen Katifa ta na nufa hadi da dauko wani buhun gana must go,da yan kayana ke ciki wanda gaba dayan su basu kai Guda 5. duka kodaddun a tomfofi ne,sai kuma rober atampha guda biyu shima,wanda sam bana son saka shi saboda kama mani jiki da yakeyi. D'auko wasu fararan kaya nayi masu kama da uniform ina mai saka shi jikina,sai kuma arsh din hijabin da baifi iya kugu na ba,nasaka ina mai xura safa kaman wanda xan tafi makaranta. wani farin ta kalmi na saka,gaba daya na fito kaman yanda Hajiya Zaituna ke bukatan ganin ko wani ma'aikaci na cikin gidan ta.
Kaman daga sama naji muryan Zaid yana bala'in da yasaba yi a kaina.
Oummah wai Suhaimah ta shigo kuwa,ko ko tana can yawon banxan nata. kallon sama da k'asa Oummah Rabi tayi masa sannan ta ta6a baki tana cewa ina xan sani,nima dan uban ta jiran ta nake tayimun sukola. ta fadi tana mai cigaba da watso da kayan dattin ta. cike da rawar jiki nayi saurin fitowa daga d'akin jikina banda rawa babu abun da yake yi. Murya na rawa nace Oummah Barka da gida".
Cike da masifah ta dago kai tana cewa" au dama kin dawo?. ehhh nace da itah a takaice inah mai nufan ta da karban kayan dattin hannun ta,ina fadin Oummah bara nayi sauri na wanke kayan!!!. Shiru Oummah tayi don so da yawa idan tafara mata fitina,yanayin sanyin suhaimat sai yasa tayi shiru ta tsaya tana mai tunanin Rayuwar ta itah da d'iyar nata Suhaimart. Shiru tayi kawai sai Muryan Zaid mukaji yana cewa" Kehhh Suhaimart Ina kudin da nace kije ki nemomun iyeh? ya fadi cike da masifah da kuma muryan Yan Allah ka shirya. Oummah na ne ta kalle shi cike da masifah tafara cewa" Fita idona na rufe Zaid, Suhaimart ne xata nemo maka kud'in da

xaka sha abun shaye$^2$? ke dama bana ce kar ki fita kije ko inah neman masa kudi ba,koda ko kasheki zaiyi da duka?. Jikin a ne yahau ky'erma a sanyaye cike da sanyin murya ta nace" Oummah don Allah kiyi Hak'uri.

Tsaki Zaid yajah hadi da ficewa yana mai banbami bata nemo masa kudi ba. Itako Oummah sai da ta gama tsitsayamun tsiya sannan ta bar tsakar gidan hadi da nufan soron ta.

Bayan shigewanta ne na tsaya ina rarraba ido,nan take komai tun daga farko ya fara dawo mun I LOVE YOU SUHAIMART".I LUV U TOO HUDAY,. gigif nayi ina cigaba da aikin da Oummah ta bani inayi ina tunanin shikenan Huday ya mutu baxai dawo gare ni ba. hawaye ne yafara bin kuncinta. a haka na kammala wanki na,sannan ko d'aki na ban koma ba,nayi saurin nufan gidan Hajiya Zaituna.

Tun daga nesa nake bin Tanfatsetsen gidan da gabaki d'ayan sa kewaye yake da Sojoji kasancewar mai gidan Soja ne Babba,wato Gen. Yak'ub d'an larabawa... cike da sauri na kutsa kaina ixuwa wajen gate din, Da isana nan Sojojin da securities kowa ya Hau kiran suna na Suhaimart" Suhaimart..." cike da smilling face dina wanda yasa dimple dina suke k'ara shigewa ciki sosai,wasu ina bin su da murmushi wasu kuma ina gaisar dasu da ce masu Barkan su da Rana". Kafin su bani amsa nayi saurin shigewa cikin dank'areren gidan hadi da nufan side din Doc. Zaituna da yan aiki irina suke acan suna mata hidima,don dama mu anan barayin ta muke mata aiki. Dai$^2$ wani coridour ne a palourn ta daya gaji da kayan alatu da more Rayuwa,komai ka gan shi a falon kud'ine d ya amsa kudi, komai na falon na zamani da tsantsan wayewa komai a falon Jah ne da milk. sai tum$^2$ da aka jera su a tsakiyan falon yyn dana Hango Doc. Zaituna zaune ta wani kishingid'a tana aikin isan k'adagin da tasaba,domun Doc. Zaituna irin matan nan ne masu isah da izzah,gata da iya gadara da arxik'i don a ganun ta a kullum talaka bawan tane,domun kudi xai mata komai a rayuwa,a ganin ta har mutum xata iyah siya.

Koda na shigo falon a sanyaye cikin takona na a hankali na tako inda Maikatan irina suke a tsaye,ko wanne sanye cikin shigarta na masu aikin wato farar wando,riga da hijaab Arsh colour iya kafad'a. yanda kasan mutum bai shigo ba haka Doc. Zaituna ta nuna don daukan ruwar roban gaban ta tayi tana kora ma makoshin ta. sukuwa sauran ma'aikatan kowa duk'ar da kansa kasa yayi yana mai tausaya mun,don ansan fitinan da xan sha a yau mai yawa ne,don karamun laifi kayi xata ce tayi maka dedoction din salaryn naka. Oumu Sulaym ne tahau washe mun Baki tana mai cewa a hankali Besty Suhaimart dina xonan. tana nuna mun inda take tsaye....

A hankali na matsa inda oummu sulaym take,ina mai gaisar da Hajiya Zaituna tunda sunan doctor ce mu kirar ta muke da Hajiya Zaituna, Ya tsina baki tayi kan daga bisani ta cigaba da bayanin ta batare da ta amsa gaisuwan nawa ba,don ita haka halaiyar ta ga talaka yake,samm bata son talaka,bb mahalukin da tafi tsana a rayuwar ta irin talaka,don ko fadin sunan talaka ba tayi,sai dai tace gayyar fitina". Wannan kenan,ban wani damu ba,nasaki mata murmushi don dama wannan dabi'a tace, Muryan ta naji tana cewa" Okay don haka tun daga yau a fara shirin tarban d'ana. banason kuringa mun shirme don xan sallami mutum kuje can gidan iyayen ku kucigaba da cin k'asa,ta fad'i tana tabe baki,sai da ta bata mana kusan 15 muna a tsaye sannan tace mana,ku wuce ku bani wuri. Mhiss Caterine ne ta hau ce mana kowa ta koma bakin aikin ta. sum$^3$ duka muka fara nufan bakin aikin mu,wanda Mhiss caterine ta kasance itace shugaban mu wato yan aikin Haj. Zaituna don aikin mu shine shara goge$^2$ cleaning dakuma Cooking.

Nufan side din mu maikata mukayi nida Oummu Sulaym don ana cewa mu wuce taja hannu na

tana nufan wani side da aka bamu mai kama da Resting room. Tun a hanya tafara kallo na tana mai cewa" ohh ni Sulaym wannan duniya ina xata kai mu ne Besty!?, Ace talaka ya koma yanda kasan bawa daga aiki,ae wlh wannan Abun da ake mana ko bayin gidan sarki baxa'a masu haka ba, sai kuma ta dora hannu a fuska tana mai rafka ta gumi,wanda nidai ban da murmushi babu abun da nakeyi mata. A haka muka shiga side din mu dai² na zauna ne tayi saurin cewa" Besty wlh har nafara tunanin zuwa mune mi aiki a cikin gidan sarkin Zaria,sarki mai Adalci kenan,mai mayar da bawa tamkar d'an gida. Jin yanda Sulaym ke xubo xance kaman wanda tasan sarkin yasani washewa da dariyan da ban shirya ba,don so dayawa ko banjin dry, Shiyasa kuma a kullum nake kara jin k'aunar Sulaym a xuciya ta. Kallona Sulaym ta tsaya tayi galala da baki tana yi tana mai bin dimple da Hushirya ta da duk suka bayyana da kallo. Lumshe segxy eyes din ta tayi tana mai cewa" washh mashaallah gsky besty na Allah yy maki kyau matuk'a. Riko hannun ta nayi ina cewa" Hmm kedai Sam Sulaym bakya gajiya da surutu kaman gidan radio. Dariya tayi don Sulaym irin yaran nan ne washa,komai abun Dariya koda kuwa bata ranta kayi sai dai tayi murmushi. shiyasa halin nasu yaxo d'aya da Suhaimart, ita dai kawai bata da Hayaniya ne,itako Sulaym ta iya shi.
Dafata nayi ina cewa" Sulaym don Allah ki taso muje mufara aikin mu kinga Hjy. Zaituna yanxun ta gama fad'a fah.
Ban rufe Baki ba ne Oummu Sulaym tace" Hmm ai wlh munga banu,don bamu fara rayuwar ta kura ba,yanxun ne xamu fara. Kallon ta nayi ina mai cewa" habawa Oummu Sulaym kowa na son sassauci ke kuma kirar mana bala'i kekeyi?. tabe baki Sulaym tayi hadi da fara mun mgn cike da muryan rada saboda gulma,nan ta fara cewa " ke Suhaimart kenafi tausaya mawa. komai kina yin shi too lazy,a kasalance gashi wannan D'an nata baya da mutunci ko kad'an wlh sai mun gunmace xama da Uwar sa abisa shi. ga miskilanci issah da wulakanci...Uhnm tom Sulaym ai sai muyi kokari mu kiyaye duk wani abu da xai sa muja mawa kanmu matsala. Wai dama tana da yara?. nayi maganar ina mai d'an ya tsina baki na. Oummu Sulaym ne ta bani amsa da,tab kedama baki sani ba,ba yara ne dayawa take dasu ba,guda d'aya Allah ya bata shiyasa suke kaunar dan kaman su lashe,kuma wama yace maki yaro ne? tom Saurayi ne wanda akallah xai kai shekaru talatin xuwa da biyu a duniya. ke samarin nan irin butters masuji da Gayu da tashen kudi,hmmm Kedai Suhaimart bari,ni ne nake fada maki shi din ajin karashe ne,wlh Ajin Sir Khaleed yana burgeni. Amma abu daya kebani haushi da shi shine son mata duk da matan ba irin su mu bane,Yara yayan masu dashi su xaki ga sunyo parcking a haraban gidannan kullum indai ya dawo, kowa so take tayi mu'amalan banxa dashi,shikuma dan iska sam baya gajiya,ni ban taba ganin Harijin fitinannan mutum Kaman Sir Khaleed ba. Shiru Nayi na wucen gadi,tom irin gidan danaxo aiki kenan. Muryan Sulaym ya dawo dani daga duniyar tunanin da nakeyi. Cigaba tayi da cewa " Kuma kinsan abin Haushun ma? ta fadi tana kallo na. Girgixa mata kai nayi alamar A'a. wai Hajiya Zaituna cewa ma take yara mata sune sukw bibiyar mata d'a,su suke neman lalata shi. Haka xatayi ta bala'i tasa ayi ma yara koran kare,don wata xubin intana gida har sawa take a sakar masu kare,cin mutuncin duniya amma bashi xai hanasu gobe su dawo ba,kaman kar nuka mtswww.... Sulaym taja tsaki hadi da kama hannu na muka fara dosan side din wanda naji an kira da Sir Khaleed. Xufah ce ta hau karyomun shikenan na shiga uku na. Ban san lokacin da nace mawa Oummu Sulaym Yanxu mune xamu ringa kula dashi har yakoma ko!?. waya fada maki xaya koma? ai yadawo kenan. tunda ya kammala digiri din shi na biyu ne,a fannin ingineering,sai kuma na farko yy a bangaren Architecture. shiyasa

ma aka fi sanin sa da Arch. Khaleed. mune da sauran Ma'aikatan sa na can companyn sa suke kirar shi da Sir Khaleed, amma da Architect Khaleed aka fi sanin shi. ai kawai gdyn da xamuyi ma Allah shine daya,da safe yake tafy Companyn sa baya dawo wa sai After 6pm. sannan kinga kafinnan tuni mun gudu gida masu yin night duty sun amshe mu.
A sanyaye nace kuma wai anan gidan yake shek'e ayan sa ko? wlh sai naji bana son ganin shi sam. na fadi ina mai bin Sulaym da kallo ina tabe dan mitsulun baki na.
Dariya Sulaym tayi sannan ta cigaba da cemun" tom bakiga tafiyan da muke xukawa bane,ae side din shi dana iyayen shi dan karan nisa ne dashi,ga shi har da gate din da xai fita tacan batare da wani ya sani ba,shiyasa tanan karuwan sa da yan matan sa ke shigowa har su gama Hajiya Zaituna batasan ma anyi ba. sai mu da mike hidimta masa.
Tun daga nan ban kuma cewa komai,gabana ban da fadi babu abun da yakeyi. Addu'a nake tayi har muka shiga side din nashi,da komai nashi yafi na sasan Hajiya Zaituna kaman sama da kasa,don da shigan mu duka muka rufe ido muna mai shakan wani irin daddadan kamshi,sunan Baya nan ne amma komai na side din tsaff da shi,abun gunun ban sha'awa sai dai kura da side din yy kadan,tun a yanayin tsarin wajen xaka fahimci lallae mazaunin Side din gogagge ne,kuma cikakken Bature ne,don sam bai xauna cikin su a banxa ba.
Daura kyallen da muke dorawa kan Uniform namu duka mukayi sannan muka fara aikin mu,sosao a lokaci kadan mukaci karfin aikin,Muryan Mhiss Caterine muka jiyo daga bayan mu tana fadin Suhaimart,Sulaym ku kara cleaning din can coridon okay?. tom muka ce mata muka juya xamu nufah coridon da tayi mana nuni. sai tsintayar muryan ta mukayi tana cewa" Suhaimart".Saurin juyowa nayi ina mai amsa kurar nata. Cike da daure fuska da nuna bacin rai tafara cemun sau nawa nake maki magana kan ki rage wannan xurmemen hijab din. ladern Hannun ta bude hadi da fiddo da hijab Half sunnah arsh,tana miko mun da cewa" kar nakara ganin ki da wannan,idan ba haka ba kuma xan sallameki a bakin aikin ki. barina har rawa yake haka jikina nayi saurin saka Hannu na amsa ina cure na jikina na saka wannan, hadi da mata godiya,duk da bana son hijab dun sam... Juyawa tayi hadi da barin side din.yyn da Sulaym taso yin mun wata maganar shirmenta kawai sai na kauda mata da kai don idan ta itane xamu kai dare a haka.
Haka muka cigaba da aikin mu wanda kan lokaci kadan muka kammala sannan muka bar sauran ma'aikatan don su cigaba da nasu aikin... A wannan rana a kakkauce na kammala nawa aikin yayin da wuraren magrib muka baro gidan Hajiya Zaituna. Sam oummu Sulaym bata barni naje gida ba sai da muka wuce karamar kasuwar cikin garin Zaria, ba wani nisa ne da gidan Hajiya Zaituna ba. itah Hajiya Zaituna a GRA Zaria take,yyn da Daga nan ne muka wuce kasuwar monday. Sai da muka isa ne na kwasa takaici don ashe gaba da kudin Oummu Sulaym Naira 150 ne. kallon ta nayi gami da ce mata" wai Sulaym mai xamu siya a kasuwar nan ne. ko so kike amana wulakanci abimu da kallon banza. Murmushi Oummu Sulaym tayi kana tace" waya fada maki aiko da dari biyu da Hamsin din nan sai kinga kayan da xamu siyo. kedai muje daga ciki kiga irin kasuwannan,ae komai nasu arhana ne dashi,nidai ban kuma ce mata komai ba,na cigaba da bin bayan ta kaman yanda tace. a wani wuri naganmu cikin irin maguxawan nan wato katafawa. tsumma naga sun xuba a gaban su suna 20 ². ko yar shugaban kasa albarka. bin mutumin da yake wannan maganan nayi da kallo,nan naga wata irin mutsitstsikakken riga wanda shida tsumma babu maraba,amma ya daga yana Ko yar shugaban k'asa albarka har da karin yanxun akayi odan su daga London. dariya lamarin ya bani,wanda

sai nayi murmushi hadi da cigaba da bin Bayan Oummu Sulaym.
Dai² masu sai da safuna muka tsaya, daga kai tayi tana kallona sai tace inyamuran ta bata safa fari mai kyau. Bayan ta bata ne tafada mana kudin nan ta mika mata 50 sannan muka kamo hanyan dawo wa gida. A napep ne  Oummu Sulaym tamiko mun Safan tana furta Besty naki ne fah,naga na kafan ki talalace ne,kuma ba'akusa bamu albashi ba,kar Hajiya Zaituna ta gani yaxa ma mana na sababi. Bude baki nayi ina fadin besty na bakya gajiya tom ngd. Haba meye na gdy Suhaimart aikin fi karfin safan naira 50. Nan kuma ta kauda maganan ta hanyar firar mhiss caterine tana kwaikwayon muryan ta wanda ta sani dariyan dole.
A dai² yan dusa zaria muka sauka yyn da Nan Oummu Sulaym ta dauko Naira 50 ta baima me napep,aiko da ganin Hamsin Me Napep ya kashe hadi da cewa shi sam kudin ba Hamsin bane. Hakuri na soma bashi,amma sai kara butsarewa yake shi sam bai san wannan ba. Hmmm Kaman mutuniyar Arxiki Oummu Sulaym ta kalleshi hadi da cewa' tom bawan Allah nawa ne kudin naka tunda ba 50 bane.
Nan kanshi tsaye yace 100 ne kudin sa. Wani wawan Dariya Oummu Sulaym tayi cike da rainin Hankali tace " Allah ko yaya na,tom gashi kuma bama da naira 1 yanxu,sai dai kayi Hakuri. Ganin Rainin hankalin da Sulaym tayi masa yasa me Napep kara tutsewa yana bala'i har mutane masu wuce mu a bakin Hanya sun fara saka mana ido. Wurgo ma Sulaym kudin yayi yana cewa wlh baxan amsa ba,sai dai ku rike duka. kai Hannu Sulaym tayi tana mai daukan kudin da ce A'a duk haka bai taso ba,kaje mayi ma sadaka. tana fadin haka taja Hannu na muka tsallaka titi hadi da barin me Napep da sakakkiyan baki.
A hanya kuwa sai da nanu mawa Sulaym rashin kyautuwar Abun da tayi,amma sai tace ai Besty haka shine dai² gobe baxai karayi ma wata ba. kinga ko ruwa da sabulu ai masiya. nidai shiru nayi mata ina mmkin Tsiwa irin na Sulaym. wanda da muka iso gidan su A unguwan Alkali tayi mun sallama,yyn da ni kuma sai da na dan kara tfy kadan sannan na isa gida...
A bakin soron mu na tadda Abokan Zaid da shi kansa zaune suna sana'ar ta su. yyn da kaina a kasa na wuce, muryan wani Abokin Zaid da ake ce mawa Aminu naji yana cewa" Babah wannan kanwan taka fa tayi,iya wuya zan fara tara kayan Aure naxo nayi ciki da itah. Banji mai Zaid yace da suba,abu daya ne najiyo tsakanin su shine zagin da zaid ke Auna masa. don fada har cikin gida ina jiyowa,arxiki na daya oummah Rabi bata nan,niko zama nayi nai shiru ina tunanin inda ta tafi da wannan yammancin.Mikewa nayi hadi da nufan rijiyar dake ysakar gidan namu na cika bokiti da ruwa sannan na nufi bandaki....
Niko Mmn teddy nan bayan shigewa n ta ban daki ne,na samu damar kare mawa Suhaimart kallo.
A takaice dai Suhaimart Yarinya ce budurwa da baxata wuce  shekaru 17/18 a duniya ba. Fara ce mai kyau,wanda wuya ya disassar da hasken takoma choculate din karfi da yaji. wanda duk da haka bashi xai hana ka fahimci cewa ita din fara ce karrr ba..... Doguwa ce bacan ba,wato matsakaiciya. tana da diri mai kyau ga shape gashi kuwa har gadon baya kaman Bafillatana,amma su cikakkun Hausa Fulani ne. tana da Ball Eyes basu girma kuma farare tasss sai tsakiya baki kirin. idan tayi murmushi ko dariya dimple din ta bayyana yake sosai ga kuma hushirya kaiiii...
komai na Suhaimart na daban ce, irin sune ake cema cikin dubu da wiya a samu daya. bin gidan nayi da kallo tabbas ko makaho ya laluba yasan suna cikin Rayuwar Wahala. Bayan Minti 15 ne na fito hadi da nufan dakina,nan na dauko wasu ko daddaun atamfa mao launin kore da

fari, shafa basilin nayi don ko arxikin powder bana dashi bare na saka.
Fitowa nayi hadi da nufan madafin mu don na girka abun da ya sauwaka mana. Anan na ga ma Oummah har ta kammala tuwo miyar yauki,nan na maida miyar wuta don takara xafi.... Komawa nayi na zauna ina tunanin Rayuwa ta. Lallae a Rayuwa na na baya maiye na dandana, Hmm Zuma ne ko mad'aci. hawaye ne yafara bin kuncina a sarari nace zuma,a yanxu ne nasoma dandanan mad'aci.
A haka ina a zaune har aka fara kirar sallahn magrib sannan na tashi nayo Alwala hadi da nufan daki na don na gayar da mai sama'u....

************************

Mom"mom..." iftihal ce mai kwala kirar sunan Hajiya Huwaila dake kishijgide ta dora kan D'an nata saman cin yanta tana mai shafa sumar gashin sa wanda da'alama tana rarrashin sa ne kan abun da ta saba yi kullum. Turus taja ta tsaya tana mai aikin turo Baki da kunkuni,gami da magana cikin ranta,wai shi kullum Ya Huday baya girma ne. kullum Mom ta dinga sangar ta shi,tana Rarrashin sa kan abun da ya wuce fiye da shekaru 10 da dori, Haba wannan naci dame yy kama. Muryan Mom ne taji tana ce wa oyoyo Ifteey na,wlcm back... Daurewa tayi hadi da fad'awa jikin Mom tana rungume ta. Huday ne ya tashi daga kwancen da yake fuska tamau a daure,daka ganshi xaka fahimci miskili ne na karshe gashi koba a fada maka ba,xaka fahimci sam baya son Raini.
Hajiya Huwaila ne tace"  Huday yanxu yaushe ne xaka tafi Nigeria?. Mom a satin nan inshaallh. Kan ya rufe Baki Ifteehal ta amshe da cewa" What??? Nijeria?. Mom me xamuyi a wannan k'asar da mazaunan ta ma so suke su barta. Gsky ni baxan koma can ba nafi jin dadin xaman london. zan cigaba da xama da Daddy na anan. Ta fadi tana shiru sakamakon hararan da Huday ke watso mata. Murmushi Mom tayi Hadi da shafa fuskan ifteey tana cewa" No My Daughter bamu ne xa muje ba,Huday ne keson tafiya can. Saboda kula da Companyn shi. ki kwantar da Hankalin ki,Mom ta karke maganar tana mai rungumo Ifteey Jikin ta.
Shikuwa Huday mikewa yayi ya nufi side din shi hadi da kirar Mhiss Umiey wanda take Scatery din shi ce na companyn shi a Zaria, yana mai sanar mata da isowan shi.

Wannan kenan...

*GIDA NAGERIA*
Suhaimart'...Suhaimart... Oummu Rabi ke kwala kirana,wanda cikin sauri na fito daga daki na,wanda sanye nake cikin shigar uniform dina na Aiki.
Kaman daga sama naji anshekomun Ruwan xafi a jikina. saurin jah baya nayi ina ganin Abun da Oummah Rabi ta watsomun a jiki tana mai Aunah mun uban zagi kaman yar tasha....

LABARIN ZUMA DA MADACI TA KUDI CE, XAKI TURO KATIN MTN,VIP 200 VTU,#200 SPC #300  NORMAL GRP #100 DUKA TA WANNAN NUMBER 08081202932.

*Mu tare a next episode*

*Mmn teddy🧸*
*🎋✨ZUMA DA MAD'ACI🎋✨*

Na
*Mmn teddy🧸*

*ALHERI WRITERS ASSO.*

*A.W.A*

https://www.facebook.com/100186388252056/posts/100188104918551/

```Kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai dan Alheri```

---

*Episode 3\4*

*ABIN ALFAHARI NA*
Gare ku iyaye na,Abin Alfahari na,ina matuk'ar godiya abisa tarbiyan da ku ka bani,Allah yak'ara nisan kwana Ameeen ya Rabil Alameen.

Wannan littafin sadaukar wane ga duk wani mai kaunar labrn Mmn teddy🧸, wannan yar k'aramar kuma Babban su,wanda ta saba nishad'antar daku da dadad'an littafan ta,mai sanya ku nishad'i da faranta ranku don nasan tabbas baxaku manta da littafin ta mai suna. *YAR AIKI,BAFULLATANAN RUGA* ba, Ga kuma uwa uba *DIJAMA Y'AR FULANI* Hmmm ummmm ga kuma *BINTOTO* Hmm wannan shiru xanyi don nasan bakwa buk'atar sharhi dan gane ga wannan book d'in... To a yau ita ta taho maku da sabuwa mai dauke hankali da kuma sanyaya xukatan ku, wato *ZUMA DA MAD'ACI* Dajin sunan kunsan da badak'ala, labrn da ya xo maku da sabon salon,don Alkalamin ba irin tasu bace, ku dai keep folowing💃. Don tabbas xuma da Madaci shidin ko a littafan wannan marubuciya na daban ne📘❤️.

wannan book kaman yanda kuka sani ta kudi ce labarin,Zaki turo katin MTN #200 VIP, #300 SPC,#100 NORMAL. Duk ta k'ark'ashin wannan number 08081202932/ 09137392680.
```

*______________________________*

*بسم الله الر حمن الر خنم*

Ganin yanda Oum na keyin Huci tana shirin cafkoni,yasa ni saurin xubewa kasa jiki na na kyarma haka baki na,Hawaye kuwa tuni yaga ma wankemun fuska. oumma na don Allah kiyi Hakuri. Na fadi ina mai bin Oumma Rabi da kallo. Yyn da itakuma cike da masifa dama kowa yasan Halin Oumma na da iya masifa sam bata da ragayya. bata bar yaranta mu ba,balle kuma makota,amma Ita oumma na irin matannan ne masu kwad'ayi da son abun duniya,bata ki taje duk inda xa'aci mata zarafi ba,indai xa'a dauko kud'i a bata.Shi kuma yaya na Wato Zaid irin yaran nan yan Allah ka shirya duk da a baiyin shaye$^2$ sai shan giya da kuma caca,don duk anan kudin shi yake karewa,amma fah shi a kwai shi da girman kai,ji da kai da isaah. Don sam har gowan shi ni yake mawa,a waje ka dauka dan wani attajiri ne,mussaman yanda inna Amsa dan kudin aikatau dina. ya kwacemun yaje ya siya ma kansa sitiru sauran kuma yayi sha'anin gaban shi da su. Itako Oumma na sam hakan da yake mun Bai da mun ta,ita dai kawai na nemo na bata,Ranan ko da ban samo masu kudi ba,a wannan rana na shiga uku na nagama,don A Ranan Zaid sai yayi mun dukan tsiya. Haka Oumma Rabi... Shiru nakeyi so dayawa ina tunanin Mahaifina da yarasu, a zuciya na nace inda ya nana nan duk ta laucin mu abun baxaiyi xafin Haka ba. Haka xan zauna nayi ta zubar da hawayen da ya xaman mun jiki don bb ranan da baxanyi kukan Maraicin Uba ba. Don na tabbata da Baba na yana nan koshi Zaid din ba zai lalace haka ba.
Muryan Oumma na ya dawo dani daga duniyan tunanin da na lula na yan seconni. don Uban ki wannan tsinkakken abun ne xaki yi ma eye".
Hawaye ne xubo mun a sanyaye kunsan ni haka dabi'a ta take,sam bana da zafin nama komai nawa salala nakeyin shi. wanda a hakan a wurin aikatau din mu wasu ke kirana da Princess Suhaimart acewan su a kwaini da kasaita. niko iya sanina haka Allah ya halicceni don tun da yarinta na ake fadamun hakan.
Oumma kiyi Hakuri bari na kunna icen na dora a wuta tayi kauri.
Bata bani amsa ba,sai dai jan dogon tsaki da Tayi ta wuce cikin soron ta. Niko tuno da masifan Hajiya Zaituna yasani saurin nufan madafi na kunna icen hadi da maida ruwan kunun a kan wuta,kafin minti 10 tuni yy nan na juya hadi da nufan soron Oumma na na ajiye mata kwanan shan dana zuba kunun. ina fadin Oumma na sai na dawo. a ciki ta amsa mun da adawo lfy. Haka na amsa ta na nufi Zsuren gidan namu ina mai Addu'an

*بسم الله توالكر ة الله ول حول ول قوات الل  بالله.*

Nan na fita ina mai kuma bin ko ina na jikina da du'ai. kunsan Addu'a makarin bawa ne, da yardan Rabbi na isa gidan Hajiya Zaituna. Nufan barayin Mu nayi wanda nan na saje da ma'aikatan gidan muka cigaba da aikin mu ni da Oum Sulaym. Bamu lafa da aikin ba sai wuraren 2pm. nan muka koma side din mu don muyi Sallah sannan muci abinci sai mukoma bakin aikin mu. Na riga Sulaym sallamewa don haka sai na mike ina mai nufan Barayin Mhiss Caterine don na gaidata. A tsaye na tadda ta kowa na tajan$^2$ wanda da'alama da wani abune dasuke riyawa suna kuma kwancewa. A sanyaye cike da zakin murya ta na gaida ta. sannan na juya zan bar wurin. cikin dan Sauri Mhiss Caterine ta dakatar dani ta hanyar cewa" Immm

Suhaimart Maxa ki nufi Side din Sir Khaleed ankai masa lunching kije ki gyara masa side din nasa wato bedroom sannan kiyi serving nasa. Gabana ne ya yanke ya fadi,jin kawai sunan Sir Khaleed da Shugan namu tayi, cikin sauri na daga mata kai alamar tom,sannan na juya hadi da nufan Barayin data Umarce ni. a zuciyata ko ina Mamakin Dama ya dawo kasanne?.
A haka na kutsa kai ixuwa side din danaga an kuma kara tsara shi, kyaun ko da yy baxai fadu ba. Nufan dirning din dake can daga bayan cushines wanda akayi shi daga sama nayi. nan naga babu masaka tsinke don shake yake da abuncucuwa kala². komawa nayi na Zauna ina mai zaman jiran fitowan shi. Amma fiye da Rabin Awa babu labarin sa. Tuno da yanda muke mawa Hajiya Zaituna mu muke tasota yasa ni Saurin mikewa gudun kar nayi wani laifi yasa na nufan wani falon sa,amma nan Ma baya nan, cike da addu'a na murda kofan bedroom din nasa,ina mai kutsa kaina ciki. Ban ga mutum ba,duk zare idon dana keyi,sai da dadad'an kamshi masu saka mutum jin kasala da shakan su. Ganin yanda Komai yake a tarwatse filoli duk a kasa,ga Shi kanshi gadon duk an birkita Shi yasa ni nufan Kan bed din don na gyara duk da nasan yin hakan is part of my duty... cire bedsheet din nayi ina mai sauke sauran fillows din kan wani madaidaicin Cushine. Kaman daga sama naji karar feshe turare,wanda yasa naji kirjina ya amsa gammmm.... Saurin Dagowa nayi ina mai bin idona da kallon inda kunnuwana sukaji mun kamshin turaren. Dressing mirrow ne nagani yana passing dina,yyn da shi kuma ya juya mun Baya,sai dai ina kallon shi ta jikin Madubin. Addu'a na hauyi baki na na karkarwa don a tunanina Sir Khaleed anjani ne,yanayin yanda yasaki sajen sa yakewaye fuska. gashi fuskan sa ta mau. kuma abun da ban taba gani ba,wai ace namiji daure da towel a kugun shi. Kirjin shi kuwa wasu irin kwantattun gashi laufffff² kwance a saman kirjin shi. Yanda naga fuskan shi tamau yasa Ni kwala ihu ina fadin wa'innahu Sulaimanu,wa'innahu bismillahir rahmanur Rahim,Allahu la'ilah haillahul wayyuuuu.... ai ganin bai motsa ba yasani fara takawa sadaf² wuff na fice daga bedroom din da gudu ina Haki wanda ko gabana bana gani. shikuwa Sir Khaleed dariya ne ya kubce masa,wanda rabon da yayi kaman sa har ya manta. Sai da yy mai isar sa,sannan yacigaba da kintsa kansa,yana furta wa a ransa yaushe Mom ta fara kawo kalon type din matan da yakeso aiki gidan nan?. A sarari ya furta gata miskila amma da akwai raki ga tsoro mtssswwww....yaja wani dogon tsaki yana cigaba da kimtsa kansa.

Niko da fitana daga bedroom din bana iya kallon abun dake gabana,burina shine kawai naga na bar Side din sir Khalid. Karar Glass cup din danayi ball dashi ne yasa nayi saurin waiwayo yyn da kaman daga sama naji muryan Hajiya Zaituna da shigowan ta kenan falon tana furta mun ki gyarashi da kyau. Okay Hajiya". Amsan dana bata kenan, itako shigewan ta bedroom din Sir Khaleed tayi ta barni da tattara glass cup din. don jikina babu inda baya kaekarwa.
Suhaimart badai har kin gama ba, ya akayi kk fashe wa'annan glass din?. Oum Sulym ce mai maganan tana sunkuyowa gareni da kokarin taya ni kwashewa. Murya na har Rawa yake cike da miskilanci na,nace mata" wlh Oum bada gangar nayi ba nima ban sani ba. Ayyyah Allah ya kyauta muje mu xuba a dustbeen ko?. Daga mata kai nayi hadi da barin side din.Sai da mukayi tafiya mai dan nisa don can backyarda din gidan mukaje sannan muka zubar da kwalaben.
A hanyan mu ta dawowa ce muka ci karo da mhiss caterine cike da mmki ta kallani tana furta,Suhaimart i deducted 500  naira from ur Salary. wannan ae iskanci ne. da kijamun bala'i gomma na 6ata maki. mtssswwww shashasha kawai. nan mhiss Caterine ta fadi tana mai rabani ta wuce ta gyefena. nikuma ganin haka sam bana son wasa da aiki na yasa nayi saurin

nufan Side din nashi. Yyn da Nan Oummu Sulaym ta hau bina da kallon tausayi.
Da shiga na falon dai² suna fitowa daga bedroom din. Cike da rawar murya don jiki na har d'an rawa yake,a cewana na cire rai da cigaba da aiki a gidannnan. Saboda Abun da nayi ma Sir Khaleed,tabbas yanda ake fad'an rashin Mutuncin sa da tijara to nasan baxai Barni ba. K'wallah ne ya kwanta mun a ido,ni har ga Allah ban san Sir Khaleed mutum ne ba,aiyah sanina gamo nayi da aljani😢. Ace mutum ya fito yana wani digar ruwa kaman mala'ikan zare rai. Ga kyau kaman Aljani wlh na tabbatar duk wanda yaga Sir Khaleed sai ya firgita don kyaun shi da kwarjini. Duk kyaun da ake yara mun,yau naga Wanda ya nikkani 100%.
Ganin suna karaso gareni yasani saurin sidda kai ina mai Furta Sannu da fitowa Ranka yadade. Hajiya Barka da wannan lokaci".
Kallon Izzah ta watsomun kan ta ya tsina bakin ta da yasha pink jan baki,kace ba ita ce ta Haifi Sir Khaleed ba. Take care of my son ok. Ta kalleni tana cewa". A sanyaye cike da Gamsuwa nace Angama Hajiya,inshaalllh". Bata kuma tanka ni ba,haka shima Sir Khaleed da sam Hankalin sa baya kanmu,ya tatttara ma wulakanci,don latsa wayar hannun sa ma yakeyi,ni ya barni da 6arin jiki.
Tare suka isah dirning area da Hajiya Zaituna kan daga bisani nayi saurin bin bayan su kaman munafuka inah mai jah masu kujera don su Zauna kan na fara serving nasu.
Sir Khaleed ne ya Zauna ammma Hajiya Zaituna tsayawa tayi har ya zauna,sannan ta Rungume shi banji mai tace masa ba,illah Murmushi dana ga tayi tana manna masa Kiss a saman Goshin sa. nan shima ya yy mata murmushi sannnan ta fice,nikuwa da nayi nisa inah tunanin wannan soyyaya da suke ma junan su,don ko ba'afa da maka ba zah ka fahimci hakan.nan na lula duniyar Tunanin tawa Rayuwar,wanda sam banji Tafiyar ta ba sai dana kwarari kusan 10mins. Shikuwa Sir Khaleed, bai bi ta kaina ba,don latsa wayan nasa still naga yanayi. Ganin haka yasani gigif na dago ina Furta,amin Afuwa Ranka yadade... Bai kalleni ba har nayi 6a6atu na na gama,wanda ganin haka yasani saurin fara serving nashi ina mai Du'a'i. Don sai yau na tabbatar komai nawa yin shi nake too lazy.... Shikuwa sai a sannan ya dago kai hadi da daga mun,wai a dole sai a yanxu ya bani amsa ta hanyar wannan guntuwar Alaman tasa. da ina can ma ban lura ba. Sai da naga ma yi masa komai ne,naja na tsaya ina mai kwantar da murya ta da cewa" Bismillah Yalla6ai". na fadi ina mai Kallon fuskar sa,da har ilah yau baya ta kaina. Cikin wani irin tattausan murya mai cike da Gent voice din sa na tsinkayi yana cewa " Madam" Stop calling me yalla6ai,and.....mtswww yajah tsaki wanda da'alama xaka fahimci baya son mgn ya hada dogon sentence..nan ya cigaba da And whatt??. sai kuma yace that stupid name that u are saying just now. ya fadi ya sauke mun Manyan idon shi a kaina. Jiki na ne ya fara rawa labbana ko har haduwa suke da juna,cikin sauri nace masa Ranka yadade. Exactly of couse that name. kar na sakeji okay. niba daya daga cikin su bane. Kun sanni da Saurin xubar da Kwallah don tuni Fuska ta ta jike da Hawaye,na oumma na tana cewa akwai ni da kukan muna funci,wanda ni kaina bansan lokacin da yake xuwa mun ba. Cike da rawar Murya ta masu kuka nace" okay Sir". don Allah kayi Hakuri baxan sake ba. Shikuwa Sir Khaleed da baiga abun kuka ba,sai ya dago hadi da kasheni da ido,sai kuma ya saki wani murmushi da bansan Manufar sa ba,nan ya cigaba da cin Abincin shi. Niko ganin Haka yasani Kara rudewa a tunani na shikenan Sir Khaleed sawa zaiyi a koreni. Shikuwa cin Abincin shi yake yana mai Lumshe ido,a zuciyan shi yana furta duk wacce tayi wannnan girkin Lallai she is expact. Murmushi yayi dago idon dayi yaganni tsaye ina xubar da hawaye. gashi ba kuka nakeyi ba,a'a

Hawaye ne kawai ke sintiri akan fuska na. shiru yy ya tsaya yana kallona. wanda hakan yasani Saurin sunkuyar da kai. Bai san Lokacin da shi kan shi yace mata" Heey nayi maki wani abu ne? ya tambayeni yana Kafeni da Manyan idon shi daya kara firgita ni. Saurin girgixa masa kai nayi alamar a'a. Murmushi yy mun hadi da cewa" Okay kice kukan ne kawai kk son yi. Nan cikin Sauri na kuma girgixa kai. Shiru yy hadi da kama kanshi don shi sam baison hayaniya, shiru yy yana mai mmkin Miskilanci irin na wannan yarinya... Don sarai ya fahimta dalililn kukan ta. Dago idon shi yy wanda har ya soma chanja Kala,yace mun Uhmmm jeki bedroom dina ki gyara mun. Da sauri na nufi Bedroom din ina Mai dan jin sanyi a Zuciya ta. Tunda yanxu gashi yasani aiki.

Haka na nufi Bedroom don nayi aiki na. Shikuwa da ido ya bini yana jin wani yanayi a tare da shi. Saka Hannun sa yy yana shafa sumar Kanshi, Baiji shigowar mhiss caterine ba sai Muryan ta yaji tana cewa" good day Sir". bai bata amsa ba sai da ya kwarari minti kusan 5. sannnan ya daga mata kai".

Cike da girmamawa ta nufi kitchen don tayi ma Suhaimart mgn. Bai bi ta kanta ba,har sai da ta fito ta kuma nufo shi tana furta Sir Khaleed don Allah Suhaimart nake son mgn da itah.

Dago kai yy a sannan ya kallata yana furta Sunan Suhaimart. Nan ya fahimci wance take nufi. A ciki ya bata amsa da Tana mun Aiki...

Ohhk Sir". tana furta haka ta fice daga Faloun tana nufan Side din Hajiya Zaituna.

Shikuwa mikewa yy yana mai goge Bakin shi da tissue. Sannnan ya nufi Resting Room din shi don ya samu hutu....

**************

Zaune yake yana Aikin zanen da yasaba nata".

Wannan wacce yarinya ce kake drawing nata haka Huday".

Murmushi yy sannan ya kalli Maryam yana furta wait dear,bari na gama,inason tambayan ki wani abu ne. Shiru tayi don dama ita a kallum tana son taji labari game da wannan yarinya da Huday ke yawan zana ta. don tun yana Student a harkan shi ta Architecture bai da wani abunyi sai Zanen wannan kyakykyawan Fuska.

Suna a zaune tana kallon shi hadi da jin tsatsan kishin wannnan yarinya da haushin ta. sai ga Sectary nashi na Companyn nashi ta shigo. Good day Sir". Mhiss Godness ce mai gayyar dashi tana dan risinawa alaman girmamawa. Sai da yasa colouring a gyefen Fuskan ta sannnan ya juya yana mai juya drawing bord din nashi yana ce mata"  Mai yafaru ne Godness? any problem. ya tambaya yana daga mata gira. cikin Sauri tace" We have Visitors in Our Company,so  i just take them to Mitting Room. Ohk Alright I'm on my way". ya fadi yana mai rufe Bord din dake xane da itah da wani kyalle... fitan Mhiss Godness yy dai² da mikewar shi da niyan xai fice daga wurin. Cike da takaici kaman wata matan shi Maryam tasha gaban shi tana furta Haba Dearie". Wannan abun da kk mun is too much for me. na gaji,kana sane duk saboda dawowan ka Nigeria nima na baro iyaye na na dawo,ammma kuma sam baka da lokaci na,sai na wannan Yarinyan da ban san wacece ita ba. Gsky kafara saka mun tsanar wannnan Yarinyan,bana son ta wlh. ta fadi hadi da Gallah ma Bord din dake dauke da Hoton ta da Harara. Murmushi n takaici yy sannan ya kalleta yana cewa" Ohkk tom Wannan yarinyan da kk gani she is my Everything,my Happiness,indai kuma kina son ganin Farin ciki na,tom ki kaunaci Suhaimart ".

yana fadin mata haka ya ra6a yana wucewa ta gyefen ta. Ya bar Maryam da sakakkiyar baki.

Nan take ta fara Tunani wace Suhaimart yake nufi? Suhaimart din da ta mutu Tsawon shekaru goma sha... ko kuma wacece. gsky dole ne ta tuntubi Iftihal don tasan wacece wannan Suhaimart, bayan wancan an kuma Haifan wata ne....

*#SHERE TO ANOTHER GROUPS*

Maman teddy🧸
*🎋✨ZUMA DA MAD'ACI✨🎋*

Na
*Maman teddy🧸*

*ALHERI WRITERS ASSO.*

https://www.facebook.com/100186388252056/posts/100188104918551/

*A.W.A*

```Kungiya masu aiki da naxari dakuma ilimi,Alheri sai d'an Alheri👌🏻```

---

*Episode 5&6*

*ABIN ALFAHARI NA*
Gare ku iyaye na,Abin Alfahari na,ina matuk'ar godiya abisa tarbiyan da ku ka bani,Allah yak'ara nisan kwana Ameeen ya Rabil Alameen.

Wannan littafin sadaukar wane ga duk wani mai kaunar labrn Mmn teddy🧸, wannan yar k'aramar tasu kuma Babban su,wanda ta saba nishad'antar daku da dadad'an littafan ta,mai sanya ku nishad'i da faranta ranku don nasan tabbas baxaku manta da littafin ta mai suna. *YAR AIKI NA* ba, Ga kuma uwa uba *DIJAMA Y'AR FULANI,BAFULLATANAN RUGA* Hmmm ga kuma *BINTOTO* *'YAR WAYE???* Hmm wannan shiru xanyi don nasan bakwa buk'atar sharhi dan gane ga wannan book d'in... To a yau ita ta taho maku da sabuwa mai dauke hankali da kuma sanyaya xukatan ku, wato *ZUMA DA MAD'ACI* Dajin sunan kunsan da badak'ala, labrn da ya xo maku da sabon salon,don Alkalamin ba irin tasu bace, ku dai keep following💃.
```

Don tabbas xuma da Madaci shidin ko a littafan wannan marubuciya na daban ne📘❤️.

wannan book kaman yanda kuka sani ta kudi ce labarin,Zaki turo #200 VIP, #300 SPC,#100 NORMAL. Duk ta k'ark'ashin wannan number 08081202932/ 09137392680.

*______________________________________*

*بسم الله الر حمن الر خىم*

Idan ko an haifo wata ne tabbas da bala'i,shikenan ni na ringa shairing din soyayya ta da matacciya? inah sam Hakan baxai yiwu ba. dole in ni dince to nice a komai,ta fadi tana kai Hannun ta ta dauki yar ficiciyar jakarta tana mai mayar da katuwar tabarau din ta da ya mamaye rabin fuskan ta gabaki daya, sannan tafara takawa cike da tsatsan wayewa da gogewa don ta nufi parcking space na wannan Company.
Sai a sannan na samu damar kare mata kallo,don Maryam irin Matannan ne masu kwarjini irin yaran nan ne kuma da hutu da kudi ya gama ratsa su,yaxama jinin jikin su,sam basu san wani abu da ake kira wai Babu ba. kullum cikin Arziki suke damalmaya. Shiyasa komai nata take yin shi cike da Izzah da fadin rai,niko nace shiyasa kawancen yazo Daya da Iftihal,don Aminai ne na Rai da Rai. Dad'a bin bayan ta nayi don nakuma kwararo maku zance akan ta. A takaice Maryam irin Matan nan ne marasa mai dan jiki wato tana da kiba duk da basosai ba,kuma bata da tsayi gajeruwa ce. duk da batayi kasa ba sosai,amma gajera ce. tana da sanyayyar kyau. da dan ido manya,gakuma Dan Karamin Baki,amma sam bata da Hanci mai tsawo. sanye take cikin shigar ta ta English Wears wato Riga top mai launin jah iya kugu sai Dogon leg jeans baki,yyn da tayi Rolling da Jan mayafi iya kafada,ta saka wannan Black Space din da ya manaye rabin fuskan ta,bakin ta kuwa yasha Lining din Brown Eye pencil da Jan janbaki da tasaka shi dai². Hmm tabbas Ko ban fada maku ba,kun fahimci Maryam kalan yan matan nanne yan gayu masu aji na karshe,duk da dai Ashekaru baxata Haura 22 ba a duniya.

Nufan wata jibgegiyar moto naga tayi hadi da budewa ta shige tana rufowa. nan ta jah ta hadi figanta cikin mahaukacin gudu,wanda nan na bi bayan moton da kallo ganin sunan ta danaga kirar End of Discussion.
Da sauri Wani sojah wato gate man na wannan ma'aikata yayi saurin bude mata Tanfatsetsen Gate din Companyn yana furta a sauka lafy Hajiya Maryam. Bata ma san yana yi ba,illah hawa kan Kwalta da tayi babu ko waiwaye,don a yau ranta ya gama Baci da Lamarin Huday. Ace duk kissan da take masa ganin ya manta da labarin wannan yarinya Still tana ransa da Rayuwar sa,tabbas akan Huday Xata iya daukan kowani irin mata ki ne.
A haka a moton sam ranta yagaxa natsuwa ta matsu matuka dason jin wacece wannnan SUHAIMARHT. A natse ta kai Hannun ta tana Daukan Wayan ta dayake ringing,wanda dajin Ringin tone din ta Fahimci ta Best friend din nata ne Iftihal. Sai da ta dan yi parcking Gyefen Hanya sannan ta Daga Wayan tana Furta Hello best Friend".
Maryam ykk ya Nigeria,fatan komai Ify,kuma kina bai ma Flowern ki ruwa yanda yaka mata?.
Mtsswww Karamin tsaki Maryam tayi kan daga bisani tace" Ifty komai na shirin lalace mun,ya xanyi yanxu? ya zanyi Huday ya so ni? tana fadin haka sai maganar nata ya sarke sakamakon

wasu zafafan waye dake bin saman kuncin ta... Cikin Sauri don Muryan Iftihal har rawa ya soma, Maryam mai yake faruwa ne? mai ya hadaki da Ya Huday din??.
Jan ajiyar Zuciya Maryam tayi kan daga bisani tace abun da dai kk sani ne Ifty. Wannan yarinya na tsane ta,sam bana kaunar ta wlh. Ni ya zanyi Zuciyar Mijina ya rabu da na Matacciya ne???. ta fadi cike da gaxawa. Ni ko Mmn teddy da bana gani nayi shiru a raina nace,kiji mun y'ay'an Zamani wai tun kan ayi Aure Har saurayin ki ya zama miji,ohhhh God,Allah ka shirya ka kuma kare mana Zuria Ameen y Rabby.
Muryan Iftihal ce ta katse ta dacewa" comedown my choculaty, Wlh ni nan da kk ganni tsanar da nayi mawa Wannan yarinya tafi naki. Tunda frank xai ce ni ba kanwar sa bace,Suhamart itace Kanwar shi saboda dodewar Basira,soyayyar ta ya rufe masa ido. ke inda kinsan Ya Huday a baya,wlh yanxu sai kinyi Hamdallah,don yanxu ya cire mawa kansa Xai kara ganin Suhamart a rayuwar sa,sai dai ya Rungumi Kaddara. Don Haka Abun da nake so dake Maryam,sam karki kuskura ki nuna ma Ya Huday kina kishin wannan Mataccuyar,inba haka ba xai tsaneki,shi yasa bama shiri sam. nima ina nan Dawo wa a Satin nan,kinsan Hubby na ya dawo. kuma bana ta6a nisa da shi. Kyalkyalewa da Dariya Maryam tayi kan daga bisani tace hakan yayi kyau ae da gskyar ki Best friend. gashi sarai kinsan waye Kwarxon naki da son Mata. Hmm kedai bari,inshaallah inna dawo komai xaiyi setling. Aha dai Suka yi Sallama da Iftihal akan Sai ta taho Nigerian. Shiru Maryam tayi a moton tana mai fadawa duniyar Tunani,tabbas tayi kuskure da har ta nuna mawa Huday bata Kaunar Wannan Matacciyar yarinyan. Mtssww nan tajah tsaki hadi da juya kan sitiyari don tabbas tasan ita karya ce a son Huday,xata iyah jure komai Har Allah ya nuna masu lokacin dasu kayi Aure,sannan sai tafara shimfida nata tsarin Rayuwar. Hakq tajuya don ta nufi Companyn domun ta Lallaso Habbibyn nata.
**************************
Suhamart " Suhamart..." Oummu Sulaym ce me kwala kirar Suhamart, turus tajah ta tsaya sakamakon ganin Sir Khaleed A falourn. Tsayawa tayi tana mai dan risinawa tana gaisar dashi,wanda bata jira amsawan shi ba,ta koma simsim ta fice daga Faloun. Shikuwa Khaleed Ganin ana damun shi da shaga da fita,ya sa shi mikewa don ya gani inta gama aikin da ya bata ta fice masa da Side,wannan damu ya isheshi,kowa ya leko Suhamart "?. Dai dai ina Jera filows don na Kammala komai ya shigo,sai da na ajiye filon sannan na juyo ina furta Na kammala Sir Khaleed. Sai da ya Lumshe idon shi sannan ya ware su a kan fuska ta. ohkk Mhiss Caterine nason ganin ki just now. Da wata mai kama da Mahaukaciya². Zaro ido nayi cike da Mmki na Furta Oummu Sulaym?".
Zama yayi akan Kujeran dake gyefen bed din sannan ya kalkeni kan ya bani amsa ne nayi saurin cewa" Ohkk Sir". Don sai a lokacin na tuna haukan da nayi,wato shine nake tambaya?". Hmm ya nisa nan nikuma nayi waje hadi da nufan inda xanga Mhiss Caterine.
Shikuwa Sir Khaleed bin bayan Suhamart yy da kallo bayan fitan ta,tabbas yana jin wani yanayi dangane da wannan yarinya, tom Amma meye?? kasan ta ne???. tambayan da yy mawa kansa kenan. Daga kafadan sa yy alaman A'a. sannan ya jawo Laptop din sa yana operating don yaga Halin da Companyn shi yace ciki,kan nan da gobe yace xai fara Shiga masana'antan. Kirar Aminin nashi ne ya shigo wayar tasa,nan yy saurin Daukan wayan yana mai furta,Huday yau ina cikin Farin ciki". Cike da Muskilanci Huday yy murmushi kan yace da gske Khaleed, me ke faru ne,ko kayi sabuwar kamu ne?. Hmm Kai dai yi shuru da Bakin ka. Yaushe Zamu hadu. Ko

na taho gidan ka na G.R.A ne?. Kai Khaleed wannan zakuwa haka,kar ka damu yanxu ina Hanyan xuwa Ma gidan Mum. idan nazo sai mu wuce can G.R.A din okay. Ohkk sai ka Karako bari na watsa ruwa kan iso. nan Huday ya katse wayan yana mai tubanin rabon da yaga Aminin nashi a irin wannan yanayin.
Horn Daya yy Wani kurtu wanda shi yake gadin gidan yy saurin wage masa gate din yana daga masa Hannu da Barkan ka da zuwa Alhaji. Sannan ya koma yana rufe Gate din. budo murfin moton nashi yy hadi da sako kafan sa yana futowa daga waje, wanda Kallo Daya zakayi ma Huday ka tabbatar da Namiji ne tsayayye,matashi maiji da aji da sanyayyar kyau,mai da manyan ido,amma kyakyawa ne fari tass yake,ya ajiye saje irin na Khaleed a kewayen Fuskan shi,wanda shi ya kuma kara masa Haiba da Cikar Kamala. Suit ne a jikin sa,don haka cike da takon Gent. man ya fara takowa hadi da nufan Side din Khaleed. don bai nufi na Haj. Zaituna ba,kasancewar yasan dr. basa da lokacin kansu,kullum suna on duty a asibiti sam basa da natsuwa. A gaban Mirrow yaga Aminin nashi yana gyara neck tight. wanda da Sallama ya shigowa tsakiyar Bedroom din nashi. Cikin Sauri Khaleed ya mika masa hannu,yayin da Huday yy saurin cewa" A'ahh Mutumin wannan kyau haka,kodai can Zaka nufah.
Ture shi Khaleed yy yana mai Zama kan Kujera yyn da shima Khaleed din ya Zauna. yana mai furta Stop Huday,ka sani yanxu Khaleed ya chanja,dabi'u halayya da koma meye da kasan yana yi mara kyau.
Cike da mmki da Rashin gamsuwa da mgnan nashi Huday yace kana nufin Har giya kadai na sha?". Kai Huday Ka fahimta wani irin Haske yaxo mun Rayuwa ta wanda baxan ta6a yarda ta kubce mun ba,irin hasken dana dade ina so da kauna,yau gashi Allah ya nuna mun,kawai kayimun Addu'a Allah ya Mallaka mun Y'ar Aiki na. Iittafin Mmn teddy kar ki sake a baki labrin wannan novel Hajiya ta.
Daure fuska Huday yy yana kallon Khaleed sannan ya furta haba Khaleed, plz har yanxu ka kasa chanjawa,yanxu iskan cin naka yakoma kan yan aikin ka kuma,plz kar ka lalata masu y'ar mutane... Cike da jin dacin maganan nashi Khaleed yace" Haba Huday in bakayi truesting dina ba,wa xaiyi,ban taba fada maka mgn akasin wannan ba, ina rantse maka baxan desieving nata ba,she is camp. taya ya zan cutar da ita. ni ko wata mace dakaga na lalata tom dama lalatacciya ce,but wannan ita ta dabam ce,ina son ta Huday, I Truely fall deeply in love with her. Ba wasa ba Huday". ya fadi yanayin shi sosai ya chanja. Shuru Huday yy yana mai Rasa Abunyi,tabbas ya dade da son ganin irin wannan rana a Rayuwar shi,Ranan da Khaleed zai daina duk wani dabi'un sa mara kyau. don haka ne ya rasa abunyi hamdallh ya dinga yi a Zuciyar shi,kan daga bisani ya daro hannun sa kan kafadan Khaleed yana furta Naji Dadi dajin wannan Magana taka Khaleed, kuma inshaallah Wannan yarinya zata zama mallakin ka,taxama ma mata Gareka uwar yay'an ka da yardan Allah. Murmushi Khaleed yy hadi da cema Huday tnc u Huday". nan ya mike yana furta lets go".
Murmushi Huday yy hadi da jerawa don su nufi Compound.
Na'am Mhiss Caterine gani". Murmushi Mhiss Caterine tayi hadi cewa" Yayan ki ne keson ganin ki yana compound. Ohkk tom  nace da itah,nan na nufi inda Ya Zaid ke tsaye yana aikin Huci kaman zaki. tunda ga nesa na hango hakan. A hankali da isana na furta Ya zaid Barka da Rana". batare da yabani amsa ba,ya fara Auna mun Zagi,kehhh dan ubanki Ina Kudin da nace ki nemomun ehhh. Jiki na ne ya hau rawa don nasan tabbas a yanxu Zaid har duka na zai iyah. Cikin Sauri na Hau cewa" Ya Zaid kayi hakuri xan samu inshaallh.

Ba wani inshaallh ne nake son ji ba,kar ki dawo gida sai kin tabbarmtar ma kin samo mun #3000 nan. yana fadin haka ya juya a fusace ya barni nan tsaye.........
Kwallah ne ya ciko mun ido,amma sai na maida su,jin an tabo baya na. Suhamart ". Oummu Sulaym ce mai wannan mgn. Waigowa nayi kaman ba komai na sakar mata murmushi. nan naga ta zaro ido waje tana Furta Suhamart jini a hancin ki,dukan ki ne Zaid yayi?. Cike da mmki Na girgixa mata kai alamar a'ah. nan tasa Hannun ta idon ta tuni ya fara fidda hawaye tana mai Goge Ha6on dake gangaromun. Saka hannun nayi ina goge mata Hawayen dacewa Oummu na ki kwantar da Hankalin ki Ha6o ne. Murmushi tayi mun kan tace tom Suhamart don Allah kudaina damun kanki kinji?. anjima muje asibiti adub...a'a Sulaym bafa ciwo bane,kawai habo ne. Na katse ta ta hanyar kwantar mata da Hankali. Itako sai ta mun Murmushi na ni yarinya ce,don sam ban fahimci mai take nufi ba. A shekaru Oummu Sulaym xata kai 20 a duniya,don haka taban kusan yakai shekara 3.
kama mani Hannu tayi sannan muka fara nufan Cikin gidan.
Sam bana kallon Gabana illah kici6us da naji nayi da mutum,saurin dago kaina nayi don ganin ko waye,amma nan naga kwarjinin da kamalan su duka ya rufeni,Huday ne na buge nan na sidda kaina kasa,wanda kaman wanda aka tsikareni nayi saurin kara dago kaina ina fito dasu waje akan fuskan sa. Shima kuma ni yake kallo...... Amma ban gane nufin hakan ba.

Hmmm muje zuwa masoyana,labarin har yanxu ba'a fara komai va,yanxu ne xa'afara chakwakiyar tsakanin ZUMA DA MAD'ACI.... Don tabbas nasan labarin nan zai taba zuxiya matuka ban dariya da Tausayawa,ban face ayi kuka ba aha...😭😅.
duk tausayin ki ga Suhamart ki daure bayan Wuya sai Dad'i😋.

Littafin Zuma da Mad'aci na kudi ne,Zaki turo #200 VIP, 300 SPC,100 NORMAL GRP. duka MTN ta wannan WHASTAAP Numbern👇🏻 08081202932./09137392680.

*Maman teddy🧸*
*🎋✨ZUMA DA MAD'ACI🎋✨*

Na
*Mmn teddy🧸*

*Page 7/8*

*ALHERI WRITERS ASSO.*

*A.W.A*

https://www.facebook.com/100186388252056/posts/100188104918551/

```Kungiya masu aiki da Nazari da kuma ilimi,Alheri sai d'an Alheri👊🏻.```

---

*Dedicated to my Sweatheart Layla🥰...*

_Wannnan labarin kirkirarrene,banyi shi don cin zarafin wani ko wata ba,illah don na fad'akar,wa'axantar nakuma ilimantar. Kuma banyar da Ajuya mun Labari ba tare da Sani na ba..._

*~DANGANE GA LABARIN...~*
Labari ne mai cike da tsatsan tausayi wanda nasan mutane da yawa xasu xubar da Hawaye ga Wannan labari,don nasan tabbas bakaramun ta6a zuciya labarin zaiyi ba. Labarin Zuma da Mad'aci labari ne da yakuma kunshi zallan Makirci kiyyayya dakuma wani irin Mahaukacin Soyayya da nasan Zaku jajan ta ma wannan irin Soyayyah ta wannan littafi. Hmm nikaina bana cewa komai,don Rubuta labarin nake amma komai ganin sa nake irin na halin da muke ciki ne ayau da kullum. Nace xan sanar daku komai da labrn ZUMA DA MAD'ACI ya kunsa to nasan xamu 6ata Awowiyi bai kare ba. Amma Hajiya ta daure kici gaba da bin Wannan littafi mai Dunbin Basirori da wayar da kan Yaya mata a wannan Zamani.💃.

Kar dai ku manta Maman teddyn ku ce🧸,wannan dinnan da kuka sani, da tasaba Zankado maku littafan ta mai sanya ku nishadi tare da fadakar daku kan Abubuwa da dama.A wannan Karan ita takuma zuwa maku da Sabo mai sabon Salo....Wato ZUMA DA MAD'ACI, Yar uwa kar ki sake a baki labari.

---

*بسم الله الر حمن الر خيم*

Cikin Sauri don Bakina banda karkarwa babu Abun da yakeyi da kyar nakuma iya furta masa yi Hakuri Ranka ya dade". Bai bani amsaba illah tsayawa da yayi ya mun kur da ido,wanda ni kaina ban fahimci Hakan ba saboda nima duniyan Tunanin da na Fad'a. Muryan Mumy Zaituna ne ya katse mu,wanda sam cikin mu babu wanda yaji shigowar moton ta bare kuma isowan ta. My Huday Saukan yaushe?. Wani faduwar gaba naji ya ruskeni,A take Kwakwalwa ta ta fara tuno mun da Abubuwa da yawa a baya. Jah da baya nayi saurin yi don Sam ban fahimtan Wani Abu,balle har naji Maganan da Wanda naji an kira da Huday ya bada Amsa. Abu daya kawai nakeji na mun Amo a kunnuwa na shine Muryan da Baxan ta6a mance shi a Rayuwa ta ba". Ki tafi mun da itah Nany,Karki Bari wani Abu ya sameta,na bai maki Amana kar ki Zalince ta,Marainiya ce a Yanxu,ki tarbiyar tarmun da ita ta farki mai kyau da zan Alfahari da ita a ranar gobe kiyama". A'a Ranki yadade Zan kula da ita tamkar Gudan jinin dana Haifah. Ki gudu kiyi nisa da Baby na Don Allah". Mum....." Mummm Baxan iya Rayuwa babu Suhaimart ba,mutuwa
```

zannnn......." Karar ne Napep da yake bina da Horn yasa nayi saurin ankarewa don sai a sannan na dawo daga duniyar Tunanin da na Afka.
Hajiya Tafiya ne?" Ina ne xan kai ki?. Sai da na shiga daga cikin Napep din sannan nace masa Cikin Zaria. Tom Angama" Ansan da ya bani kenan kan yaja Adaidaitan shi ya hau kan Kwalta.
Bangaren Mumy Zaituna kuwa Rungumo Huday tayi tana mai shaida masu da Anan zasu yi Lunching don Haka babu inda xasu tafi a yanxu, sai dai Su koma,Haka suka juya don nufan Side din mumy Zaituna,wanda Oummu Sulaym kam ta muzan ta,don babu irin gaisar da Hajiya Zaituna da bata yi ba,amma Ko Arzikin Kallon ta bata samu ba. Don Duk miskilancin Huday shine ya amsa mata. Shikuwa Khaleed ya dade da sanin Halin Mahaifiyan nashi,don Haka ne sam bai damu da ganin Abun da tayi ma Oummu Sulaym ba,tunda tasaba yin mafiyin wannan. Haka dai oummu Sulaym ta tafi sum² jiki bb kwari,don ita abun da yafi damun ta shine Yanayin da Suhamart ta shiga lokaci guda.
Bangaren ko Hajiya Zaituna a wannan Rana sam ta rasa ina zata saka kanta don farin cikin ganin yaran nata,sosai take farin ciki,don rabon da ta gansu sun zo nan gida Nigeria ita kanta ta manta. suna can kasar Waje. Rayuwar su Ya tattaru ya kare a Abroad. Shiyasa yau kan ta tsinci kanta cikin jin dadi matuka.
Haka nan suma Su Huday din,don a wannan karon da son Ransu suka dawo Kasan tasu.
*Wacece Hajiya Zaituna*
Hajiya Zaituna ta kasance mata A wajen Gen. Yakub d'an larabawa. Wanda ta kasance masa mata daya tilo a rayuwar sa,don ita ke dashi ita daya. Sai dan su Khaleed da shima ya kasance shikenan masu gaba da Baya a duniya. Shiyasa suke nuna masa so fiye da tunanin mai tunani,sosai suke kaunar Dan nasu. Shiyasa suka sangar tasa,tun da yaranta,sam bai taba niman abu yakasa samu ba. sai ya sameshi duk rintsi. Haka nan Sir Khaleed ya kasance Matashin Saurayi mai ji da isah Izzah ga kuma mahaukacin Arxiki da wasu ke masa kirari da yaro mai tashen kudi,Don a Yanxu ma so yake ya shafe iyayen nashi,duk kuma fadin Nageria babba da yaro babu wanda bai san Waye Arch. Khaleed d'an larabawa ba. Hajiya Zaituna ta kasance cikakkiyar likita ce,don Haka ne take Rayuwar ta a nan Zaria,don har aikin ta Asibitocin ta duk a Zaria Suke,yyn da Gen.Yakub yake Zaune a Abuja don can ne nadafan shi,wanda bai tahowa Zaria sai a ranan sati. Tunda shi ba irin mutanannan ne masu tsauri kan Ra'ayin su ba. Shi dai burun shi yaga ya Faranta ran iyalin shi,shiyasa duk abun da suke so sukeyin shi Openly. kuma Salin su duka Hajiya Zaituna da Gen. Yakub yan Adamawa ne....
Ba wata kuma Alaka ce tsakanin Khaleed Da Huday ba,illah Abota,tabbas Aminai ne na Rai² wanda sanadin Hakan har Abota ya hadu tsakanin Hajiya Zaituna da Arch.Huwaila,wato Mahaifiyar Huday. wannan kenan maji Sauran bayanan A gaba.
Niko Suhaimart tun da na isa gida naci sa'a Zaid baya nan,don sai asannan na tuno da sharadin da ya shimfida mun akan na nemo masa kudin. Nufan Daki na nayi na cire kayan jiki na,ina mai Daura wasu atampha sannan na fito na dauki buta don nayo alwala in yi sallah.Da kammala Alola na ne na nufi daki na don nayi sallah wanda bayan yan lokuta kalilan na Ida sannan na fito don nufan Dakin Oumma na". Da shiga na dan karamin dakin nata wanda yake dauke da ginin soro,nan na tadda ta Kwance kan wani yagalgallen tabarma wanda ya cinye ga tsufa da yayi. Kan ta ko ta tada shi da wani kullun kayan ta data daure da Dankwali.Baccin ta kawai takeyi don bama tasan da shigowa ta ba sam. Sai da na kare ma Dakin Kallo ina mai tausayama kan mu sannan na nufi inda take cike da tako a hankali gudun wai kar ta farka daga Baccin. Zama

nayi gyefen ta,ina mai daukan Kafan ta ina dora shi jikina,sannan na dauko dayan duka na dora jikina. A sanyaye na fara mata tausa,don nasan Oumma na bakaramun gajiya ne tayi ba. A haka nayi ta mata Wannan tausan ta yanda nasan zata kara jin dadin baccin ta,wanda ina a haka sam ban san sanda Bacci yy awon gaba dani ba.
****************************

*MASARAUTAR SARKI AHMADU MAI LAFIYA*
Cikin garin Gombe kenan,wani masarauta ne na gani da girma da tsarin sa gakuma Kwarjinin sa duk sai da suka dauke Hankali na wajen tsayawa ina bin wajen masarautar nan da Kallon Mmkin irin Gidan Sarautar. Tabbas ko ba'a fadamun ba wannnan masarauta Babban masarauta ce,wanda ta kwashe shekaru aru² Da kuma manyan ajiyoyi gare ta.
Kutsa kai na na hauyi batare da na bi takan Fadawan da suke ta zare mun ido ba. don gaba daya hankali na yayi gaba,burina daya in ganni cikin Wannan masarauta. Haka nayi ta kutsa kaina ina bin koina da Ido. Ina kuma mmkin Ganin yanda kowa bawa ka gani a cikin wannan Masarauta Yana rayuwa ne cike dajin dadi da kwanciyar Hankali. Wanda da'alama Wannan Sarki Ahmadu mai Lafiya sarki ne Adali,mai kyautata ma Talakawan sa,shiyasa tun daga wajen Masarautan nake jiyo kirarin mutane a gareshi,kowa da salon nasa gaisuwan karamci da girmamawan da yake bin Wannan Sarkin dashi... Ganin wata mata nayi sanye cikin wasu irin dakakkun yadi mai irin Karfin nan wanda yafi shige da saken fulani Baki,ta wani kinkima Dauri kaman Saraauniyan Dahhh.... tafiya take Zafff zaffff kaman zata tashi sama. Bin bayan ta nayi da kallo yyn da najah baya na tsaya don ban san inda zan saka kafafuna ba kuma. Muryan wasu Barori mata dake gyefe na ne naji suna cewa junan su cike da Rada,kai Jakadiyar Fulani ce,muje mu cigaba da Aikin mu. Ae da jin Furucun su nan nayi saurin bin bayan wanda aka kira da jakadiyan Fulani,don dama neman inda zan rakube na tattaro maku bayani akan wannnan Masarauta na keyi.
Wani sasa naga ta nufa,wanda tun da na kutsa kaina ido na ke Rawar kyerma dan gane ga Zinaran da akayi adon su tundaga wajen Sasan,bama akai ga shiga cikin wannnan Sasa ta Fulani ba. Yanda naga ana Barori na Zube mawa Jakadiyan Yasani sakiin Baki ina cewa a raina lallae duk inda wannan mata takaiga a gidannan tom da akwai bayani a tare da itah,wannan Zube mata kaman zasuyi Sujjada, ai ko Matan Sarkin Fulani sai Haka,Amma bari na kama baki na gudun kato6ara,don bansan ita kuma Sarauniyan Ya ake mata ba,kilah ita kwantawa kasa suke saboda Girmamawa.
Wani irin falo naga ta shiga da yagaji da kayan mulki dana Alatu da more Rayuwa. Yayin da na hango wasu mata Xube a kasa,wasu kuma suna Dauke da irin wani Mafirci mai bangaje,wanda daga kasan shi akayi masa a don zinarai,kai abun sai dai muce mashaallh. kutsa kaina nayi ixuwa inda wata mata ke a kishingide wa'annan Barori na mata firfita a hankali,yyn da ita kuma ke aikin baxa isar ta da Mulki. Zubewa Jakadiyya tayi a gaban Fulani tana aikin barbadancin gulman data saba. Na gaisheki Gimbiya matar Sarki mai Zamani mai karfin mulki,matan sarki ta gavban goshi kowa dole yy bayan ki kice a gaba,sarki mai Adalci mai Tausayin Talakawan sa. Hutawan ki lafiya uwar Daki na. Allah yakara nisan kwann..... Ya isah haka Jakadiyya". Fulani ce tace hadi da daga mawa jakadiyya Hannu,wanda inda Sabo ta saba da yarfin mulki na Uwar dakin nata Fulani. Risinawa ta kuma yi tana mai sidda kan ta kasa jikin ta har kyarma yakeyi irin na munafukan matannan, na ta furta Allah ya wuci Ranki yadade". Fulani ce ta rankafa kanta tana mai kara kishingida yyn da Barorin ke dada yo mata sijjada hadi da cigaba da aikin bautan

su babu kakkautawa. Hmmm nisawa Fulani tayi tana mai gyara alkyabban jikin ta dake wani irin Walwali da sheki, jikin ta ko inah walwalin Zinarai yakeyi. A cikin wata irin murya da tafi kama dana gadara ta furta Jakadiya ki maza ki sanar da kowa Na gidannan dawowan D'ana Yarima Abdul Manan". domun nan da yan awanni kadan zai sauka a gidan Nigeria. kai masha'allah,lale marhaban da dawowan yarima mai jiran gado". Allah dai ya sauko dashi lfy.
Kehhhh Jakadiyya mai nekejin Bakin ki na Furtawa ne? Waye yarima mai jiran Gadon,ae duk kan Masarautan nan babu wani mai jiran Gado da ta wuce ni,ni na cancanci na mulki Wannnan Garin ko bayan kaucewan  Mai martaba". Ko kin taba Ganin D'an Kwarkwara ya gaji Sarki???. jin yanda Fulani ke daga muryan da bata saba ba,yasa jikin Jakadiyya ya hau rawar kyarma cikin Sauri ta furta Allah ya wuci Zucuyar ki ranki ya dade. tuba nake". Tana fadin Haka ta juya sim² ta fice daga Sasan don ta isar da sakon Uwar Dakin nata". A ranta ko tana tunanin maganganun Fulani,wai itace kadai xata gaji masarautar Mai lafiya? tom ko ta yaya hakan xai faru ohoo!!! nan ta cigaba da sakawa tana warwarewa a zuciyan ta, don Sarki bai da d'a namiji ko guda daya sai Yarima Abdul Manan da ya fito ta bangaren Kwarkwara ae a tunani na Shima da ne". Tunda shikenan masa a Rayuwa namiji sai yaranki mata Uku. to yara mata ae baxasuyi mulki ba,kuma yanxu duka kowa tana dakin mijin ta. Uhmmm wannnan Masarauta da rikici gsky. Haka Jakadiyya tayi ta zancen zuci,kan ta nufi Sasan Barorin gidan don ta shaida masu dawowan Yarima Abdulll.... Fada ko tuni Aka nufi airport don taryan Prince Abdul Manan.
Bayan yan Awanni da Isan fadawa da securities don taryan shi jirgin Prince Abdul Manan ya sauka. ai nan na kara firfito da idanuwana waje don ganin Prince Abdul Manan. Wani kyakykyawan Matashi ne wanda a shekaru baxai Haura 35 ba ya fara sakkowa daga wannan jirgin,yyn da tuni fadawa da sauran masu tsaron lafiyan sa suka nufesa. Mtssww dan karamin tsaki yayi hadi da Gyara bakar glass din Fuskan sa da yy,a ranshi kam yana mai cewa shikenan yadawo gida xa'a fara damunshi da hayaniyan wannan abun. ya fadi yana bin Algaitan hannun wani ba fade da kallo. Niko kara kare masa kallo nayi,don sai da yake matsowa kusa damu na kara kallon sa da kyau. Fari ne wanda da ka ganshi kaga fulanin Gombe. shi kuma ba dogo ba can,sannan baxaka kira shi da mai jiki ba,kuma ba suriri ba. dai dai namijin da ake kira da ingarma. wasu fadawa ne sukayi saurin Rufa masa Alkyabba don sai a sannan naga ashe kananun kaya ne jikin shi. Daure fuska yy tamau kaman wanda bai taba dariya ba,ya na shigewa moton da aka bude masa. a ransa ko yana mai jin Haushin shikenan yanxu xai fara saka kayan nauyin nan da yafi komai tsanar su a duniya.
Zaune take tana aikin bin fuskan ta da Kwalliyan da ta saba,gyefe kuwa masu hidimta mata ne kowa tsaye cirko² don sunfi awa daya a haka. Itane goga wannan itace goga wancan. Muryan Ammie n ta taji daga bayan ta tana furta mata Nana Aysha wannan kwalliya haka sam bakya gajiya kaman kin san da dawowan Yarima Abdul Manan?. Saurin juyowa Nana Aysha tayi tana furta Ammie da gaske yau Hamma Abdul zai dawo?".  Murmushi Ammie tayi tana mai juya baya hadi da furta mata dayake nasaba fada maki karya? yanxu haka ma yana fadan Mai martaba. Wani ihu Aysha tasaka. wanda nan Ammie ta fita tana murmushi hadi da mmkin irin kaunar da Aysha ke mawa Dan yar uwan ta. Itako Aysha da fitan Ammie ta daga Wayan ta tana mai kirar Khaleed wanda kira daya biyu Khaleed dake Zaune kusa da Aminin nashi Huday ya daga Wayan yana furta Ahhh,wannan murna Haka ae ko baki fada ba nasan Abdul Manan ya sauka".
Dariya tayi cike da kuma jin kunya ta datse wayan tana furta masa Hmm bakomai shine babu sanarwa ko ?. Kan ya bata amsan ne ta datse wayan tana mai kara ca6a ma Fuskan ta

Ado,hadi da Addu'an Allah yasa Ammie ta bar ta a yau taje masarautar Sarki Mai lafiya don taga magamin Rayuwan nata ko tasamu yau tayi Baccin dadi.
*_______________________________*

Kaman daga sama naji muryan Oumma na tana furta kiran Sunana Suhaimart" tashi kije dakin ki ki kwanta kinji. ta fadi tana dan girgixa ni. a Hankali na bude darararan idanu na hadi da Sauke su akan nata. Cike da muryan mai Barci na furta Oumma Har kin tashi". Murmushi Oumma tayi sannnan taban Amsa da Ehhh Suhaimart na tashi, tashi kije ki kwanta Allah yayi maki Albarka kinji. Ameen na bata amsa sannnan nafara shurin mikewa daga Kwancen da nake. Cike da muryan Wanda sukayi shaye² sukayi tatul naji Muryan Zaid yana cemun Kehhh Suhaimart ina kudin dan Uban ki. Shiru nayi don bani da amsan bashi. aiko ganin Haka yasa shi nufo ni da niyan dukana. Oumma na ne tayi saurin tashi daga zaune ta dauko Mucciyan gyefen ta ta nufo shi dashi,ganin haka yasa shi fucewa daga dakin yyn da Oumma na ke bin shi da zagi dacewa ya kiyayeni. shiko Zaid duk Rashun jin shi baya son yaga bacin ran Oumma shiyasa ya fice daga gidan. Niko Zama nayi ina mai Rafka uban tagumi har Oumma na ta shigo dakin nata. Suhaimart maza ki kwanta ni yanxu xan je gidan Tani na ranto mana Bashin abun da xamu ci,kan karshen wata a buyaki Albashin Aikatau dinki sai mu biya". Tom" Oumma na ki dawo lafiya". Allah yasa sai na dawo. Ammie tace hadi da ficewa. Ina a zaune fitan Ammie ba wuya sai ga Ya Zaid ya shigo gidan. Keni ne xakisa Oumma tazaga aiko yau sai naci ubanki a gidannnan..... Wani wawan Mari ya kaimun,wanda sai da yasani na kifah sai jini da yafara xubomun ta hanci da baki. Duka na yake yana karawa,nan na hau ihu ina mai Rokon shi kan ya Hakuri nan da gobe xan samo masa,amma ko saurarona baya yi,sai uban duma na da yakeyi kaman sa'ar sa. A haka ya Haujah mun Hannu har wajen soron gidan mu.
*******************************
Yanxu Huday ya zanyi ni bansan ma ta yaya zan sanar mata da soyayya ta a gareta ba.Dariya Huday yy yana mai kallon yanda gabaki daya Khaleed soyayya ta gama sauya sa lokaci guda". Hmm tom yanxun bari mu gani? Huday ne yace yana mai tunano mawa aminin nashi mafuta. Year yanxun dai Ka kirawo Mhiss Caterine kace kana son bama wannan Maaikaciyar Aiki ne". Kallon Sa Khaleed yy kan daga bisani yace ohk. Wata ma'aikaciya ce taxo wucewa mai irin kayan Suhaimart, gaishe su tayi wanda nan Khaleed yace Tayo masa kirar Shugaban tasu. cike da girmamawa ta juya dai² Oummu Sulaym na shigo wa don ta karke aikin Suhaimart da ta tafi ta bari. Barka da Gida Yallabai". Kallon ta sukayi kawai sai suka kware da Dariya. wanda ya sanya ta tsayawa tayi shiru tana kallon sa dama suna dariya haka? tom meye Abun dariya a tare da itah. Huday ne cike da muskilanci yace mata Halan mu mata ne daxaki ce mana Barkan mu da gida"? Tom ai yanxu xamu fice Madam. Ita dai kasa basu amsa tayi sai tace masa toh kayi Hakuri kuskuren Harshe ne. Ohk Khaleed ne ya bata amsa a dakile. mai kikaxoyi nan?. Ehhh yallabai dama dama² uhmmm naxo na karke aikin Suhaimart ne". Kallon ta Huday yy sannan yace ita ina Take mai aikin? Umm bata jin dadi ne shine yasa ta koma gida". Ai dajin Suhaimart babu lafiya tuni Khaleed ya mike daga kwancen da yake,cikin Sauri ya furta mai yasame ta"? Ba wani ciwo ne ba sosai. uhmmm ina ne gidan su sai muje muga lafiyan ta,ko aikin da tayi mun ne yasa ta ciwon. Bude Baki Oummu Sulaym tayi sai kuma tace tom Ranka ya dade a cikin Zaria take". Mikewa Huday yy yana furta a gsky ya kamata mu duba ta Khaleed. yanxu je ki dakko komai naki muna jiran ki a Moto ki same mu,don ke Zaki kai mu". Tom

angama ranka yadade ta fadi tana Rawar jiki ta juya. Dariya Huday yy yana cema Khaleed see dis girl like a jorker. kara kwashewa da dariya sukayi suna mai kwasan keys din su don su nufi Parcking space............

Labarin ZUMA DA MAD'ACI ta kudi ce zaki turo #200 VIP, idan SPC #300,NORMAL #100 duka ta wannnan number 08081202932/09137392680.

*Maman teddy🧸*
https://www.facebook.com/100186388252056/posts/100188104918551/

*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Episode 9 - 10*

*___________________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*___________________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*
```

Haka suka tattara kayan su suna mai nufan Farfajiyan gidan suna mai jiran isowan Oummu Sulym. Itako Oummu Sulym tunda ta nufi Sasan su ta Ma'aikatan gidan sam ranta yaki natsuwa,tabbas tanaji a jikin ta kaman da wani dai abun ne kasa". Haka ta tattara kayan ta a jakanta sannan ta nufo filin Harabar gidan da ya kayatu da Abubuwan more Rayuwa komai na filin abun burgewa ne da ban sha'awa... Nufo su tayi a tafiyan ta na halin ko in kula,don baxaka ce Oumu sulaym wai budurwa ce ba. Ba Ruwan ta ita tafiyan ta kawai take babu Ruwan ta da komai. Binta da Kallo duka sukayi sannan da isowan ta Huday yy murmushi gami da fitowa yana kokarin bude mata Murfin moton. Murmushi tayi masa tana mai furta masa Ranka ya dade Ae na iya budewa,koba haka bane tafadi tana kokarin bude murfin moton wai ala dole xata nuna masa. Dariya yayi yajah ya tsaya yana kallon ta har ta bude sannan ta Waigo tana furta Ranka ya dade kagani?. Nan yayi mata tumb da babban yatsa alaman da kyau. sannan ta shige tana dariya. Yana mai Rufo mata murfin moton.
Shiko Sir Khaleed gaba daya sun fara bashi haushi,shi dai har ga Allah ya kosa yaga hurril aynin shi. A haka cike da zalama yajah moton yana furta Ibeg muje Huday i'm eager. Dariya yy yana furta Okay Rumio,ka kosa kaga Juliet ko,don't worry ai mun kusa isa kaganta.

Haka dai yayi Dariya da jin maganan Da Huday ya fad'a masa,nan ya furta masa waye wani Rumio da Juliet,aeni a Son ta nafi Layla majnun....😂
Dariya duka suka saka.yyn da Oummu Sulaym ta baxa kunni don ta nadi gulma ta sanar ma Aminiyar nata Suhaimart. Amma sai dai kash ita sam tagaxa gane inda zancen su ya dosa ba. Ita dai kawai abun da take ta nanatawa shine Layla majnun gasky dole ne ta tambayi Suhaimart wannan maganan wai Layla Majnoon don ta fahimci inda suka nufa.

A haka dai ta cigaba da nuna masu Hanya tana kwatanta masu inda zasu shiga ahaka har suka isah cikin Zaria city.

"Duka na yakeyi kaman Zai Karni don kiyayya,yyn da tun ina gani har na soma ganin duhuwa,saukar marin da Oumma na ta wanka ma Zaid yasa ni xubewa yyn da sama² na kejin hayaniyar Muryan Oumma na tana Zube masa Bala'i da hargoguwa tana mai Zubar da Hawaye da kirar Suna na".
Suhaimah" Suhaima na bude idon ki ki kalleni".
Girgixa ni take amma ko numfashi bana iya fitarwa don bana numfashi. Hawaye ne yafara bin kuncin Oumma na,dagowa tayi tana kallon Zaid da ya tsaya ya rasa duk wani abun yi,don shi sam baya a hayyacin sa yy mun wannan duka,tun da a bige yake. Ficewan shi yayi yana maganganu kasa² yyn da Oumma na tayi saurin fita daga soron namu tana taro me Napep daga bakin Hanya. nan ta ciccibe ni sannan me Napep yajah muka nufi Asibitin A.B.U hospital. Wanda da isan mu nan cikin Gaggawa Nurses suka amshe mu hadi da nufan Emergency room dani.

Itako Ommu Sulym a haka suka dinga kurdawa har xuwa Unguwan namu wanda da shiganka basai anfada maka ba kasan unguwan talakawan tilis ne,amma ko a unguwan gidan mu yafi na kowa talauci don Abun ma yy muni matuka. Shikuwa Da Sir Khaleed tun isan su Unguwan yake

tunanin dama da akwai Unguwa masu fama da Talauci irin haka?"  A gsky shi sam bai san da hakan ba,indai ma kam hakan talaucin take tom bai taba ganin talauci ba a rayuwan shi.
"Dako A kozo dai² gidan mu ne Oummu Sulym tayi saurin cewa Sir Khaleed mun zo fah". Tsayawa yy hadi da yin parking din moton nashi,sannan yace mata Bismillah". A hankali ta bude side din ta gami da fitowa daga moton tana mai nufo gidan namu".
" Suko Khaleed da Huday shiru sukayi babu mai iya furta kanzil", Musamman Khaleed da a zuciyan shi yake furta Sorry Hayatee na". Nan da yan lokaci kadan baxan barki ki zauna a cikin wannan Talauci ba". Zaman Nageria ma baxa muyi ta ba inshaallh". Abun da Khaleed bai sani ba shine ba a zuciyan shi yake mgnan ba a sarari ne". Huday ne yy murmushi cike da Tausayin Aminin nashi,duba da yanda ya fada soyayya ga Wannan yarinya,soyayya makauniyya wanda sarai yasan Khaleed bai taba fadawa duniyar irin wannan Son da yakeyi ba. gashi yasan irin soyayya r Khaleed don inyafara baijiin bari sam. Shiru yy yana Aiyana Allah yasa Yarinyan nan ta Kaunace shi kar ta Wahalar da Abokin nashi,don a halin yanxu Khaleed ya rasa wannan yarinya bb shakka komai na iya faruwa dashi".

Tabo shi Huday yayi yana mai furta masa A'a Khaleed ka natsu don Allah. Inshaallh Suhamart Matar kace zata kasance ma yanda kake buri,kuma inshaallh zaka sanyata cikin Farin ciki kaman yanda kake mafarkin gani".
Murmushi Khaleed yayi cike da jin kaunar Aminin nashi yace Na gode Huday da Addu'ar ka gare ni". Kafin Huday yace masa Wani abu ne sukaji Muryan Oummu Sulym tana cewa Sir Khaleed wlh mun zo arashin sa'a don gidan ma a rufe take basa nan dukan su". Saurin kallon ta yy don lokaci guda idon shi ya sauya Kala daga Fari zuwa jahhh..." Nan take Zuciyan shi tafara kisima masa kodai Ciwon nata ne yy worst?. Muryan Huday yaji yana bata amsa da Ohk Badamuwa, Amma bakya tunanin Ciwon nata ne yy tsanani???. A'a ranka yadade inshaallh komai zai zo da sauki".

Ohk Allah yasa,shiga mikai ki gida".
da jin haka Oummu Sulym tayi dariya hadi da cewa" A'aa Ku tafi ai nan unguwan mu ce,yanxu zai kai gida inshaallh ". Okay tom shikenan mun gode". Bakomai ranka yadade". Haka dai suka tafi suka bar Sulaym tsaye don ita kanta tana mmmkin inda Suhamart ta tafi da wannan Yammaci haka". haka dai ta tsaya tagama kusifa abubuwa kan daga bisani ta fara tattaki zuwa layin su".

Niko tunda nasamu kulawar kwararrun likitoci tuni na dawo hayyaci na,yyn da Suka yimun Alurar Bacci Hadi da saka mun drip. Oummu na kam taso daga hankalin ta,babu abun da take tunani sai Kalmar Ga Amana ta nan". Safa take da marwa har Wata nurse da doctor suka fito. Cikin Hanxari tasha gaban shi tana mai furta Doctor ya jikin yarinyan nawa?. Kallon ta Doctor n yy cike da tausayi don ko ba'a fada masa ba yasan suna cikin talaucin Rayuwa. Ki kwantar da hankalin Mama inshaallh ba abun da zai sameta,kinga yanxu ma tayi Bacci". Hamdalah Umma na ta hauyi hadi da yima Doctor n Godiya,sannan ta juya hadi da nufo Dakin da aka kwantar dani tana mai tsaye bakin window don ance ba'a bukatan kowa a ciki. Haka Oumma na ta dinga kallona ta jikin tagan,yyn da Wasu Zafafan Hawaye ki bin fuskan ta,bakin ta kam harda ma Zuciyan ta Addu'a kawai take mun.

A haka fiye da Awanni sannan ta nufi farfajiyar Asibitin don tayo Alwala taga batar da sallah don a lokacin har an soma kirar Ishaa'i.

Niko sam ban farkaba sai Wuraren 8:30pm. Mikewa nayi cike da cije labbana don wani irin tsami danaji jikina yy gaba ki daya. Addu'a nakeyi wanda dai² idona na sauka kan file dina da aka ajiyemun gyefen Gadona saman drower".

A hankali na kai Hannu na hadi da dauko File din na bude ina mai duba rubutun dake kan farar takardan. Wanda duk da ban da wani ilimin zamani,makaranta ma na gomnati nayi,wanda a SS 2 Ummma na ta dakatar dani saboda rashi da ya ishemu akan na soma zuwa aikatau.

Duk da Hakan ina da dan ilimi na na boko dai². Karanta takardan na somayi nan take gaba na yayanke yafadi don kirgina sai da Naji bugawan ta. Cigaba da karanta takardan nayi yyn da hawaye kebin kuncina. Wanda sam banji shigiwan Doctor Zainab ba sai muryan ta da naji tana kirar Sunana" Suhamart " Suhamart ar you okay?". kina ganina da kyau ko??.

Goge kwallah nayi ina mai kakalo murmushin da yake a jini na ne nace mata ehh Doctor ".

Yauwa mashaallh. Nan ta zauna kusa dani tana mai fuskantoni hadi da saka hannun ta ta amshi file din" Shiru kusan minti 5 babu wanda yace komai,kowa da abun da yake kisimawa a zuciyan shi.
Suhamart... " kaman daga sama Naji muryan Doctor tana kirar sunana" Kallon ta nayi akaro na biyu na kuma ce mata Na'ammm...!!!"

Suhamart kiyi hakuri komai da kk gani akan file din ki kisashi a mixanin Kaddaran ki". Komai Allah keyi,kisani ana doraki akan magani zaki warke,kuma koda an vata maki rai kidaina Damuwa plz, idan kina sawa a ranki to tabas xaki ringa xubar da jini ta hanya daban², kaman Ha6o da sauran su: Don haka kisani Suhamart zaki warke inshaallh ".
wani irin mun murmushi nayi mata mai dauke da fassarori da dama, kana nace da ita Doctor kina ganin zan warke? wannan Ciwon fah ba karami bane,kuma sannan koda zan warke Doctor ina zan samu wa'annan zunzurutun Kudi???.
Nan Hawaye ya cigaba da mun Ambaliyya akan fuska ta. Wani irin tausayi na ne yagama kama likitan a hankali ta kai Hannun ta tana mai dafo kafada ta da cewa" Kiyi Hakuri Suhamart kije ki cigaba da huddan ki da mutane,bb abun da Zai kuma samun ki,kuma ciwon baxai taso maki ba sai bayan nan da kaman watanni Uku. Kuma nasan kafin nan kinsamu kudin Maganin. Ga wa'annan magungunan su zaki ringa amfani dasu kan wannan lokaci ". Ta idda maganan tana nuna mun wasu magunguna,nusawa nayi ina mai amsan maganin sannan na kalleta ina mai cemata" Doctor don Allah ina so ne kimun wani alkawari daya ina zaki iyah". Cike da bata kwarin kwiwa irin na likita da majinyaci tace mun fadi maganan ki Suhamart.
Nisawa nayi kana daga bisani na ce da ita" Doctor don Allah so nake ki rufe wannan sirrin wani ciwo na,kar ki sanar ma kowa dagani sai mahalliccin ki,saboda sam bana son Hankalin Oumma na ya tashi,wlh itama ba lfy ne da ita ba". Na fadi cike da matsanancin damuwa". Girgixa kai

Doctor tayi kan daga bisani tace nayi maki Suhamart, amma don Allah duk bayan wata 1 kiringa xuwa ina dubaki naga Ifyn ki kinji"?

Daga mata kai nayi ina dan murmushi na jin dadi. Haka ina A zaune tayo kirar nurse don ta dan gyarani hadi da mun bed making. Doctor Zainab ne ta ciremun Drip din Hannuna don ya kare,nan wannan nurse ta fara aikin ta.
Niko jirgawa kadan nayi duk inda na muskuta ta gyra har ta gama aikin ta. Dai² Oumma na na shigowa gaisawa suka yi da Doctor sannan Dr. Zainab ta fice daga dakin tana mai kara sanar mawa Oumma na da Na sauki sosai kilan mu amsa sallama a daren nan .

Cike da jiin dadi Oumma na ta matso gareni tana furta Sannu Suhamart!!! ya karfin jikin naki???.
Murmushi nayi mata sannan na furta Oumma na naji sauki sosai, don A yanxu Oumma nafi dama jin karfin jikina. duba ki gani !!!... na fadi ina washe mata fararen hakora na". Dariya Oum Rabi tasa cike dajin dadin ganina ta hau cewa" Kai mashaallh" Alhmdllh.

Nufo ni tayi tana zama gab dani,sannan ta bude kwankwatstsayan kwanon da ta tahomun da Tuwo miyar yauki a cikin ta". Kallona tayi hadi da furta Suhamart maza kici abincin nan Ko kyakara jin karfi jikin ki. Murmushi nayi ina daukan ruwa na wanke hannu na a wani Bowl sannan nasaka hannu na da zamman fara cin Tuwon".
Wani magana ne yafara dawo mun a shekarun baya da suka wuce!!!.
Ga Dumamen ki nan ki ci". Tom Oumma Zaid ina spoon?. Hhhhhhh Zaid ne ya kwashemin da dariya,yyn da Oumma ta galla mun Harara da cewa kehhh bana son shashanci,idan kinsaba komai naki na dabi'un nasara,tom nan mu koyi muke da addinin musulunci maza kisaka Hannu kici da yatsun ki kar ki fusata ni".
Ya Hakuri Oumma na bata amsa yyn da nake tsoma hannu na cikin kwanon abin cin.

Murmushi nayi gami da kallon Oumma na da tayimun kurr da ido,a sanyaye na fara kai loman tuwon baki na.

Sai da na kammala sannan na ajiye kwanon tuwon ina Mai Hamdalah ga Allah,sannan na kalli Oumma na ina mai Furta Oumma na I luv u".
Murmushi tayi mun tana mai kallona da cewa" ohh ni Rabiatu!!" Suhamart ni sam nafada making bana jin wannan yaran naki fah".

Okay tom Oumma ya kamata mu amshi sallama don banason kwanan Asibitin nan,suce a biyasu Kudi n gado kuma.

Kallona Oumma na tayi tana zaro ido waje Suhamart haka ne ko???.

Dariya nasaka hadi da ce mata ehmana Oumma ". Ae ko Suhamart bari ki ga tunda dai kin warware mu tafi a ayau din kawai. tana fadin hakan ne hadi da ficewa daga dakin don nufan Doctor.

Niko Bin bayan ta nayi ina mai tunanin furucin Oumma na" Suhamart ni bana jin wannan yaran nake fah". Murmushi nakuma ina mai kuma tuno Abubuwa da yawa" I luv u murmy".
luv u so much too my Daughter". Suhamart ki zo mu tafi kar muyi latti fah"... Tom my boooooo ina zuwa minti 2 kacal. natafi haba Hamma na iyayen Zuciya ina katafi waxai kaini School din?. Basai ki je da kanki ba,ae ke komai naki yi kk kaman wata Babba,amma jibiki Har yanxu baki fi 5 yrs ba... Hohiooooooooo Mummy... Dadddy..." Hamma Huuuuuuuu...

Suhamart ya jikin naki??. saurin juyowa nayi ina furta naji sauki sosai. tom mashaallh yanxu ga takardan sallama nan,bayan Wata daya kai dawo". tom ngd likita. nan Oumma na ta hau gdy hadi da fara tattara komutsan mu.

Me napep ta taro yayin da ya shigo har farfajiyan Asibitin sannan mu ka nufi gida.

A wannan dare sam Oumma na taki yarda ko nan da can na jirga,karoko ma A dakin ta na kwana.

Da Asuba kuwa kan na farka tuni ta fice ta dora ruwan koko sannan bayan ta kammala ta doramun na wanka.

"Khaleed... Khaleed" .... sai da ta yi maganan ya kai sau uku sannan ya dago kan sa yana kallon ta,fuskan sa kam dauke da damuwa fal. Kirjin ta ne ya buga,cikin saurin ta kai Hannun tana safa gyefen fuskan sa da yake kwance kan Resting chair. a sanyeye cike da taushin murya da tsatsan soyayya ta Uwa da dan ta Mum Zaituna ta shafa shi tana furta My baby meke damun ka,baka da Ify ne??.

Saurin girgixa mata kai Yy hadi da juyi akan jikin ta sannan cike da muryan shagwaban d yasaba mata ya fara cewa" Oumma Hayatee na bata da Ify ne". Cikin Saurin tace Ayyah Ita Iftihal din ce babu Ify ai ban sani ba,kuma daxu muka gama mgn da ita tace xata taho Nageria nan da Kwana biyu 2. Wani daddaciyar yawu ya hadiye da kyarrrr....murya can kasan makoshi yace Mummy ba ita ba.

Shiru Hajiya Zaituna tayi kan daga bisani ta tsaya tana observing din yaron nata,lokaci daya ta fahimta tabbas dan nata he fall deply in love...tom amma da waye??? tambayan da ta dinga mawa kanta kenan!!!. Hmm nan ta nisa tana mai ce masa Ohk tom wace ce ita ? fada mun my son" aina take YAR WAYE a Fadin Nageria?. littafin maman teddy wanda bata karanta ba anvar ta back...💃

Shiru yy kan daga bisani yace Mummy ita Hayatee na ba yar kowa bace,amma ki natsu a hankali nan da Kwana 2 xan kawota ki ganta.

Hmm dan murmushi tayi don a tunanin ta shadi fada yake mata". Shafa sumar kansa ta dinga yi

hadi da sakat masa AC wanda a haka da kyar Bacci yy awon gaba dashi.

Niko bayan na kammala wanka nayi sallah ne na sha kokon da Umma na ta ajiyemun hadi da korawa da magani na. saka kayan Aikatau dina nayi,sannan na fito a daki na ina furta Oumma sai na dawo".

Suhamart ina zaki tafi kina fama da kanki??.

Oumma naji sauki don Allah kar ki damu.
Shiru Oumma tayi kan daga bisani tace Suhamart don Allah ki kula,idon baxaki iya aikin ba kai dawo gida kinji? tom Oumma na tafi". A dawo Ify.

Haka na nufi gidan Hajiya Zaituna bayan napep ya saukeni na sallame sa sannnn nayi saurin shigewa gidan,don ko sasan Hajiya Zaituna baje ba,saboda makaran da nayi.nufan sasan Ogan nawa nayi direct don nayi saurin Kaddamar da aiki na,a raina ina tunanin hukuncin da zan fuskanta daga gurun sir Khaleed. don nasan yanxu ni yake jira na hada masa breakfast.
Shi yasa nayi saurin nufan barayin sa.

Shiko gaba daya Sir Khaleed yagama cika yy fam,Haushin kowa yakeji,buri n shi kawai yaji halin da Suhamart din sa ke ciki!!.
Ga kuma yan aikin da suka zo su biyu a makofin ta wai su hidimta masa,gaba dayan su sungama wulakanta don ko sun gaishe sa baya amsawa,sai daure fuska da yakeyi,ga wani hararan raini da wulakanci da yake binsu dashi. Gaban sa Laptop ce yake Operating yyn da yake sanye cikin Farar t.shirt sai boxer iya gwiwa,ko shirib nufan Companyn sa baiyi ba. don shi yau sam bai son ganin kowa sai Hayatee n sa.

Da sallama dauke a Abaki na na shigo falon,wanda kallon inda nake baiyi ba sai ma tattara laptop din sa da yy ya nufi resting room din sa. Jiki na ne yy sanyi kalau. a raina ina cewa shikenan yau naga ta kaina,Allah yasa basun sallame ni bane. musamman yanda naga su Atika na aiki na. Daga masu Hannu nayi nan cike da iyayi suka dago mun,su adole yau sun amshi aiki na,kila nima an sallame ni ne.

Sum² nafara aiki na ta hanyar nufan kitchen don dama su goge falon da sharewa suke. Banfi mintoci 30 ba na kammala masa dan abuncuwa da zai samu yy break. Muryan su Atika naji suna gulma ta hanyar cewa" kuga Wahala Matan da Ansallemi kan mhisd Caterine ta dakatar dake kinxo kina wani wahalar banza.

Gaba na ne ya fadi Kwallah ya ciko min ido. duk da haka ban bar aikin ba sai da na kammala komau sannan na dau yar wayata baby nokia. hadi da nufan Resting room din sa,don na gaishe sa daganan na Wuce gida tinda Naji ansalle meni.

Kwance na hango shi yyn dora Hannun saman koshi idon shi na kallon POP din wurin. Daga dan nesa na bude baki ina furta Sir Khaleed bar da Safiya". Banxa yy mun, wanda sai da na

mamaita sannan ya tashi daga kwancen ya zauna hadi da kallona. Kasheni yy da ido wanda hakan yasani saurin sidda kai ina ambaton Allah,kat yy mun tijara sannan ya koreni,gomma ya koreni da mutunci na!.

Cikin dakakkiyar murya fuska babu wasa yace mun Zo nan". Kallon shi nayi nayi shiru ina tunanin wani abu. don nagama tsorata da shi.

Muryan shi na kuma ji cike da maxantaka yace mun tsoro na kikejiiiii???.....

*Labarin Zuma da Mad'aci na Kudi ne,ga mai bukata zaki turo #200 VIP,#300 SPC,#100 NORMAL na MTN duka ta wannan numbern 08081202932/09137392680.*

*Maman teddy🧸*
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Episode 11*

*______________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪```

*______________________________*

*بسم الله الر حيم الر خيم*

"Tsoro na ne kike ji?.
Shuru na masa sai da kyar na iya girgixa kai na alamar A'a. Hmm nan ya sakar mun murmushi hadi da kai Hannun shi yana shafa sajen gyefen fuskan sa yana mai kuma cemun a karo na biyu (2), Ohk tom na gane zo inason sanar dake wani abune Suhamart". Kirgina ne ya buga mun,duba da yanda naji ya wani kira sunana!!! A raina ne nace dama Sir Khaleed ya san suna na? Tom ta yaya???. ko baxa ki xo ba?. ya fadi yana kafe ni da idon sa wanda lokaci daya naji wani irin kwarjinin sa ya Rufe ni". A hankali na fara ta kowa har Zuwa inda yake a Zaune. Shiko Murmushi yake ta bina da shi har na karako inda yake. Banyi Aune ba sai jin nayi ya kamo hannu na yana Zaunar dani gyefen sa.

Cike da tsoro da mamaki na bude ido na ina kallon sa hadi da saurin matsawa nesa dashi".

Kallo na yayi yana mai kara jin wani irin kauna na yana ratsa duk wani sassa da gaba na jinin jikin shi. Cike da gentle Voice din shi ya fara cemun Sorry Hayatee,banyi hakan dan wata manufah ba. Kawai dai so nake na fada maki wani Abu!!!.

Hmm tom Inajin ka Sir Khaleed, na fadi ciki da Rawar dari wanda daka ganni kasan a tsorace nake. Dariya yy gami da cemun Okay Rufe idon ki". Kallon sa nayi cike da mmki sai kuma ganin ya kashe ni da ido yasani Bin umarnin nasa ta hanyar Rufe ido na". Murmushi yy nan yakai Hannun sa yana riko nawa hannun wanda ya sani Saurin bude idona wanda ban shirya ba. Murmushi yymun mai kayatarwa nan yace mun Okay kar ki rufe idon naki,amma plz ki tsaya yanxu xan rubuta maki wani abu ne.
Shiru nayi ina mai kauda kai na gyefe had'i da mika masa hannnun ina mai Ware taffa na gare shi. A bangaren Zuciyata kuwa sosai nake mamakin mai Sir Khaleed Zai yi mun haka?. Tom dama wai yana magana ne haka???. jin saukar Biro a kan tafin Hannu na yasa ni saurin rintse ido ina Addu'ar Allah yasa yayi sauri yagama abun nan nashi,kan wasu kuma su shigo ayi mun mummunan Zato...
Koda ya kammala Rubutun ina jin shi ya rike Hannun nawa bai sake ba kusan minti Biyar,kana ya saki Hannun nawa yana fadin Suhaimart kar ki bude hannun naki sai ba kowa kuma sai kin samu natsuwa kin kwantar da Hankalin ki waje daya kinji?.
Daga masa kai nayi ina saurin mikewa don duk na kosa na gudu na bar dakin. Sai kuma tuno da ae ni ce Zanyi Serving nashi yasa ni saurin sidda kai ina furta Sir Khaleed Breakfast dinka fah ya Kammala.
Murmushi yayi mun Hadi da cewa" Nop kije ki huta kiyi Bacci don nasan baki da lafiya And then
```

jikin nan ki na son kulawa da hutu,kije side din ku ki kwanta kinji?.
Cike da tsantsan mamaki nake bin sa da ido da kallo wanda sai da yayi mun murmushi yasa ni saurin daga masa kai hadi da ficewa daga Restingroom din nasa wanda yana yin yanda yake bina da kallo har tuntube da yatsuna nake yi ina furtawa a zuciya ta,Allah yasa Ba iskancin nasa bane da'ake bani labari zai dawo kai na". kee Suhaimart ke awa ne da Sir Khaleed zaiyi yunkurin lalataki?. bayan ga yan mata masu ji da aji yayan hutu yayan masu da shi da kullum suna aikin sunturi a gidannan shikuma yana aikin Wulakanta su???. Zuciya ta ce tabani amsa da hakan. A haka dai nake ta tunani tom ya akayi Sir Khaleed ya san nayi Rashin lafiya. A haka dai na nufi Side din mu ina zancen zuci don a tunani na Mhiss Caterine ta sallameni kaman yanda naji Wa'ancan suna gulman su,amma abun mmki da shiga na ta nufoni tana tana shafa gyefen fuska ta da tambaya na ya karfin jikin nawa??? Anan na bata amsa da naji sauki,Oummu ce ta taso itama tana min sannu,kan mhiss Caterine tace ta kaini Dakin mu na samu na kwanta na huta,yau baxan yi aiki ba sai zuwa gobe innaji Sauki".

Haka dai Muka shiga daga ciki ni da Oummu Sulaym yyn da nan Oummu ke ta kwadun Sannu har nagaji da amsawa". Don Oummu Sulaym Sam bata gajiya da surutu haka Allah yayi ta,dakanta ta kwantar dani hadi da gyeramun fillow ina mai tayar da kai na dashi.

"Ban wani jima ba bacci yy awon gaba dani".

________________________________

Hutawan ka Lafiya allah yajah da kwanan yarima mai jiran gado,gaban ka da baya Mulki ne jinin sarauta,Naman giwa ta fi karfin hargogowan yara,yaro maza gaexaya je kanemo tsaranka,yarima Abdoul daya tilo, hutawan ka lafiya ranka yadede...
Duk wannan kirari da ake sheko mawa Yarima bashi yasa shi daga kai ya dube su ba,sai da ya kwarari kusan mintoci 10 sannan ya daga masa kai a hankali,wanda inba ka kuresa da ido ba,tabbas da baxaka fahimci yy wani Reaction ba.
Wani bafade ne ya baxa malilin malin sa yana zaman dirshan gaban yarima duba da ya fahimci da bayani bakin yarima,Amma mulki da isah ta hana sa bude bakin. Ni dai Labban sa kadai naga yana motsi sai kuma naga Wannan ba faden ya furta angama ranka ya dade Hutawan ka lafiya...." yana fadin haka Prince Abdoul manan ya mike yyn da Fadawa nan suka tashi suna mai mara masa baya.
Shiko wannan bafade da mikewan sa ya nufi Barayin Fulani wanda a hanyansa ta zuwa suka hadu da Jakadiyya".
Sanar mata da sakon yarima yy akan yana so afara shirye² na tafiyan sa zuwa Zaria a satin nan da yardan Allah". wanda yana sanar mata ya juya hadi da nufan barayin Yarima".
Itako Jakadiyya baki Uwar magana tuni ta juya hadi da komawa barayin Uwar dakin nata Fulani don ta sanar mata da Tafiyan Yarima zuwa zaria,wanda su sam basu san mai zai kai shi can din ba".

Niko Suhaimart ban samu farkawa ba sai can Wuraren 4pm. don lokacin tuni aikin mu ya wuce sai kuma masu aikin dare sune suka amshe mu".

Waigawa nayi gyefena nan naga babu kowa don haka sai na tashi daga Zaune baki na na dauke da addu'an tashi daga Bacci".
Kaman wanda aka mintsila na tuno da Rubutun da Sir Khaleed yy mun don haka ban tsaya wata² ba na bude Hannun tawa ina mai kura dakwa² n idona don ganin mai ya rubuta mun".
Kirjina ne ta buga nan take,kara bude ido na nayi ina mitstsuke su don tunanin ko ba sa nuna mun dai² ne,Amma still abun da nagani shine dai. Nan take Gumi ya fara karyomun,kwallah ya ciko mun ido a sarari kam furtawa nake wayyo niiii...wayoooo ni Suhaimart, Sir Khaleed mai yasa zaka cemun haka???? ko so kake dan Abincin da muke samu sanadin aiki a karkashin ka shima mu rasa!!! Bakomai ni nasan a kwanannan watan Korana daga aiki yatsaya...Ina maganan ne hadi da Zubar da kwallah,banji shigowar ta ba sai muryan Oummu Sulaym naji tana cemun Suhaimart mai naji kina cewa ne? Meye Sir Khaleed din yy maki??? Kuka na rushe mata dashi ina kwantar da kaina bisa kan kafadan ta ina furta Oummu Sir Khaleed ne,shikenan zai jah mun sallama,yanxun in ankoreni ina xan je?".

Rungumo ni Oummu Sulaym tayi tana furta haba Suhaimart wlh ajiki na nakejin Babu abun da zai faru babu wlh,meye wai Sir Khaleed din yy maki ne???.
kasa bata amsa nayi sai dai kawai ware mata taffan Hannu na nayi ina mai kawar da kai gyefe. Bin Hannun nawa tayi da kallo hadi da Karanta kalmar kamar Haka: I LOVE U SUHAIMART!!! DO U LOVE ME???.
Wani ihu mai hade da kara Oummu Sulaym tasa hadi da kankane ni tana furta wayyo Suhaimart dina,yanxu tom mai zaki ce???.

Zaro ido waje nayi ina kallon ta tabbas ban taba yarda da Oummu Sulaym bata aiki da hankalin ta ba sai yau, tom ita har tana ganin na amince masa? ina badani ba,ai Sir Khaleed sam ba aji na bane,yafini kaman sama da kasa,ai Babban goro sai magogin karfe,Ana babbakan giwa wake jiyo kaurin zomo?, Ae komai kwarya ce tabi kwarya!.
Duk maganan nan a tunani na a zuciya nakeyi but unporturnetly a sarari neke ta zubo su".

muryan Sulaym na tsinkaya tana cemun" Maganan ki haka ne Suhaimart, tabbas Kwarya tabi kwarya ne,Amma kuma kar ki mance ita Kwarya ta gari..?
Don haka ni sam ban goyi bayan ki janye kiki yarda da amincewar Soyayyar Sir Khaleed ba,Amma zan maki Uzzuri akan kija masa aji na martaban ki ta ya mace. ta fadi tana mikewa wanda da'ala Oummu fushi tayi akan maganata, sai da ta kusa ficewa ne daga dakin na tsinkayo muryan ta tana cewa" Amma kisani K'awa ta wlh amincewar ki kan soyayyar Sir Khaleed kaman taimakon sa ne zakiyi,don a halin yanxu Sir Khaleed yana bukatan taimakwan mutumiyar kirki a rayuwar sa bana banxa ba". Sir Khaleed babu wasa a furucin sa da gaske yake yana Kaunar ki,kuma so na ki zama uwar yayan sa,kisani ni ba karamar yarinya bace tuntuni na dade da fahimtan hakan,duk da sunan shi miskili ne amma ya kamata tuni ki fahimci hakan!!, Don haka ni baxan maki tilas ba,Suhaimart inkin kaunaci Sir Khaleed wlh zaki ga ribar shi gaba,kuma komai kkyi ina maki Izirin yarinta".
Tana gama fadin haka ta fice daga dakin,yyn da niko da ido nabita da kallo,a sarari na furta,Wlh sam baxan amince ba,sarai nasan Halin wannan bawan Allah mata nawa yasaka kuka akan soyayyar shi agaban ido na".

ina sam ba dani ba,wai kina wani Zanga ribar shi,wani riba xanga dai asarah,don in Hajiya Zaituna tasamu labarin nan ae wlh yanda ta tsani talakan nan sai tasa ankarar da dangin mu duka...
Mtswww wlh Sir Khaleed kayi hakuri duk da nasan kawai yimun dai kkyi,inma tunanin ka ni yar iska ce tom ba haka nake ba". haka na dingi maganganu na ni kadai ina mai mikewa don nufan Bandaki nayo Alwala. Bayan fitowa na ne nayo Sallah dako idarwa na ban tsaya ko juran Oummu Sulaym ba na biyo hanyar gida,a tunani na ma Sir Khaleed xai iyah sakawa a kamo ni ta karfin tsiya. A hanya kam da zan fice gate ne na ci karo da Wata Zukekiyar Budurwa wanda ashe karu ta haura 30 a duniya, gaba daya shigar ta babu na kwarai ta saka wasu damammun Riga jecy da wandon jean kanta da wani siririn mayafi. Sarai ta ganeni don randa da taxo har fada ya kauraye tsakanin ta da wata karuwar tasa mina wurin don har dani cikin wanda suka serving nasu, kauda kai na nayi gyefe ina kiyaye ma kaina mutunci na".

Heeeee....." abun da tace mun kenan,wanda dajin hakan nasan dani takeyi yasani waigowa ina kallon ta. Arch.Khaleed na nan kuwa???... ta fadi tana wani ya tsina mun baki hadi da wani farrr da ido sai kace nine Sir Khaleed din. Daga mata akai nayi alamar ehhh,sannan ta juta hadi da nufan cikin gidan yanda ko take karkada duwawuka sai da naji mata kunya don girgixa kai nayi na wuce ganin yanda sojojin gidan da masu aiki maza ke bin Duwawun nata da kallo.
Haka kam fa fitowa na na fara takawa a kasa don a yau bana da na abun hawa,shiyasa nake takowa tundaga gidan Hajy Zaituna har cikin Layin mu.

Jiyo Horn din moto a baya na yasani Saurin juyowa hadi da tsayawa cakkk a wurin don ganin waye ke bina da Horn".
Fuskan sa sake yanda nasaba ganin sa ya fito hadi da yi mun Murmushi yana furta Har kin tashi?
Dan murmushi nayi masa ina mai kara bin sa da kallo,hadi da ce masa ehhh Yahh Huday yanxun nafito".
Kirjin sa ne ya buga jin kirar sunan da nayi masa, a zuciya n shi yana son tuno inda ya taba jin wannan murya dakuma mai kirar sa da wannan Sunan Amma ya kasa".
Ganin haka yasa shi saurin sosa kyeya yana furta tom shigo na kai ki gida" kinga yamma tayi.
Kallon sa nayi gami da dan zaro ido na waje kan daga bisani nace a'a nagode yanzun fah zan kara ka.
Daure fuska yayi gami da ce mun" okay ni wato Suhaimart ba yayan ki bene,bana da matsayin da Zance kiyi abu kiyi,amma idan da Khaleed ne ai zaki shiga ".
Shiru nayi bance masa komai ba,sai kawai na nufi moton inajin ba dadi akan tirjiyan danaso masa,Murmushi yymun cike da miskilamcin sa da ya zaman masa jini tun fil azeem ya bude mun murfin moton nashi,yana mai rufowa....Tunda muka shiga moton bai kuma cemun komai ba,sanin hali yasa ni nima Shiru ina mamakin miskilanci irin na Huday,don narasa wayafi wani tsakanin sa da Sir Khaleed.

A dai² PZ wuraren Chiken republic ya tsaya,kallona yayi yana furta mun ina zuwa Minti buyu. yana fadin haka ya fice daga moton hadi da nufan cikin wurin Chicken Republic din. Baifi yan mintoci ba sai gashi gidan baya yafara budewa sannan ya rufo hadi da dawowa gidan gaba

wurin maxaunin sa yajah moton muka tafi.

Har kofar gidan mu ya sauke ni,sannan nayi masa sallama zan tafi,anan ya daka tar dani yana fitowa hadi da bude moton yana dakko wasu manyan ledoji guda biyu hadi da mikomun,Suhaimart ga wannan ki gaida Oumma". Tsayawa nayi na kasa amsa,wanda ganin haka yasa shi kawar dakai yana shan mur. a hankali nasaka hannu na amsa ina masa gdy sannan nayo cikin gida,Murmushi yymun kan na shige ne yakira sunana.
A sanyaye na waigo.
Buden bakin shi cewa yayi innako ma mai zan ce kince a fada ma Khaleed???.
kasa basa amsa nayi sai dai dan Murmushi danayi ina mai kutsa kaina cikin soron gidan mu.

Murmushi yy hadi da nufan moton shi wanda bai tada ba sai da ya kira Khaleed ya sanar masa da ya kawoni gida sannan yajah moton,don dama a idon shi yana kallona ta Windown sama da zan fita nice bangansa ba,ganin na fita yasa shi sanar ma Huday da yake kan Hanya akan ya maidoni gida".

Bangaren Oummu Sulaym ko batayi mmkin ganin Babu Suhaimart ba,don sarai tasan Halin ta, Murmushi tayi mawa kanta,kan daga bisani ta tarkato kayan ta hadi mawa Mhiss Caterine sallama sannan ta dau hanyar tafiya gida".

Itako wannan karuwa da shigan ta side din Sir Khaleed direct falon shi ta kutsa kai kaman dakin Uwar ta,haka sauran Ma'aikata ke gayar da ita amma bi ta kansu ba tayi ba,burun ta kawai ta ci karo da Sir Khaleed yanda ta debo fitinan ta da magungunan da tasha ma cikin ta to ta sauke jarabar ta akan shi don duk don shi tayi wannan aiki...
Tafiya kawai takeyi amma jin ta take a sama,banda tsiyaya babu abun da takeyi...sai Uwar gumi da take futarwa". Fitowan sa daga Privacy kenan daure da towel a kugun sa daya hannun sa kuma yaba dauke da karamin towel yana goge sumar kansa...
Nufo sah kawai tayi gadon gadon tana wani fixgar numfashi kaman numfashin nata zai dauke duka.......

Littafin Zuma da madaci na kudi ne,VIP da Normal #200.
Transfer #200 SPC 300.Duk ta wannan number 08081202932.09137392680.

*#SHERE TO ANOTHER GROUPS*

Mu tare a episode na gaba💃.

Maman teddy🧸
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Episode 12*

*______________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*________________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*

_Dedicated to my teddy🧸Wannan pagen taki ce y'a d'aya tilo😂._

*_Domun samun Littafin Zuma da mad'aci tun daga farkon sa har karshe zaki tuntubi wannan number 09137392680/08081202932._*
_*Ma'ana zaki turo #200 idan VIP,idan kuma SPC ne #300,100 kuma NORMAL kenan....*_

_*Plz don't miss dis novel,the latest  Hausa nvl in 2021.*_
_*Do not miss this Novel Hajiya ta,idan baki karanta ba an barki a baya Hajjaju....💃*_

*__________________________________*
```

Sai a sannan ya ankare da isowan ta bedroom din nashi,don haka cikin mugun tsawa da yake firgita su ya daka mata wannan tsawa ta hanyar daga mata hannu yana mai cewa"Heee Stupid get out my Hause".
Ya fadi maganan ta hanyar yi mata nuni da kofah wato ta fice ta basa wuri".
Kallon sa tayi cike da Rashin fahimtan anyah Khaleed din ta ne,Khaleed din da ta sani ne ko wani ne dai da ban. Bin jikin ta tafara yi da kallo,ko shigarta ne batayi atracting nasa ba. ganin komai nata ya baiyana masha'allah babu wani mahalukin namji da xata gufta ta gaban sa bai ji wani iri ba yasa ta kara sauke idon sa akan na Khaleed da har ilah yau Fuskan sa take a murtike kaman bai taba sanin yanda ake dariya ba".
Bakin Zeebu har rawa yake da kyar ta iya furta masa Khaleed youuuuu???.
Mtssswwww wani dogon tsaki yajah hadi da nanata kalmar I said you should get out to my Hause,Idan kuma ba haka ba i will call my guid to fushh you away... ya fadi yana kama hanyan nufan falon sa". Saurin shan gaban shi tayi gami da furta Khaleed Da gske kk na tafi na bar ma gidan ka?" Ko dai kasha wani abu ne???, Bai bata amsa ba illah ra6ata da yy ya wuce ta gyefen ta yana mai nufan farfajiyan gidan Had'i da kwala kurar Securities maza guda biyu,wanda su ke da alhakin shigar kowa Side din sa". Cike da tsawa ya fara masu bayani akan daga yau kar su sake barin wata y'a mace ta shigo side nashi ba tare da amincewar sa ba,kuma su zo su fitar masa da wancan matan". yana fadin haka ya juyahhh fuuuuu hadi da shigea ciki,wanda a falo suka ci karo da Zeebu tana mai mmkin wannan dabi'a ta Khaleed da ya bijiro mata dashi lokaci guda,don abun jin shi take tamkar a mafarki. Kafin tayi masa mgn ne tuni Security ya daka mata tsawa ta hanyar cewa" Hajiya Outt".....
Kallon Securityn tayi wanda da kaganshi kaga yare hausa bata ganshe sa ba. da kyar cike da dacin rai tace" Heee do you know Who I'm i!!?? I think you are Nonsence,ibeg give me chance to go"..tana maganan ne cike da matsanan cin bakin ciki da tashin hankali". Shi dai security matsawa baya yayi hadi da ce mata Oyyah go Out Hjy...Out". yanda kasan yana kada karya. Haka tasa Kafan ta ta fice daga side din tana mai nufan Farfajiyan gidan don ta shiga moton ta ta sulale babu kwarin gwiwa".
Suko sauran ma'aikatan barayin nashi kowa haka ta kama kanta,don yau sun san Sir Khaleed a zuciya yake da kowa,tunda har ya bata ran ta gaban goshin sa Wato Zeebu". kowa a zuciyan sa tambayan kansa yake mai ya kawo mawa Sir Khaleed wannan Sauyi lokaci guda ne?.

Niko Suhaimart da shigana gida na tadda Oumma na tana Zaune tsakar gidan mu tana sukola,da ganina ta hau mun murmushi yyn dana furta Oumma na Barka da gida".
Da murmushi da kuma jin dadin yanda na koma kaman bani nayi ciwon ba tace Ifyl Suhaimart ya aikin naki"?
Aiki Alhmdllh Oumma na".
Ajiye kayan hannuna nayi gyefen dakin mu ina mai cire hijab din jikina da furta Oumma bari na karke Sukolan!!.

Na rabaki Suhaimart " jiya fah aka sallamomu daga asibiti,ae bar sukolan nan sai kinji sauki,maxa shiga daki yanxun zan shigo nima". Tom Oumma na ga wannan!!'.
Nan na miko mata ledojin da Huday ya bani,cike da mmki Oumma ta saka hannu ta bude

ledojin da nan taga daya kaji ne cikin sa,dayan kuma kayan makulashe nd iri².

Kallona tayi wanda cike da daurewan kai Tace mun Suhaimart a'inah kika samu wa'annan kayan?.
Shiru nayi na kasa cewa kala" don sai na tsinci kaina da kasa furta mata da Huday ya bani".
Muryan ta Naji tana cewa" A wurin aikin ne aka baku?.

Saurin daga mata kai nayi da ehhh,sannan kan ta bani wata tambayan nayi saurin shigewa dakin nata...Itako Oumma sam Zuciyan ta bata bata ba,amma tarasa ta hanyar da zata fasalta mawa Ranta dangane da wannan kaya dana bata".

Don tana da 100% garanti akan Tarbiyan da tabani,tasan baxan je nayo abun da zai bata mata ba,amma kuma ranta cewa take dole takuma kula da Suhaimart, don Suhaimart tamkar amana ce Allah ya bata". Bata da kowa sai itah da Zaid,shi kuma ga yanda yake,girman ajiki yake kadai.

Bangaren Sir Khaleed kuwa sosai yakejin tsanar duk wata  y'an matan sa na banza,dama wanda suke masa true love duka ya watsar da lamaran su,burin sa kawai yaga ya mallaki Suhaimart, wanda da ya rufe idon shi fuskan ta kawai yake gani tana masa gizo,tana sakar masa da wannan kayatattciyar murmushi n nata,mai sakar masa da Kasala,dajin Zuciyan shi cikin Annashiwa da jin dadi".

Rufe i don shi yy yana mai furta I Really love you Suhaimart ".  Sai kuma kaman wanda aka tsikara ya mike hadi da nufan wani Daki dana gani daga gyefn bedroom din nasa,bin bayan sa nayi wanda da shiga na naga ashe Achitect Room din shi ne, Wani bord ya dauka hadi da daukan kayan colouring yafara zanata a kan bord din yana mai jin duk wani dakika son ta nakuma nikkuwa a cikin Zuciyan sa, a sarari kam Addu'a yake Allah yasa Suhaimart ta kaunace shi koda kuwa kwatan son da yake mata ne, don shi sai a yanxu dayaganta ya tabbatar da itace komance fatan shi,kwanciyar hankali,kuma tabbas ya yarda da rasa Suhaimart a rayuwan shi Babban Illah ne wanda sam baxai iyah jurema hakan ba".
Haka dai yake ta drawing nata abunka ga Archetecture tuni yayi nisa yana zanata hadi da binta da kalaman masoya masu kwantar da hankali kaman tana gaban sa".

Hmmm muje xuwa masoyan Maman teddy🧸. Don nasan Tabbas zakuyu jinjina ga wannan labari mai taba zuciyan masu karan tawa. Koya Lamarin Khaleed da Suhaimart xai kasance Allah masani,muje dai Xuwa kar ku mance nice dai taku har kullum mai maku fatan Alkhairy da nuna kauna gare ku: Wato Ayshatou Moh'd ( Mmn teddy🧸).

******************************

*JIHAR GOMBE*

Nana Aysha wai tunanin me kikeyi ne haka?". Tun da yarintan ki kar kifa dorama Zuciyan ki

damuwa".
Dagowa Aysha tayi hadi da kallon Ammaie da take tsaye rashin karkashin y'an nata duk ya ishe ta.Da kyar Aysha ta iya kakalo murmushin dole ta hanyar cewa" Ammie wlh bakomai,kawai dai Rayuwar Yarima Abdoul ne yake damuna,wai ace Ammie mutum har ya isa musali ya isa munxali,anki bude masa Sirrin da aka rufe tsawon shekaru,inba a sanar masa yanxu ba tom yaushe zai sani,yaushe zai shaida ni y'ar uwar sa ce ta jini,kullum yana mun kallon bare,wlh na gaji da wannan Buye masa matsayuina da akeyi". Ta fadi tana mai cuno baki gaba".

Murmushi Ammie tayi tana mai zama gyefen Diyar ta ta, A hankali ta fara mata magana cike da taushin murya,Nanah Aysha ki fahimceni,sam bana son Karajin wannan mgn daga bakin ki,kisani idan maganan nan ta fita nice za'a kira da babban kawai,wannan sirri ne datake Rufe tsawon Shekaru 30 da dori,kuma ni na sanar dake tsakanin ki da Yarima Abdol Manan ne badon komai ba sai don Ki samu soyayya daga gareshi,ta haka ne zamu shayar da fulani mmki,kuma abun da take ganin baxai yiwu ba,xataga tayiwu". Amma idan kikayi gaggawan sanar mawa Da Abdoul Manan cewa" Fulani ba mahaifiyar sa bace,tom wazaki ce mahaifiyar tasa?

Dole ne mu cigaba da Rufe wannan sirrin Har Allah ya nuna mana lokacin da komai zai fito sarari makiya kuma suji kunyah,dan hakin dama daka raina shike tsone maka ido. Nanah Aysha kicigaba da hakuri,duk hantaran da Abdoul manan zai nuna maki kar ki damu,kisani bayan wuya sai dad'i".

Nisawa Nana Aysha tayi kan daga bisani tace" Ammie shin kinji Labarin tafiyar Hamma Abdoul kuwa??.
"Wai naji ance zai tafi Zaria ne,but bansan maiye manufar Zuwan sa can din ba".
Dariya Ammie ta sakar ma diyar ta ta,kan daga busani tace" Naji lavarin hakan Aysha,Don maimartaba oready ya sanar mun,Sannan zuwan Abdoul Manan Zaria ki sani ba wani avu bane zai kai sa illah dawowan Aminan nasa wato Huday,da Khaleed.
Ammie da wayyo dadi da gaske???, indai ko Haka ne A satin nan zan tafi Murmmyn Khaleed".
Nayi mata Hutu can,cox Ammie na nasan In Hamma Abdoul bai sauka gidan ta ba,to kilah baxai wuce gidan yah Huday ba".

Dan murmushi Ammie tayi cike da jin dadin maganan Ayshan,da cewa xataje yima Yayar ta wato Hajiya Zaituna Holiday don sam Aysha bata son shiga cikin jama'a,amma yau sanadin Yarima Abdoul zata je har ta jima can Garin Zaria. kai masha Allah". Abun da Ammie tace kenan,kan ta mike tana furta Aysha Abban ki na kan Hanya,bari naje na cigaba da shirin dawowan sa!!".

Tom Ammie nima yanxu inna kammala Duba magazine din nan zan fito".

Wahhh ke din ce zaki fito,bayan kin fara duba Magazine din ki na fama"!. Hmm ae nasan fitowan ki ba yanxu ba". Dariya Aysha tayi tana mai cigaba da Gyara Medical glass din ta,tana karanta wasu news.

Ita kam Ammie Juyawa tayi tana mai rufo mata kofah,a ranta tana jajan ta hali irin na Aysha,kullum ka ganta a koke duba Jaridu,idan baka ganta anan ba,zaka ganta tana watching News...Ae wannan ko shi SENATE IBRAHIM DUTSE wato ma haifin Aysha bai wannan Resarch din irin nata lokacin yana da Kuruciya haka".
Haka Ammie tayi ta zancen Zuciya har ta isah Tanfatsetsen falon ta da yasha Ado da kayatuwa har ya gaji".

Ma'aikatan ta ne suka fara mata barka da isowa",yayin da nan ta amshe su cike da karramawa irin ta matan da suka san darajar dan Adam,don yanda take masu sai da na fada duniyar tunanin Anyah Ammie Safiya da Mum Zaituna yaya da kanwa ce???. Hmm Hakan ne tunda da bakin ta Ammie Safiyya ta fadi".

*GARIN ZARIA*
Bangare na kuwa ni Suhaimart A washe gari da sassafe na kammala shiri na na tafiya wajen Aikatau dina dana saba,don haka bayan nayi mawa Oumma na sallama ne na yo waje hadi da tare me napep gudun kar na makara na samu wata matsalan dan gane da aiki nah".
A haka muka shigo G.R.A zaria,wanda jefi² nake kallon wurare dabam².
Ido na ne ya sauka kan wani gida,wanda nan take naji kirjina ya yanke ya buga,saurin dafe kirjina na nayi,ina mai karanto Ayar Allah,har na samu natsuwa,wanda duk da hakan girman gidan har Ilah yau bamu wuce ta ba,gida ne mai mahaukacin girma da tsaruwa,wanda gaba dayan sa yake mamaye da Sojoji da jami'an tsoron lafiya.Zufah ne ta hau karyomin ta koinah,tabbas a jiki na inajin na taba Rayuwa a wannan gida". Amma kuma a yaushe a wani lokaci ni ban sani ba!!!.

Dafa kaina nayi ina mai son tunowa amma na kasa,Wage dankareren gate din da akayi yasa mai Adaidaita danake ciki dakatawa don wanda aka bude ma gate din gidan ya fito sannnan muyi gaba".

Idona ne ya sauka akan sa,wanda a sarari na furta la shakka dama nasan kaine Ya Huday ". kawai sai naji zafafan hawaye na bin koinah na fuskana. Ta jikin madubin me Adaidata na kare ma Fuskata Kallo,yanda nake a kode a kuma jeme,ga wani baki da nayi,uwa duniya baxaka taba cewa Ni Suhaimart fara ce karr ba".
Share Hawayen kan Fuska ta nayi ina mai bai Uzuri A rayuwa,don tabbas wanda yasanni abaya baxaya taba cewa nice dai Suhaimart ba'.

Tayarda da napep din da yy ne yasani ankarewa da Moton Huday ya wuce,nan naga me napep din yana wani irin gudu dani,wanda cike da sanyin murya ta nace Don Allah Bawan Allah kajah ni a sannu".

Tom Hajiya" Wannan saurin dana keyi wlh badon komai bane,saboda Nayi saurin kai ki ne,Saboda kinsan mai neman takarar mataimakin Shugaban k'asa wato Alhj. Muhammad Harun Ya dawo kasannan yau...

inkuma su kafara isowa baxamu samu hanya ba".
Gumm na masa da baki,ina mai kara maimata Sunan Mataimakin shugaban kasa Alhj. Muhammad Harun...
A haka banyi Aune ba naga ya tsaya a daga nesan gidan Hajiya Zaituna don sam mutane basa rabar kofar gidan,saboda wa'annan murda² n sojojin da suke safa da marwa hadi da bin mutane da mazurai".

Sallamar sa nayi ta hanyar basa kudin sa sannan na nufo cikin gidan,ina mai gaisar da Securitie din da sojojin sannan na nufi barayin Hajiya Zaituna,don na gaisar da itah".
Hmm sosai na wulakan ta duk da daman wannan halin tanne wulakanta talaka,mussaman mai mata aiki a karkashin ta".
A haka na nufo side din Sir Khaleed, wanda da isana na tadda mhiss caterine da mataimakin ta wato Mr. faul".
Gaishe su nayi saurin yi ina mai nufan kitchen don na kammala ma Sir Khaleed breakfast.

Cike da natsuwa na fara komai,wanda ba tare da na dauki wasu lokuta ba na kammala masa,hadi da fara jera komai a kan dirning area.
Sai da na kammala komai ne sannan na daga kaina hadi da bin Agogon falon da kallo,yyn da take nuna mun karfe 7:15am.
Shiru nayi ina mamakin rashin fitowansa har yanxu,wanda a haka ina tsaye fiye da mintoci nan na nufi,wani dan daki daga wajen falon nasa yyn da nayi saurin daukan Sweeping Stick,sannan na dawo na fara gyeran falon nasa da kitchen da sauran dakunan da suke a jere a falon.
Bayan na kammala ne na dauko Mopper na fara moping din ko inah na falon,da kammala wa nane na fara bin Falon da Room freshner,ina a haka na fara jiyo takonsa hadi da shakan daddadan turaren sa,don dama tuni na fahimci Sir Khaleed ma'abocin son Kamshi ne,komai nasa ka daga sai kaji yana wani irin kamshi na dabam.

Dariyar su naji wanda sam bansan shi da waye suke wannan dariya ba". Don nasan Sam Khaleed ba wani harka ne dashi ba". Ajiye Turaren hannu na nayi a gyefen wani Table,yyn da dai² suna karakowa inda nake a tsaye". dago kai na nayi,yayin da dai² yana kallo na,saurin sidda kai kasa nayi ganin hada idanun da mukayi,shikuwa murmushi ya sakar mun mai kayatarwa".
Sai da suka taho gab da nine cike da Sanyin murya na nace masu Barkan ku da isowa,antashi lafiyahh!!!?
Babu wanda ya bani amsan gaisuwa ta,wanda hakan ya haddasa mun faduwar gaba,tom kodai yaji Duk abun da nayi mawa Sulaym jiya ne???.
Hmmm nisawa nayi sannan na kuma nufan su,yyn da dai² suna zama akan dirning. Kwallah ne ya ciko mun ido,nan nayi saurin mayarwa don kar su lura,amma abun da ban sani ba shine tuni komai nawa a kan idon shi nakeyi". Ya fito ni yayi da Hannu". Cikin sauri na karaka inda suke Wanda a hankali nake komai na nafara serving nasu, don ban kuma ce masu komai ba". Shiko Sir Khaleed tuni yayi nisa a fadawa dunuyar tunani na,don Magana Abdoul manan ke masa bai ma san yana yi ba".

Komai na Suhaimart burge sa yakeyi,sam baya gajiya da kallon ta,binta yake da kallo yana mmkin Saurin kukan ta mai kama da shagwaba!!.
Sam bai san lokacin da labban sa ya furta I love u Suhaimart ba".
Due a hankali yy maganar don ita hankalin ta sam baya tare da ita ta kosa ta basu wuri,don tuni ta lura da dukan su irin samarin nan ne yan duniya idon su carrr yake,shiya sa sam bata ji mai ma yace ba!.

Murmushi Abdoul manan yayi yana Kallon sa dacewa " Yah Mutumin Kodai ita ce?.

Bai basa amsa bai sai murmushi da yy masa,wanda dai² ina kallon su da furta Bismillah!.
Murmushi Sir Khaleed yy hadi da mikewa daga Zaunen da yake Matsowa dab dani yayi hadi da jah mun kujera,Hayateee na Zauna nan muyi break".
Murmushin da ke dauke akan fuska ta ne na daina lokaci guda. saurin waigawa inda Abdoul manan yake nayi,nan take kwallah ya ciko mun ido,lokaci daya hawaye kaman wanda aka buga ya fara xubo mun".
Girgixa masa kai nayi alamar ya rufamun Asiri,kar ya jah mun fitina...

Littafin ZUMA DA MADACI ta kudi ne,Normal and VIP zaki turo #200, idan SPC ne #300. duka ta wannan Number 08081202932./09137392680.

Maman teddy🧸
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Episode 13*

*______________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*______________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*

_Dedicated to my teddy🧸Wannan pagen taki ce y'a d'aya tilo😂._

*_Domun samun Littafin Zuma da mad'aci tun daga farkon sa har karshe zaki tuntubi wannan number 09137392680/08081202932._*

_*Plz don't miss dis novel,the latest Hausa nvl in 2021.*_
_*Do not miss this Novel Hajiya ta,idan baki karanta ba an barki a baya Hajjaju....💃*_

*________________________________*

Cikin sauri don bakin shi har Rawa yake sam baya son ganin 6acin ranta ko damuwa a tare da ita,da sauri ya furta i'm sorry Suhaimart bazan sake ba tunda bakya so".
Ban basa amsa ba illah saurin jah baya da nayi ina mai barin falon da sauri yykin da Hawaye har illah wannan lokaci bai dai na Zuba mun ba".

Zama yayi Da6as,jikin sa sam babu isashen kwari,Da kaganshi zaka fahimci yana cikin damuwa matuka". Cike da jin matsanancin tausayin Sir Khaleed Abdoul Manan ya kai Hannu ta hanyar dafa kafad'an Aminin nashi,Alaman Ban hakuri Bisa komai".

Dagowa Khaleed yayi yana kallon Abokin nashi,wa'annan Segxy Eyes din tuni suka kara kankancewa,idon shi kuwa ya kad'a daga fari zuwa jah,da ka ganshi zaka fahimci yana cikin damuwa na kurewa.
Da kyar kuma ya iyah motsa labbansa ta hanyar cewa" Abdoul Manan ya zanyi Suhaimart ta So ni!!.
Itace komai na ya zanyi Wlh bazan iya rasata a Rayuwa ta ba".
```

Suhaimart ita ce komai na,plz Abdoul Manan ya zanyi ta soni,wlh Son ta nakeyi Auren ta Zanyi,ta haifamun y'ay'a masu kyau irin nata,tare da kyaun Halin ta....I can't do any thing without her Abdoul.
duk maganan nan da yake sam yin su yake baima sanin Abun da la66ansa ke futarwa".

Abdoul Manan ne ya kuma dafo shi yana furta Hee Guy ka fahimta,Haba Khaleed kaman bakai da nasani ba"? Inaso na sanarma ka Suhaimart baxata ta6a kinka ba,Kawai ka fahimta tsakanin ka da ita akwai tazara ne mai tsayi,wanda abu ne mawiya ci Suhaimart ta amince da soyayyar ka,don zatayi tunanin ita fah ba yar kowa bace,kuma zata ga ita bakomai ba ne akan ka".

Ehhhh Abdoul Manan Amma yakamata ta soni,ina mata Reall luv,wlh ina son ta Abdoul, ta soni,inda zata saurare ni ae da tayi tunanin True love never End!!!.

Niko Suhaimart da nake a rakube jikin wani Coridour don na kasa fita a halin da nake ciki,kar na hadu da wani afara sakamun alamon tambaya,shiyasa na dawo da baya na Rakube daga gyefe wanda sam kowaye baxai fahimci da mutum a wirin ba".
Kuka na kara sakawa sakamakon yanda naji Gaba Daya Sir Khaleed ya sauya,tabbbas koba afadamun ba a yanxu ni kaina zan gasgata ba wasa ne Sir Khaleed yakeyi ba,soyayya ta kaman yanda yace tana neman Fitar da hankalin sa,sam zai iyah bayya na ta a gaban koma waye!.
Tuni tausayin kaina ya gama kamani,ga kuma tausayin Khaleed don a daya barayin na zuciya ta ina zullumi da fargaban ranar da Hjy Zaituna xata samu wannnan labari".
Don sam baxata amince dani Suhaimart a matsayin suruka ba.
Cikin sauri na mike hadi da nufan barayin mu don naji shiru babu alamar da akwai wani daga wajen...
Barayin mu na nufa direct,wanda da isana na fada gadon mu ina mai cigaba da Rushewa da kuka mai cin raina da ban tausayi...

A sarari nake furta Hohohi ni yo ya zanyi,maiyasa Khaleed ka bari zuciyan ka ta kamu da sona? Ba kasan wacece ni ba,ba kasan Asalina ba...shin xaka iyah zama dani idan har kaji labari na kuwa,kajiyo asalina...!!! kara rushewa da wani irib kuka nayi,wanda rabon da nayi shi har na manta a duniya.

Oummu Sulym wai wannan wani irin zama ne kikeyi sam kinki motsawa bayan kin san yanxun zaki tafi Aikatau din nan naki".
Hmm nisawa Oummu Sulaym tayi,kan tayi duba ga Mama da tayi nisa wajen saka D'an waken sayarwa mutane kuwa har sun fara rufa mata. Hmm tom Mama bari na mike wlh banjin dad'in jikina ne".
Oummu Sulym ce mai wannan maganan tana mai mikewa daga kan kujeran tuka tuwo ( Stool ).
Kallon ta Mama tayi kana daga bisani tace Oummu wani abun ne ke damunki? Ko dai wani abu ya samu Suhaimart ne!!?.

A'a Mama bari na shirrrr....

Keee...." keeee Oummu uban wa kike jira ya wanke maki wa'ancan kayan eyeee..Ko kina nufin ni ce da y'ay'a na zamu yi wanke$^{2}$ n gidannan?. ke kuma kina can kina aikin Gantali da watsewa,kina fake ma mutane da Aikatau,waye bai san halinki ba,ko aka ce maki komun fakewa da aikatau din da kikeyi ba'asan tsinewan da kikeyi bane? tom ki sani Wlh ko Ubanki ya shigo gidannan baxan barki ki fice ba sai kinyi wanke$^{2}$.

Kallon Mama Oummu Sulaym tayi yayin da cike da rashin nunawa ko ajikin ta duk da maganganun Inna Atine yy mata Zafi matuka. Amma sanin halin mutum sai ta daure ta saki mata murmushi kana daga bisani tace" Inna Atine don Allah kiyi hakuri Wlh na makaran isah wajen aikin nan,kuma naga gasu Innah Wuri nan ki saka ta ta wanke".
Fadin haka da Sulaym tayi yasaka Inna Atine cike da munafunci ta hau kururuwa kaman wanda Oummu tasa hannu ta bugeta,na shiga Uku na malam".

malam..." yau ni zan saka Sulaymu Aiki taki mun,tana kwada zancen ga y'ay'ana nan nasa su ita ban haife ta ba?...ta fadi tana bankada labulayen dakin Baba Amadu.

Cikin sauri cike da Rawar jiki ya fito wanda daka ganshi kasan asallame yake tabbas an gama da shi.bai da tacewa a cikin gidan nashi,gashi daka ganshi kaga malamin Zaure...

Uwa ta". maxa wanke mata kwanukan sannan ki tafi kinji?".

Baba ne ma fada ma Oummu Sulaym wannan maganan cike da rawar jiki da tsron Inna Atine.

"Tom Baba". Oummu ce ta fadi hadi da nufan can karshen gidan don ta fara wanke$^{2}$ kaman yanda Baba Ahmadu ya bata Umarni".

Itako Mama Baiwar Allah,kallon inda suke sam batayi balle tayi nuni da Ranta ya sosu a saka makon cin mutuncin da Inna Atine tayi mata da diyar ta ta".
Baba kam kasa komawa daki yy sai saka takalmi da yy ya fice wajen gidan nasa,don sam idan Inna Atine ta tada fitina baya iyah zaman gidan,Itako Diyar Inna Atine wato Inna Wuri tuni ta fito tana aikin Girgixa kaman mai shurin yin dambe.

Itako dai Sulaym ra6ata tayi ta wuce ta gyefen ta kallon ta batayi ba.

Sosai Oummu Sulaym tafara wanke$^{2}$n don aiwatar da abun da Baba ya sata. Amma Inna Atine kuwa sam duk da hakan bata daina hargogowa tana zage$^{2}$ ba".

Wata ce da'ake kira da Ramatu makobciyar su da ta shigo sayan d'an wake wanda komai akan idon ta akeyi tace" Haba Atine wannnan fitina da mai yy kama,ki zagi y'a,kin kuma zagi Uwar ta". naga kina da iko da Sulaymu amma baki da iko da Mama Laure,tunda a girme ta girme maki,keba sa'anta bane.gsky gidan nan naku da gyara wlh ku gyara,ki banxa yaya matane da ku,maiye amfanin kullum sai anji Harshenki a makota.... Haba zafa kuso mazan kwarai suxo

gurun yayan ku bana banza ba".

Inna Atine shiru tayi don sarai tasan wacece Ramatu da fitinan ta,sam bata da Ragayyah shiyasa ta kasa tsagalgale mata kaman yanda take mawa wasu.

Buden Bakin Inna Atine cewa tayi,a'a ai ni y'ata mazan kwarai ke zuwa wurin ta,kuma a haka har na Aurar da Zainabu,yanxu ma Inna Wuri bazata shekare mun ba da yardan Allah,wanda suka zo zama dai su zauna,babu ko mashin shine saboda bakin jini,wlh anyi asara". Mutum shekara Ashirin kenan bana,amma bb karen dake sallama,tir da wannan bakin jini,mu dai mun gode mawa...!!! Gsky kin bani kunyah Atine, sam ban tunanin jin haka daga gareki ba,amma kisani shi Aure lokaci ne,idan lokacin tayi yi wlh babu mai hanata,ai shi ba'a gori da Aure".

Niko ina wanke² ne amma bansan lokacin da Hawaye yafara mun sintiri a fuska na ba....Tuno da maganar Mama da take fadamun komai lokaci ne kuma bayan Wuya sai Dad'i. A raina kam a yo cewa nayi yaushe ne komai zai karemun A rayuwa? tun banfi shekara 11 ba nake fuskan ta kalubalen Rayuwa? haka dai Sulaym tayi ta zancen zuci,a ranta tana tabbas ita ta d'an dadani Mad'aci,amma har Ilah yau bata samu zumar ba".

Ramatu kam ci gaba da cewa tayi kuma da kike wani mgn,waye bai san Abun da Zainabun tayi ba,da'aka samu da kyar aka kaka mata a Kauyen Fallanki ko?.
Tana fadin haka tajah tsaki hadi da ficewa daga gidan tana mai mitan idan kowa zai gori ai ke bai kamata aji bakin ki ba Atine ".

Mama dai babu uhumm bare uhum'ummm....A haka Sulaym ta kammala aikin ta tanayi tana kallon Mama ta gyefen ido ko zataga wani sauyi a tare da ita amma sam bata ga komai ba. illah sana'ar ta da takeyi abun ta".
Hakan ko bakaramub kular da Inna Atine tayi ba,don tun maganan da Ramatu ta fadi tajah da baya jiki babu kwari ta koma dakin ta...

Itako Oummu Sulaym nufan dakin Mama tayi don ta shirya ta tafi wajen Aikatau din ta". Don a yanxu lokaci sosai ya kure wuraren 11: 30am.

Da shigan ta D'akin Mama laure ta hau bin garun dakin dako plasta babu dabe ne kawai...
Bin ko ina ta hauyi da kallo,kwallah na kara ciko idon ta,duk da wannan halin da muke ciki,ace kwanciyar hankali ma babu. Habawa Inna Atine wlh dani kikeyi,dadin abun kin sanni sarai. Arzikin ki Mama da Baba duka suna nan ne,amma in basa gidan ai bakya mun don kinsan Wlh dai² nake dake".

A haka ta dinga shurin ta ta hanyar saka uniform din Aikatau din tana mai gaggawan fitowa...

Suna a zaune tsawon A wanni Khaleed kam ya tasa abun da ya saba sha wato giyan sa yana daddaka ma cikin sa,sunan Suhaimart ne kadai yake nana tawa. Yayin da Yarima Abdoul

Manan kuwa gaba daya hankalin sa ya idah tashi,don bai san wannan wani irin mahaukacin so ne Khaleed kemawa Suhaimart ba". ita ba wani Abu daxaice tana dashi ba,a yanxu fah auren Kwarya tabi kwarya akeyi,babu mai jawo ma kansa talauci,don cewa ma suke talaka gayyar tsiya!!!. Amma shi duk akan wannan Yarinya karama ya gama daga hankalin shi,a tarihin rayuwan shi bai taba ganin Khaleed yayi soyayya da yarinya ba. don shi sam bai kallon macen da bata haura 25 ba,acewan shi sun gi hankali bai son sakarcin yarinya ta,Amma a yau gashi Yarinyan da batafi 17/18 ba tana neman burkita sa gaba ki daya".

Duk wannan Sumbatun da yakeyi akan idon Oummu Sulaym da shigowan ta kenan barayin tana neman Aminiyan ta,don damuwan ta kanta ya ishe ta".

Amma kuma ganin Halin Da Sir Khaleed ke ciki bakaramun firgita ta yayi ba,Abdoul Manan kam Rarrashin sa yake akan zai nemo masa soyayyar wannan Yarinya,amma har a wannan lokaci yaki kwantar da hankalin sa".

Ganin haka cike dajin haushi don  tuni Oummu Sulaym ta gama fahimtan komai,nufan barayin su tayi saurin yi,wanda da isan ta dan madaidaicin dakinsu ta cidda Suhaimart kwance tana sharar baccin ta".

Nufo ta tayi cike da jin zafi ta daga hannu hadi da nana mata duka a baya!.

Gigif na mike ina mai kara bude idona don ganin wanda ya dada mun duka haka,ita dince dai nagani Wato Aminiya ta Sulaym.

Saurin mikewa nayi ina mai zaro dakwa² n idona da furta Sulaym mai nayi maki haka?.

Cike da masifan ta tafara cemun,ehhh dole ki tambayen mai kkyi mun!!?,bayan kin bar bawan Allah gayican kin zauta shi bai san duniyar ma da yake ciki ba".

Dajin haka nayi saurin mikewa daga zaune ina mai kara zaro ido,don na tsorata da Maganan Oummu Sulaym. Kwallah ne  nan danan ya ciko mun ido.

Itako Oummu Sulaym cigaba tayi da cemun" Wlh Suhaimart kiji tsoron Allah,kar Allah yabaki dama ki masa Butulci,Suhaimart ki kaunaci mai Kaunanci,ki kuma so mai son ki tun kan dama ta wuce maki".
Suhaimart ni kaina na isheki ishara ,gani nan babu saurayi tsayayye sai yan iskahhh....tana fadi n haka sai kawai ta Rushemun da kuka mai taba rai da kuma ban tausayi,wanda ni kaina bansan lokaci n dana fara yin nawa kukan ba".

Ina kuka ne gami da cewa" Oummu Sulaym na tuba ki daina kuka wlh bansan naga damuwar ki,ki fadamun mai kkso ni kuma zan maki".

Ai dajin haka Oummu Sulaym tayi saurin saka hannu tana goge kwallahn kan fuskan ta tana

mai nufo ni hadi da cewa" Yowah Aminiya ta,kawai ki Amince da soyayyar Sir Khaleed, komai yace maki kar ki masa jayayya,kisa a ranki Sir Khaleed mijin ki ne mah".

Dariya ne ya kuncemun Wai Sir Khaleed miju na,ko tayaya hakan zaiyi wuuu ohoooo.
Tom Sulaym nayi maki Alkawarin baxan kuma masa musu ba..."

Yauwa yar gari yanxu maza ta shi kinga yau bai fita ba kuma kene da masa hidiman komai. tom nace mata sannan na mike hadi da kama hannun ta ina furta tom ae kinsan aikin side din shi banawa ne kadai,har dake ko!!.

Dariya duka muka saka kan daga bisani mu tashi duka muka nufa barayin nasa".

Muna cikin tafiya ne sai naji cike da tsorata da mamaki Oummu Sulaym ta Furta Iftihal..."

Zuciya nane ta buga lokaci guda kawai jin sunan Iftyhal da Oummu Sulaym ta furta". Juyawa nayi inda naga ma'aikatan gidan kowa hankalin sa na kai".

Wato matashiya ce wanda ashekaru baxata haura 22 ba a duniya". Sanye take cikin shigarta na Golden Abaya da akayi masa adon stone daddabe....Rolling tayi da yar mayafin ta yyn da Hannun ta kedauke da wata yar ficiciyar jaka".
Kafan ta kuwa sanye cikin Half cover mai tsinin gaske....
Fuskan ta kam a daure yake tamau,wanda basai anfada maka ba daka ganta zaka fahimci ita din bata da mutunci sam.

Bin fuskan ta nayi da kallo wanda yake sanye cikin Makeup kaman wanda zata tafi taron fitar da kyawawan Duniya. A takaice dai Iftyhal irin matan nan ne masu fama da hayakin kai,marasa mutunci wanda kowa ya gifta tsakanin su sai sun keta masa rashin mutunci.

Saurin jan Hannu na Oummu Sulaym tayi mukayi baya,yayin da aha cike da takon takama take takawa ma'aikata kuwa cike da Rawar jiki ake gaysar da itah,haka nan mu ma da tazo ra6awa ta gyefen mu,don duk hada baki mukayi muka gaisar da ita,amma sam bamu samu arzikin Ko kallon kirki ba,balle kuma Amsawa".

Barayin Sir Khaleed ta nufa,yayin da gaba daya zuciyan ta tagama karaya da son Ganin Habibyn nata.
Kutsa kai tayi tun daga farkon Falon nasa haka ta dinga raba ma'aikatan cike jin kyankyanin su a dole ga Talaka kar su shafa mata talauci,don suma haka suke gaisar da ita ko kallon su batayi ba".

A haka ta isah midle Falour n da har a Lokaci n Khaleed da Abdoul Manan na zaune,duk da a wannan karon babu kayan shaye$^2$ n nasa don Abdoul Manan da karfin tsiya ya kwashe su daga gaban sa".

Ganin handsome din nata xaune ga wani kyau da yakara mata kwarjinin sa yakuma cika mata ido".
Da gudu ta nufe shi hadi da Rungume shi tana furta Hyyyy my Dierling". Na dawo gareka my Husby ya ka ganni". ta fadi maganan tana daga masa gira fuskan ta dauke da Murmushin nuna farin ciki".

Mudai tsayawa mukayi saroro muna kallon ikon Allah,bani ba ba kuma Sulaym ba".

Kissing din shi tayi saman kumatun sa,wanda hakan yasa shi tsaiii da idon shi a kaina,nikam dukar da kai na k'asa nayi ina mai wasa da y'an yatsuna.ganin haka yasa shi matsar da Iftyhal daga jikin sa,yana mai Furta Iftyhal Bana jin dad'in jiki na". yanda yayi maganar yasa ta kara shige masa tana tallabosa dacewa" AYahhh My dierling mai ke damunka,ko missing dina ne dakayi,sorryyy hear!!?.
Kauda kai gyefe yayi don Iftyhal tana neman ya Sauke fushin sa kanta ne.
Itako sam bata ankare ba,mikewa tayi tana mai bin falon da kallon don kakaro wani laifin ma'aikatan gidan..." My kaga shiyasa bana son zaman Nigeria,kawai mukoma Abroad da zama,nidama don kai na dawo".
tana maganan ne hadi da nufan dirning Area,don a tunanin ta ankammala mawa Khaleed din nata lunching nashi.

Ganin tun kayan breakfast da akayi serving koci ma baiyi,amma ba'a kawar ba yasata cike tsawa tace" Waye ke da duty a Yau?.

Duka ma"aikatan ne idon su ya dawo kaina, wanda cike da sanyi da natsuwa na karaka gaban Dirninig din ina furta nice".
Daga hannu tayi hadi da sakarmun wawan Mari da sai da yasa naga taurari biyu". Tuni hawaye ya fara bin kunci na,cike da masifa da fitina ta fara nuna ni da yatsa tana furta ,ubanki ne kija barmawa Wannan Abincin Eyyyeeee".

Muryan Hjy Zaituna naji daga baya na tana fadin da kyau my Iftyhal".

Shiko Huday da shigo wanshi kenan kuma komai akan idon shi akayi,tuni bai san lokacin da ya nufo iftyhal yana mai daga hannu zai sharara mata mari ba,Amma ina tuni Abdoul Manan ya rike masa hannun,Saukar mari naji an dauke Iftyhal da shi wanda da sauri na juyo ganin wanda ya dauke ta da wannan mari haka ma mu duka,don Sir Khaleed tuni idon shi ya chanja kala,tabbas badon kawaycin da yy ma Huday ba,da tuni yayi maganin Iftyhal don zuciyane dashi kaman mutuwa".

Niko jin ansauke ma Iftyhal mari yasani kara zaro ido cike da tsoro don ganin wacce tayi wannnan Aiki???....

*TOM FAHHH K'ARAK'AK'A,FREE FAGE NA GAB DA KAREWA FAH.DOMUN A PAGE 15 ZAIYI ENDING.* *MAZA KI HANZARTA WAJEN BIYAN #200 KACAL WATO IDAN VIP NE*

*IDAN KUMA NOMAL KK SO NE #200*

*IDAM KE ME RA'AYIN SPC GRP NE ZAKI TURO 300 CIKIN SAUKIN FARASHI*

*ZAKI TURO KATIN TA WANNAN MTN NUMBER 👇🏻*
*09137392680*

*SANNAN SAI KIYI MAGANA TA WANNAN WHATUP NUMBER 👇🏻*
*08081202932.*

*HAJIYA KADA KISAKE LABARIN NAN TA WUCE BAKI💃*

Akafta🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️.

*Taku har kullum Aysha moh'd* *(Maman teddy🧸)*
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Episode 14*

*____________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*______________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*

_Dedicated to my teddy🧸Wannan pagen taki ce y'a d'aya tilo😂._

_*Plz don't miss dis novel,the latest  Hausa nvl in 2021.*_
_*Do not miss this Novel Hajiya ta,idan baki karanta ba an barki a baya Hajjaju....💃*_

*________________________________*

Niko Suhaimart kara dakwako ido nayi waje,ina bin wannan baiwar Allah da kallo,wanda take sanye da wata Bak'ar jallabiyya,tayi rolling gami da mayafin shi wato baki,fara ce mai matsakaicin jiki...kafan ta kuwa sanye cikin irin wa'innan manya² Combus masu girman gske farare kal....Haka jakar hannun ta fari yake. da kaganta zaka fahimci ta yaga mawa Iftyhal tijara da Rashin mutunci haka akomai mah,don wannan wayayyar Gske ne,har tunani na fara anyah A nigeria take kuwa,a tunina kila dai Balarabiyya ce ba anan take ba,tom abun ka ga kyau na mutan Gombe.
Tana marin Iftyhal taja ta tsaya,yyn da cikin Rawar jiki Mom Zaituna tace" Aysha ya haka Iftyhal ce fah".
Kan ta bata amsa Huday ne yace" Mom hakan shi ya dace,don ni kaina da badon rikenin da Abdoul manan yayi ma wlh sai na mata wanda yafi wannan".
Ae kafin yagama Rufe baki ne Iftyhal tace" Kam bala'i nice zaki mara Aysha??? Ke wacece kuma yar gidan Uban waye...???

Murmusawa Aysha tayi tana mai kuma matsowa dab da Iftyhal kana tace da itah" Nice Aysha kuma Y'a ga Sanate Ibrahim dutse... And You?"
Ta tambaye ta cike da rainin hankali da wayo".

Ae ko nan takuma fusata Iftyhal wanda cike da bala'i ta fara cewa" Hee Stupid will u keep up your mouth,wlh sai na tajaraki Aysha,baxan barki ba sai na kuma wulakantaki".
nan ta juya ga Huday tana mai kallon Abdoul Manan da cewa" Ayyah ae da kasani baka rikesa
```

ba ya mareni indai shi din ya cika mutum,kuma wlh sai na fad'ama Daddy". Ta fadi tana mai share Hawayen takaici da Bakinci,akan yar aiki baiwa tattaka ne za'aci mata mutunci haka,nan take ta fara tunanin yanda zata karar da kowa na dangin wannan yarinya wato Suhamart,tabbas bazata barsu,sai ta daddana mata bakin ciki har abada kuma har karshen Rayuwar ta,sai ta gwada mata banbancin talaka da mai kudi da tazara kaman sama da k'asa".

Niko Suhaimart ban da zubar Hawaye babu abun da nakeyi,ni yau Allah ya gamani da fitina,ya zanyi yau,abun da nake cewa kenan a zuciyata kuka kam yin shi nake,don sai a yanxu na fahimci Iftyhal k'anwa ce ga Huday".

Hjy Zaituna ne tayi saurin Matsowa kusa da Iftyhal tana Rungumota hadi da shere mata hawaye tana mai furta,sorry my baby,kiyi hakuri wlh a yau wannan yarinyan zata bar gidan nan...Sosai Iftyhal taji dadin Maganan Hjy Zaituna don haka sai takara lafewa jikin ta".

Itako Hjy Zaituna sai dagowa tayi tana mun kallon Wulakanci da kaskanci, cike da tsatsan tsana ta ta furta,ke kina yar matsiya ta ne zaki saka a mari sirikata!!?
Tom daga yau na sallameki daga aikin gidana,karki kara dawomun gayyar jaraba".

Kasa cewa komai nayi sai hawaye dakebin kunci na,yyn da Aysha cikin Saurin ta bude baki da zummar yin mgn,sai dai duka muka tsinkayi muryan Sir Khaleed yana mgn cike da issah da mulki da cewa" Mom babu inda zataje,Saboda ina son Ta,kuma ni ita ce zan Aurah".

Difffff kikaji wurin,nikam da nake kuka ban san lokacin da kukan ya dauke ba,nan na zaro ido,waje a raina ina shikenan nashiga Uku,yau Khaleed yajaxa mun futina".

ma'aikatan kuwa da su Mhisa Caterine Ae gumi ne ya hau karyomasu,suna mai cewa shikenan yau ni naga banu,ae wlh na shiga uku,kowa a birnin Zuciyan sa kuwa Tausayamub yake...

Muryan Hjy Zaituna naji tana cewa" Khaleed!!! mai kunnuwa na kejinmun takakan naka kkso??? yar aikin ka!!!???. This is impossible".

Ae dajin haka nan da sauri da kuka na bar falon ina mai cigaba da zubar da Hawaye.
Itako Hjy Zaituna cigaba tayi da cewa" Khaleed ka mankan ce ne???.
Cike da jin zafin ta saka masa Suhaimart din sa Kuka yace" Plz mom Allow me to Rest,I lov Suhaimart, and i Really Luv her,babu wanda zai dajatar dani".
Muryan Aysha cike da tsiwan ta ne sukaji tana cewa" Dakyu yah Khaleed, Wannan haka yake Ita yar talaka ba mutum bace,ae shi so babu Ruwan sa da wani duba arziki ko Rashin sa,so a zuciya yake Ahaaa!!!.
Ta fadi tana cike da Tsiwa,kunsan dai Aysha".
Bude baki mom Zaituna tayi,sai Abdoul Manan yace" Nana Aysha maiyasa kk zo Zaria? Waye yace kizo???.

Zaro ido tayi waje kawai sai tasaka kukan sargancin y'ay'an Hutu,tana furta ae dama nasan

bakasona a wuri,duka bakuyi farin cikin Ganina ba,don haka Yau zan koma,Allah yakaramun da nazo...Ku kwantar da hanklin ku yanxu ma zan tafi hankalin ka ya kwanta Yah Abdoul.
Tana fadin haka ta juya hadi da fucewa daga Dakin fuuu.....cike da fushi,wanda ganin haka yasa Hjy Zaituna cewa" Abdoul Manan don Allah jeka taro ta kar ta tafi,kasan Aysha da saurin fushi".
Aiko da Sauri ya fita Don bin bayan ta,amma ina kan ya isah farfajiyan gidan tuni Anbude mata Gate ta bar cikin gidan cike da wani Irin mahaukacin gudu".

Shikam cikin Sauri ya juya hadi da shiga moton shi yana mai kokarin bin bayan ta".

Niko tafy kam kawai nakeyi nakasa sanin inda nake dosa,tafy nake kaman wata zautacciyah.

Moto ce naga tasha gabana,wanda kan na karaso ne tafito tana mai Kallona da furta mun Suhaimart!".
kasa cewa komai nayi kawai sai nasaka kuka,nan cikin sauri Ta rungumeni tana mai Furta plz Sorry...sorry..." Ki kwantar da Hankalin ki,mu tafi gida yanxun dai kawai". Nan tajah hannu na tana mai saka ni A moton nata,yyn da tayi saurin zagayowa gami da jan moton nata.

Tunda muka shiga moton banda kuka babu abun da dana keyi,itako Aysha gaba daya hanklin ta a tashe yake,sai Rrarrashi na takeyi, Ahaka dai har muka isa gidan mu".
Da fitowan mu daga moton ne tace Suhaimart muje na gaida Mama ko?.
tom nace da itah yyn da muka kutsa kai izuwa gidan namu.

Tun daga wajen gidan mu Aysha ki bina da kallon Tausayi wanda koda muka shiga tsakar gidan mu sam na kasayin Sallama saboda murya ta da ta dasashe bata fita sam,saboda tsaban kukan dana sha. Aysha ne ta Furta Assalamu Alykum..."
yyn da cikin sauri Oumma na dake sharar tsakar gida ta dago Hadi da amsa mana sallaman". Tana mai kuma bina da kallo hadi da son fahimtan wani Abu dan gane dani,koba'a fad'a mata ba tasan nayi kuka,kukan ma bana wasa ba,don gaba d'aya fuska ta tajeme, manyan idanuwa na kuwa sun kada sunyi jajir dasu. Da kyar Oumma ta iyah Furta Sannun ku da zuwa,Suhaimart badai har antashi Aikin ba,naga lokacin baiyi ba".
Ta fadi tana mai tsaida idon ta akaina,don jin amsan da zan bata,amma kuma sai nayi mata shiru Hawaye na kara bin fuska ta. da kyar na iya cewa" Oumma na An sallame ni ne".
Shuru tayi na wasu dakiku kan daga bisani tace" Tom Suhaimart wannan shine Abun damuwa? Share Hawayen ki kinji,Allah baxai Wofuntar damu ba". Maxa kai bakuwa Daki ki shimfida mata Tabarma,mun barta tsaye".
Ta fadi tana kallon Aysha da Tausayin mu ya gama cika ta".

Juyawa nayi hadi da cema Aysha bismillah mushiga daga ciki".

Murmushi tayi mun kan daga bisani ta biyo bayana. a daki kam na shimfida mata wata yagalgalalliyar tabarma,wanda cike da sakin jiki ta zauna".
Zama nayi ina mai daukan wani Kwanan sha ina mai debo mata ruwa na ajiye a gaban ta kan

daga bisani na zauna".
Kallona tayi cike da murmushi tace" Suhaimart kenan tom ngd. Hmmm Suhaimart don Allah kar ki dau wannan abun da ya faru dake a matsayin wani Abu babba,kuma sannan da kk mgnan an koreki,ae Yah Khaleed yace babu inda zakije,don haka gobe ki saka kayan ki ki taho wajen aiki.

Sannan hargagin da kikaga Iftyhal nayi ba wai don wani abu bane kwai dai Saboda tana Son Yah Khaleed ne. Kuma shi Baya son ta,cox ita ba choice din sa bace,ba type nashi bace,sam bama ya son mace irin ta". Don Haka Plz ki kwantar da Hankalin ki,wlh bayan Wuya sai dadi,kuma dama indai Ana soyyayah da Alkhairy cikin sa,sai anyi pacing irin wannan problems din,amma mai sai kunyi hakuri ga ba dayan ku,ku dan ka komai With time,komai mai wucewa ne Okay".

Ta karke maganan tana daga mun kai,nan nayi murmushi hadi da cewa tom ngd Aysha". Murmushi itama tayi mun kan tace ni ban gane Hakan ba,kice mun kin amince zaki cigaba da Soyayya da Yah Khaleed, wannan abu baxai taba sakaki ki chanja ra'ayi ba,don haka fada mun kinmun Alkawari zaki cigaba da Soyayya da Shi din"?

Shiru nayi ina Murmushi araina ina mai cewa" Oh ita A tunanin ta Wai ma muna zuba Soyayya kenan,Hmmm daga mata kai nayi Alamar na Amince,aiko nan ta hau Dariya tana mai Rungumoni don Murna,a ranta tana kisima dama ae Iftyhal bata fara ganin komai a Rayuwar taba,tunda bazata natsuba,tabbas yanxu ne Khaleed ya cancanci Aure,ba ada ba".

Sallaman Oum Rabi yasa mu duka mai da hankalin mu kanta hadi da amsawa gareta.

Zama tayi yyn da nan Aysha cike da girmamawa da dattako ta fara gaisar da Oumma,wanda hakan sosai yy ma Oumma dadi arai".Shiyasa cike da Harka ta amshe ta,don kunsan Oumman nawa talaka ce amma akwai isah da fadin rai...

Bayan sun gaisa ne ta mike hadi da mana Sallama,haka mukayi mata asauka Ify,sannan tayi waje".

A zauren gudan namu ne zata fice dai² Hamma Zaid na shigowa,bin ta da kallon banza yayi kaman dan wani da wani,a cewan shi taga Butter,din shi gani yake yafi kowa ni da namiji kyau".Musaman yanda yan matan layin mu ke yin shi".

Itako tsayawa tayi har ya wuce,addu'a kawai bakin ta keyi,A ranta tana fadin yah Haka??? ina tabbas wannan ba ido na bane,Ban taba ganin mutum mai kama da Yaya Abdoul Manan kaman wannan ba,kaman is tooo much,ta fadi tana fitowa daga soron.

Shi kuwa Abdoul Manan da dama Ya biyo bayan su kuma yaga inda tazo shiyasa ya tsaya jiran ta,tana futowa yace Kee Iyayen yan shishshigi zonan mu wuce".

Sai a sannan ta ganshi cikin dan daure fuska tace" Ni katafi,mai zaka mun tunda bakaso gani

na ba.
Habawa Autan Ammie ni na isa nace banso ganin ki ba,amma kksani ko Gombe zan mayar dake yau din nan. yafadi yana murmushin ba'a.

itako sai ta zaro ido tana furta Gombe kuna". Ehhh mana can zan kai ki". Dariya duka m sukasa wanda a ranta tana mmkin dama Hamma Abdoul Manan ya iyah ba'a. yau ina hantarar da yasaba mata duk babu. don hakane cikin sauri tace" Hamma Abdoul Manan Kaga mai kama da kai kuwa yanxun ya gifta".

Wah haba yarinya idon ki ne Allah,ko kinga Aljani da wannan ranar".

Aljani kuma? Tace dashi tana dan turo baki. ehhh mana muje Mom na can duk ta damu da Rashin ki'. Tom yaya moton nawa fah ae dole ni zan tukata ko?.
Okay tom muje don inason inkin huta nayi mgn dake dangani ga Suhaimart ".
Tom Hamma Abdoul.

Haka ta shiga moton nata wanda sai da tafara gaba sannan ya biyo bayan ta".

Bangare na da Oumma na kuwa da fitan Aysha ne Oumma tafara tambayana mai yafaru.wanda nan na fada mata komai da ya wakana a gidan,da yanda Sir Khaleed yace yana sona,don duk shine musabbabin fitinan.

Wani dogon tsaki Oumma taja,kan tace" Tom mai zata iyah mana eye,ta je tayi iko da d'an ta ne bakye ba,ai ba ita ta haifan mun ke ba,Suhaimart ki sani ke amana ce a gareni,kuma Wlh baxan bari a cutar mun dake ba,kuma sannan bance ki Wulakan ta Khaleed ba,amma kisani ko mahaifiyar sa bata fito da wannan Abu ba,ke da Khaleed da Akwai banbanci,ya fiki kaman sama da kasa. Amma bance ki Wulakanta shi ba,don mai kaunar ka ka kanauce shi ko yaya yake,Amma kififita Addu'a fiye da komai a yanxu".

Tom Oumma na nafadi cike da Karaya.Maza tashi kije kiyi Alwala ki dawo kici Abincin ki,da tom na bita sannan na mike hadi da ficewa daga Dakin namu.

Tunda su Aysha da Yarima Abdoul Manan suka isah gidan Hjy Zaituna bata kuma komawa barayin Khaleed ba,don side din Hjy Zaituna ta nufah shi kuma Abdoul Manan ya wuce side din Aminin nashi,Haka ta shiga izuwa babban falon ta,ma'aikata sai aikin su suke,da ganin ta kowa ya hau gausheta,nan ta hau Amsa su cike da mutuntawa,da isan ta taga wayam ba Hjy Zaituna anan, zuciyar ta ne ta Raya mata,tana can barayin Khaleed don tasan yau baxasuyi baccin Dadi ba.

Dan karamun tsaki tajah,kan daga bisani ta tattara kayan ta ta nufi Dakin ta danata ne wanda duk in tazo gidan take sauka a ciki,tana Riyawa ae Dad ya kusa dawowa wlh shi bazai ta kuramu ba".

Ialai kuwa maganar Aysha dutse don Hjy Zaituna takoma kamar zararriya,don tunda Iftyhal taji magnar cike da dacin rai ta bar side din nashi hadi da barin gidan gabaki daya,babu kirar da Hjy Zaituna batayi mata ba,amma tayi mata banza don ko waiwayo ta batayi ba". Tuni yan aikin kowa ta ware don kar fushin wani yashafi wani".
Ai ko nan Hjy Zaituna ta fara cewa" Khaleed baka hayyacin ka ne mai zakayi da Wannan yarinyan talakan ka...cikin sauri ya katse ta da Mom ita ni dai nakeso...

Tsayawa tayi sororo na tsawon Mintina don sam tarasa ta ina zata fara controlling din yaron nata,gashi ita tunda take dashi bata ta6a tsawata masa ba,balle kuma wai har tayi masa fada,rasa abunyi yasa ta matsawa gare shi tana furta Okay son,ka kwantar da Hankalin ka kaji"?

Kallon ta yayi sannan yace Kin amince mun da Suhaimart a matsayin mata na?.
Da kyar ta iyah hadiye wani abu kan daga bisani ta daga masa kai,alamar Ehhh".

Rungume Mom din nasa yy yana kissing din kumatun tana dariyan dole,don a ranta tasha Alkawarin 6atar da Suhaimart da Ahalin ta.

Shiko Huday ganin komai yake a tafin Hannun sa,duk wani bariki na Hjy Zaituna kallon ta yake,kuma shi ya Iashi takobin ganin babu wani abu da zai samu Suhaimart, yana ganin ta tamkar jinin sa ce". Murmushi kawai yake bin su dashi irin na bakaken Miskilan nan....

Aha Hjy Zaituna ta mike daga zaunen tana mai furta Bari na hada maku Lunching don yau babu inda zani ina tare da yara na". Dariya suka saka suna fadin Mom da ko minji dadi,don munyi missing din girkin ki, Kallon su takuma ta na fadin Aiko yau Mom zata yi maku wanda sai kunyi santi fah,don nasan fevorate din kowa,tafadi tana mai ficewa daga falon,sukuma suna dariya".

Shi kam Khaleed dora kansa yayi a saman kujera ya rasa abunyi,anyah yau zai iyah Hakuri baiga Suhaimart ba,Ina sam,tuno da Marin da Iftyhal tayi mata,da kuma irin cin mutuncin da Mom nashi tayi mata Again yasa shi rintse ido, kanshi na sara masa".
Huday ne ya kalle shi hadi da cewa" Plz Khaleed ka kwantar da Hankalin ka,in shaallh Suhaimart Takace,kuma wannan Abun basan bazata juya maka baya ba".

Kallon Huday yy kan daga bisani yace" Huday Suhaimart bata bani amsan tayin Soyayya r danayi mata ba,indai na rasa Suhaimart tom tamkar na rasa Rayuwa ta ne gaba ki daya. ni bansan ya zanyi ta soni ba,gashi yanxu Mom ta fadata mun komai ya zanyi"?.

Dariya Abdoul Manan ya sheke dashi yanayi yana karawa,wanda da kyar ya tsagaita sannan yace" Khaleed anyah ba hakkin yan matan daka saba yaudara bane zai kama ka,don yau na hadu da Zeebu itafa har yanxu tana kan bakanta". sai ya kuma kwashe dariya".

Kallon sa Khaleed yayi cike da takaici da ya Auri zeebu ai gomma ya karke rayuwar sa babu Aure,cike dajin Haushin dariyan da Khaleed ke masa yace" Stop Abdoul,bana so".

Saurin sada kai kasa Abdoul Manan yayi yana fadin tuba nake ranka shi dade,amma kyakykywan Albushir Suhaimart fah ita ta amince da Soyayya r ka tuni,don ita sam bata da zabi,kuma babu tangarda Mr. man, in wani Abu ya biyo Baya tom daga kau ne".

Cikin sauri Khaleed yace Plz Abdoul Stop Playing,da gske ta amince mun. Murmushi Abdoul Manan yayi sannan yace" Tun isowan ta nan da Amin cewa ta zo,sannan kuma kaje ka tambayi Aysha ita nasan bazaka aza wasa zata fada maka kaman ni ba,tunda ita da bakin ta sunyi mgn da Suhaimart, kasan k'anwar tamu da iya shishshigi,don da tana nan bazaka wani sha wahala ba,ita da kanta zata dasa maka fulawan ka.

Bai tsaya bin Ta Abdoul Manan ba yayi waje hadi da nufan Side din Mom Zaituna. Yayin da Huday ya bishi da kallon tausayi tabbas yana masifar Kaunar Yarinyan".

Niko Suhaimart da futana ina a tsugunne ina Alwala sai ji nayi numfashi na na daukewa,nan take Jini yafara zubo mun ta hanci.
da Sauri na saka Ruwa ina wankewa,hadi da saurin nufan Daki na,can kasan Katifa ta na daga na dakko wasu kwayan mgnin ta tafara afawa. kusan mintuna biyu sai jinin ya dauke,komawa nayi na bi Ifyn Gado,hawaye nabin kuncina babu kakkautawa". A haka bacci yayi awon gaba dani".

Shiko Sir Khaleed da yaji duk yanda sukayi da Suhaimart a bakin Aysha bai san lokacin da yace Aysha ki fadamun ko wata kasa kkso na raiki ki a watannan,wannan Albushir da kk mun bana da kamanki.
Dariya tayi sannan tace" Ni Yah Khaleed Saudiyya zanje inaso nayi Umrah,don a tunanin ta kota tasamu tayi Addu'a wanda takesi ya sota itama".

Angama Aysha a satin ki shirya". Kallon sa tayi gami da zaro ido tana cewa kaman bikin Yah Huday nan da Sati biyu ne masu zuwa,ae sai an gama sannan sai na tafi".

Sosa kyeya yayi sannan yace" Na tuba Aysha ngd Allah yy maki Albarka".

Amin yaya na".
Tace suna mai sakkowa kasan falo don nufar dirning da Mom keta kwala kirar su,akan komai ya kammala su ake jira".

Kai wannan Rana dukkan su,dangane da Khaleed, Huday, Abdoul Manan, Aysha duka sun tsinci kansu cikin matsanan cin farin ciki". Don haka suke cin Abincin su suna zuba santi hadi da fira suna dararraku,ita kam Hjy Zaituna mmki ne ya cika ta,wai dukansy suna goyan bayan Khaleed kenan? Haka dai tayi ta Dauriyya itama Ana dan taba firan da itah".

Niko Suhaimart ko da gari ya waye,wanda Ranar ta fado ran Alkhamis kenan,kuma a wannan Rana A gidan Hajy Zaituna yafi mata kowacce rana,don bak'aramun wahalar Aiki muke sha

ba,saboda a daren Juma'a mai gidan nata wato Gen. Yak'ub yake dawo wa". Don haka tun safe sulaim ta shigo mun akan na shirya na tafi,amma Oumma na sam tak'iya,Acewan ta in Yau na koma kuma ai kilah sai duka ko kuma kaini Station,ita sam bata da Arzikin jayayya dasu,don sun fi karfin mu,ayau koda tana dashi bata ga dalilin tashin hankli ba,don haka ne tace mani nayi zama na,zuwa gobe na naimi wani wajen aikin.

Haka Oum Sulaym ta tafi jiki babu kwari,wanda koda ta je gidan Hajy Zaituna,bayan ta kammala koman ta ne,tana cikin saka ma zuciyan ta inda zasu tafi itada Suhaimart niman aiki kawai saiga Nana Aysha ta zo side din Sir Khaleed din". Cike da zakuwa da son ganin Suhaimart tafara tambayan Oum inda Suhaimah n take,Amma cike da inda² Oumu Sulym ne tace" Yau bata samu zuwa ba". Kan Nana Aysha ta bata amsa ne sukajiyo muryan shi don duk basusan da Zuwan sa ba yana mai cewa" Sulym menaji kina cewa? ina Suhaimaet?.

Shiru Sulym tayi kan daga bisani tace" Yau bata samu zuwa bane Ranka yadade".

Yana a tsayan gami da kafe ta da ido,don san fahimtan wani abu,kunsan Abunka ga Arctist tuni yayi Observing din Abubuwa da yawa dan gane da maganan Oummu Sulaym don haka sai ya saki wani murmushi mai ciwo gami da mgn can kasan makoshin sa yana furta Maiye Dalilin Rashin Zuwan nata?".

Sir Khaleed Wlh ban sani ba,ina tunanin Wani abun ne".

Kallon ta yy hadi da bin Aysha dake tsaye nan suka hada ido,a ransu duka suna maimata kalmar kila wani abun ne!" wani abun mene??. Tambayar da duka suke mawa kansu kenan".

Ohk Zaki iyah tfy". Yace mata a gajirce yana mai nufan Dirning shida Aysha,don Abdoul Manan Bai kwanan gidan ba,a gidan Huday ya kwana".

Zama Aysha tayi,bayan ta jah masa kujera,nan wasu ma'aikata wato Cook suka taho don su fara Aikin Serving nasu,amma sai ta daga masu hannu alamar no need,don haka nan suka juya hadi da komawa bakin aikin su,wasu kuma suka nufi side din Mhiss Caterine don sanar mata da kammalawan su".

Sulaym kuwa tuni tayi nisa da barin Side din Sir Khaleed ta nufi nasu barayin".

Itako Nana Aysha bayan ta zuba masa break din sane,nan ta kalle sa duk da tasan abune mai wuya ya iyah yin break din nasa a halin yanxu". Haka amma ta daure Wurun cewa" Yah Khaleed Bismillah". No Aysha kiyi break din naki kawai,yanxun ni zan wuce Company".

Da jin haka yasa ta a sanyaye mikewa tana mai cewa" Plz yaya ka natsu wlh Suhaimart fah zata dawo gareka,kuma gobe ma Daddy zai dawo duk mu huta".

Wani kayataccen murmushi ya sakar mata kan daga bisani yace" Aysha nasani,nasan

Suhaimart ta wace,ni kuma kadai,vabu mai kwace mun itah,but ki sani,baxan iya cin Wannan Abuncin ba ne,saboda Harshen ne yasa ba dajin dandanon ta,a halin yanxu girkin ta kawai nake bege bana bukatar na kowa". ki kwantar da Hankalin ki my littale,zan dawo cikin Koshin Ify". yana fadin haka ya juya hadi da ficewa daga dakin".

Itako Aysha Zama tayi dabas a kan kujera ta kasa motsawa,tayaya zata fara ganin ta faran ta ran Yayan nata ne,amma bata sani ba".

Zaune na hango ta,sanye cikin wasu dakakkun Bowel lace masu masifar kyau,wanda suke dauke da Launin Cofee brown,Daurin Ture kaga tsiya ne ta tokaro shi,yayin da fuskan ta ke dauke da Kewayayyan farin glss kuma dan siri wato medical. Dattajiwace wanda ashekaru bazata Haura 50 ba aduniya. duk da hutu ya boye wannan shekarun nata,don bazaka ce ba sai an fada maka, mata ce wanda da kaganta zaka fahimci irin matannan ne masu harkan gske,fatan jikin ta kuwa luff² yana sheki da kashe ido.komai nata karr²..... Da ka ganta kaga farar Bafullatana,fara kuma mai Farar Aniyya,Bakowa bace wannan mata Illah Hajiya Huwaila,Amarya kuma Uwar gida ta wajen Ahj. Muhammad Harun. Wato mahaifiya a wajen Arch. Huday da Iftyhal".
"Ohk mashaallah". Tom dear ina jiran isowan ki fah,ta gumi zaman jiran isowa,sai kuma tasaka dariya". tana mai datse wayan nata hadi da mika shi ga Wata Assistant nata".

Da kuka ta shigo falon hadi da nufan Upstairs da dan gudu".

Bin bayan ta Momy tayi cike da damuwan ganin diyar tata cikin wannan halin tayi saurin kirar Sunan ta da Baby Ifty.." Ifty na". Nan Hjy. Huwaila ta fadi gami da mikewwa don nufan Upstairs don ta lura da daru Autan nata ta shigo.

Koda ko taje tun a bakin Bedroom din Iftyhal ta tadda a gar make,wanda bugun duniya taki budewa,haka tayi ta Bata baki amma nan shiru,babu abun da take jiyota tana furtawa sai kalmar Sunan Khaleed".

Shiru Mumy tayi gami da juyawa tana nufan kasa,wanda da saukan ta dai² Maryam da suka gama waya tana shigowa,da sauri tana nufo Momy tana Rungumeta gami da cewa" Oyoyo momy na, I really miss u".

Murmushi momyn Huday tayi kan daga bisani ta sha fuskan Maryam tana furta Nima haka Daugther na ya Mom din ki,tana Ify?".

Lfyl,ta bata amsa a takaice. Momy ina Iftyhal?.

Nisawa Momy tayi sannan tace" Yau ifty yan darun na kusane,amma tana sama kije ki lallashi Aminiyar taki ko kila ta sauko inta ganki".

Tom Momy,ta fadi hadi da nufan Upstairs...

Niko Wuraren Karfe 5pm ne Oummu Sulym tazo mun,akan itama tunda na janye aiki gidan Hjy Zaituna tom itama ta janye,amma a yau taji labarin Wata Company na daukan ma'aikata masu goge$^2$ da shara,don haka su shirya da sassafe su tafi can".

Sosai Oumma na tayi na'am da maganan Oummu Sulym yyn da nan ta kalkeni gami da cewa" Suhaimart kin gani ko? ae duk bakin da Allah yatsaga baya taba hana sa Abincin da zaya ci". ki natsu inshaallah goben zakuje can". Da tom na bi Oumma na,kan daga bisani mu cigaba da taba hirar mu da Sulaym mafi yawa dai dariya nake sha,don duk mgn ce akan inna Atine. wanda daga karshe mukayi sallama akan sai goben.

Dako Sulym ta isa gida,sai da aka ta6a daru da inna Atine acewanta dole sai sulym ta debo masu Ruwa,ita kuma tace sam bazatayi ba,ga inna Wuri nan tayi,sosai Sulym tayi ta amayar da abun da ke cikin ta ganin babu Inna Laure da Baba. itako Mama Atine daki tashige don yau ta lura Sulym din dai $^2$ da ita take a gidan".

Da safe ko kaman yanda mukayi da Sulaym karfe 80.00am muka bar gida yyn da Oumma na ta bimu da Addu'a sannan muka fito".

Me Napep muka tara hadi da sanar masa da companyn da zamu nufah a yanxu wanda yake can wajen gari,wuraren Samaru kafin ka kai Abiation.

Bangaren Ko Iftyhal dajin muryan Aminiyan nata ne ta bude kofahn da sauri hadi da koma ta fada kan makeken gadon ta tana mai jawo teddy jikin ta tana wani irin kuka mai dacin gske".

Da sauri Maryam ta saki Wasu doguwar rigar Gown da ta riko,ala dole taxo nuna mata shi duka zasu saka aranar Get togethern da zasuyi shi yasu yasu nan da Kwana Uku,wato su kadai kaman Ita Maryam,Aysha,don dama Aysha kawace a wurin Maryam tun bayau ba,sai Iftyhal,Abdoul manan,Huday,Khaleed sune kadai zasuyi wannan Get togethern wanda duk cikin shagalin bikin da zasu fara Gabatarwa ne.

Hmmm niko Maman teddy nace anyah na za'ayi bikin nan kuwa,naga wuta tafara ballewa ne ta ko inah. Inajiyo Addu'ar ku gareni da kuma gdyn ku ,nima ina gdy kwaran gske,Allah yabar mun ku yabar kauna".

Cike da matsananncun damuwa Maryam ta nufeta hadi da tambayan ra Ify?  meya sameta".

Da kyar Iftyhal ta samu ta dai$^2$ ta na tsuwarta tafara koramawa Maryam zancen komai da yafaru dangane ita da Suhaimart.

Wani dogon tsaki Maryam tajah,hadi da jawo Asha riyya tana Auna ma Suhaimart dacewa" Yar

matiyata kawai,wlh ki bari sai mun batar da wannan Yarinya". Amma ki bari ba yanxu ba,for now ki kwantar da hankalin ki,ki nuna kaman komai ya wuce maki,idan kikayi haka shine nan koda anyu komai vaza'a zargemu ba".

Kisani nan da Kwana 13 ne biki na da Huday, amma kifara kirga rayuwr wannan yarinya da Duk Dangin ta yazo karshe. nayi maki Alkawarin wlh sai munyi bikinan cikin Kwanciyar hankali,kuma kafin nan kinsan Khaleed ya zam naki har Abada".

Dariya suka sheke dashi,wanda Huday da yake bakin kofah don Momy ce ke sanar masa da zuwan Maryam shiyasa ya nufo bedroom din Iftyhal din,kansa ne ya sara masa rasss....

Dajin mugun nufin su akan marainiyan Allah,wani tausayin Suhaimart ne yaji ya tsirga masa". da kyar ransa yagama baci sosai ya juta hadi da nufan varayin sa. a Zuciyan sa yana mai wasiwasin anyah ya samar ma y'ay'an sa Uwa ta gari kuwa??".
Hmm muje Zuwa fans..💃.

Niiko da Oummu Sulym bamu isah wannan Company ba sai Wuraren 9.00am.

Mun dan sha wahala matuka kan Abar mu muka shifa daga cikin companyn,don mun sha bincike har mun gode Allah, don da kyar duk da hakan suka barmu,banda bin mu da kallon wulakanci babu abun da wa'annan securities sukeyi, Suna kare ma surfaffun Atamfan jikin mu kallo,wanda ya dade da fita kamannun sa". Bakar hijab nasaka amma aaboda koda gar jajjah takeyi daga sama".

Da kyar dai suka bar mu muka shifa don ni nayi ta masu magiya akan su taimakemu. A haka suka hadamu da Shugaban Masu Cleaning din da share² n da kyar.

Itama kam fa ba wani arziki ne da itaba,amma abun ka ga mutanen Nigeria da sungan su wani matsayi sai su nima taka mutum,nan itama ta bimu da kallon Wulakanci don taji mai ya kawo mu". Office nata ta nufah damu,hadi da bamu ma sauki. Tana mai mana wasu yan tambayoyi,da tambayar mu inda muka da kata da Karatu,anan duka muka bata amsa da Secondary muka tsaya,don ni a SS 1 na dakata,har gomma Sulaym takai SS3.

Muna a Zauna ne wani mutum sanye da shigar sa ta court ya shigo,wanda nan naga tayi saurin mikewa hadi da dan Rawar jiki tana furta Weldone Sir".

Ammm Mhiss Zayyad Muna son ganin ki yanxu".

Okay Sir ".
Abin da tace kenan hadi da saurin bin bayan Wannan Mutumi da babu shakka ko ba'ace ba wannan bayahude ne. nine mai fadan haka a Raina".

Zama mukayi mukayi shiru,babu mai magana,don Oummu Sulaym hankalin ta nan kan Wurin da ya kayatu komai abun burgewa ne da kallo". Ko wani lungu glass ne,da na'urori gasu nan dai".

Bin wani Hop nayi da kallo,wanda nan take kirjina ta buga,ido ba kuma zarowa waje ina kare ma Hoton dake jikin Garun da kallo,don bakowa na gani ba Face Sir Khaleed,da shigannan nasa kai ka rantse bature ne.

Zaro ido nake ina mai kuna fito dasu,dai² na bude baki ne zanyi ma Sulaym mgn, Mhiss Zayyad ta shigo".

Don Allah ku biyoni. Babu musu duka muka bike hadi da bun bayan ta. Tfy mukayi mai dan tsawo wanda duk wani wuri da zamu wuce sai na Urah tagama lacce mu tass,sannan.

Ahaka muka isah wani Office da girman sa ya tsora tani,amma na dake sam na waje na baya hango mu,amna mu komai ganin sa muke kaman a gaban mu".

Tun daga nesa muka hango shi zaune kujeran nan na juya shi gaba daya hankalin sa na kaina". Wani sanyi yakejin yana ratsa shi.

Zaro ido waje Oummu da sai ayanxu ta ganshi tayi".

Niko da gudu na juya da zummar futa na koma inda na fito,amma sai wani sexurity yy yunkurin tareni. Banyi aune ba naji Sir Khaleed yasar masa wani wawan tsawa akan ya varni. da sauri ba fice hadi sa gudu² sauri² don na bar ma'aikatan".

Napep na tara,hadi da shigewa ciki nan na bar Oummu da Sir Khaleed don bansan dunuyar dasuke ciki ba".

A layin tudun wada ya sauke nidon daganan ne kudi na ta kare,shi yasa na fara takowa dan shifa cikin Zaria da kafah".

Nayi tfyn fiye da Awa daya sannan na isah gida".

A bakin gidan mu ne ta tadda wata moto da sam ban wani tsaya kare masa kallo ba nayi cikin gida,don na kwaso gjy sosai.

Amma kuma da shiga na a bakin Kofan dakin Oumma na ne wazan gani kuma naji?. muryan Sir Khaleed naji yana mgn da Oumma na,wanda hakan takuma haddasamun bugawan kirji.

Mu sani Free page na gab da karewa,inshalh free page zai kare a page 15.

Don haka mai bukatan karanta littafin ZUMA DA MADACI zai turo #200 na NORMAL DA VIP. SPC kuma #300. duka katin MTN ta wannan Number 08081202932/09137392680.

*#SHERE TO ANOTHER GROUPS*

*Maman teddy 🧸*
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*page 15*

*______________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*______________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*

_Dedicated to my teddy🧸Wannan pagen taki ce y'a d'aya tilo😂._

*_Domun samun Littafin Zuma da mad'aci tun daga farkon sa har karshe zaki tuntubi wannan number 09137392680/08081202932._*

_*Plz don't miss dis novel,the latest  Hausa nvl in 2021.*_
_*Do not miss this Novel Hajiya ta,idan baki karanta ba an barki a baya Hajjaju....💃*_

*________________________________*

Wani gumi ne ya hau karyomun,yyn da lokaci guda cikina ya fara murda mun,kasa daga ko kafafuna nayi,so kawai nake najiyo Mai Sir Khaleed da Oumma na suke cewa,amma nakasa jiyowa".

Motsin su danaji alamar kaman fitowa zasuyi yasani saurin motsawa don na gudu,amma inah banyi wani motsi ba". Har ya fito daga dakin,Oumma na kam na tayi masa godiya". Kafe ni yy da wannan mayan kallon nasa,wanda yasani saurin sidda kai na kasa,don sau dayawa inyana mun irin wannan kallon bana fahimtan komai da yake nufi. Wani kasaitaccen murmushi ya sakarmun hadi da bin jikina da kallo ganin yanda nake ta Rawar kyarma kaman wanda nayi gagarumin laifi".

Oumma na tafi".
Tom Khaleed Allah ya tsare". Amin yace da itah kan daga bisani ya fice,niko baki bude nake bin Oumma da kallo,sarai nasan Halin Oumma bata da Kwadayi,amma wannan Abun da nagani mai take nufi kenan?_ Tabbas da akwai wani abun a kasa".

Kallon sama da kasa Oumma tayi mun,kan tace maza kiyo Alwala idan kin kammala inason mgn dake". Niko cike da sakin baki nace tom Oumma hadi da juyawa don nufan Daki na".

Wasu maza ne cike da sallama suka shigo gidan namu,dauke da Caton da buhun hunan Kayan Abinci, Wanda bani ba har Oumma na sai da tayi mamaki,nan tayi saurin cewa" Wannan kuma
```

daga inah yan samari". ta fadi cike da son jin daga bakin su".

Kai tsaye suka bata amsa da Alhaji ne yace a shigo dashi".

Nidai tunda naji haka najah kafa na da sauri hadi da kutsa kai cikin Daki na,ina mai lalubar magani na don nasha".
Da misalin Karfe 8pm.
Zaune duka familyn Gen. Yaqub D'an larabawa duka kowa ka kalli fuskan sa yana cike da matsanancin farin cikin dawowan Dad din nasu". Fira yake da Nana Aysha yyn da take koro masa zance kaman gidan radio". Don dama haka take ita Aysha,nasu sosai yazo daya da Dad. shiyasa kullum take aikin sintirin tsakanin Zaria da gombe".

Kallon Khaleed yy wanda tunanin sa yy nisa kan laptop din gaban sa,wanda sunan yana kallon Laptop din ne,Amma sam hankalin sa ba anan take ba". sosai yayi nisa wajen tunanin Rayuwar Suhaimart don shi a iyah saninsa Tausayi ne yafara shiga masa nata,wanda daga karshe ya fahimci da ya kamu da Azababban sonta". Khaleed kuma irun wannan mutanen ne da idan suna kaunar mutum to ko ainah zai ce yanayi,idan baya kuma Ra'ayin ka kashiga uku da Hantara.

Tuni Mahaifin nasa ya dago da damuwa tare da d'an nasa,don haka ne ya gyara zama yana mai kallon dukan su ta hanyar cewa" Amm Hajiya Zaituna dama ina son wata yar magana ce daku,don haka don Allah inason ku bani hankulan ku".
"Tom genar muna sauraren ka".
Gyara zama Genar yayi kan yafara cewa" amm dama naji mgn ce game da Khaleed da kuma wata yarinya da naji ance mun yar aikin nan gidan ce! tom so nake naji gakyar maganan a yanxu".

Wani kayataccen murmushi Hajy.Zaituna tayi don an tabo inda yake mata kaikayi,don a yau za'ayi ta ta kare dole ne Khaleed ya janye daga soyayyar wannan Yarinya mai kyau Aljanu. Cike da kwantar da murya gamai gidan nata,ta fara cewa" Kwarai kam Genar dama nima inaso nayi maka mgnar,amma sai na bari ka huta sannan,mashaallah tunda yanxu kaji Ibarn dai duk da ba duka ne ba!.

Nisawa Hajy.Zaituna tayi kan ta fara koro mawa General komai da yashafi Khaleed da Suhaimart,wanda daga karshe ta sanar masa da natsayan ta akan cewa ita sam bata kaunar ta,kuma dole ne Khaleed ya rabu da itah".
nan ta kuma cewa" Amma Genar kar muji Haushin Khaleed, wannan yarinya ne shaidaniya,don ina tunanin Wlh bata barmun Yaro haka ba".

Jin maganar da Hajy. Zaituna take zibowa yasa Genar saurin daga mata hannu alama na ya isah!!
Sannan cike da d'an bacin rai ya fara cewa" Haba Hjy,da girman ki da hankalin ki kuma? wannan mgn taki sam batayi mun dadi ba,mene naki na shiga Hurumun yara,shifa Khaleed

yace yana son ta,don haka ni sam bazan masa dole ba,kuma kema idan kinyi tunani hakan muce zamu masa dole sam ba'abu mai kyau bane,ki natsu ki sa hankalin a mizani Hajy plz.

Mikewa tayi daga kishingiden da tayi daga jikin Kujera da sauri don har zufah tafara tsatstsafo masa,a sarari ta fara cewa" Yalla6ai Genar mai nakeji daga bakin ka??. Kana nufin Zaka Aurar da Khaleed da wannan yar gidan matsayatan yar talaka?.
Kallon ta yayi cike da dattako yace hajy A gaban yara fa muke,wannan duk mgnan ki bari sai mun zauna daga ni sai ke,Amma maganar Aurar da Khaleed da Wannan yarinya babu fashi,inda yana kaunar ta,Nan ya mai da Hankalin sa ga Khaleed da ya sunkuyar da kai tunda Hjy. Zaituna tafara mgnan har ta gama bai dago ba".
Amm Khaleed Ka kwanatar da Hankalin ka zan Aura maka Suhaimart indai kana sonta,kuma baxaka cutar masu da y'a ba". Don haka kaje ku fahimci juna sosai,ni Mahaifin ka na baka go Ahead,duk randa kuka shirya zan nemi iso ga Iyayen Ta". Zaro ido waje Aysha tayi tana d'an ihu hadi da Rungume Genar tana fadin Dad mun gode,Allah yabar mana kai". Murmushi yy hadi da ce mata Bakomai mama na". ku shiga daga ciki inason mgn da Mom din ku ne".
Sai a sannan Khaleed da Farin ciki ya gama cika shi yasamu bakin cewa" Tom Dad na gode,Allah yakara girma da daukaka".

Ameen Khaleed ".
Nan Aysha ta riko Hannun Khaleed cike da Murna sukayi waje".

Shiko A wannan Rana sosai Genar yaso ganin Hjy.Zaituna ta amince da mgnar nasa,amma ina sam ta kiya,har ya gaji yace shi sam Bazaiyi ma Khaleed dole ba,Aure kam zayayi masa nan kusa,tunda Yaro ya nuna yana son yin Aure kuma yana son yarinya".

Niko nace muje dai Zuwa💃 .
Kar dai kumanta free page yakare daga wannan pagen,don haka idan kina bukatar cigaban wannan littafi ki tuntubi wannan Number 08081202932.

Niko tunda na shiga daki sam na kasa fitowa sai Wuraren La'asar wanda da fitowa na natadda Oumma Zaune bakin Wuta a madafi( Kitchen ), wanda da'alama tana hidimar dora abincin dare ne".

Barka Da gida Oumma". Dagowa tayi tana kallo na kan daga bisani tace mun Yowa Suhaimart, bacci kikayi ne?.

Ehhh", Amma yanxun na tashi Alwala ma zanyi".
tom idan kingama kizo inason mgn dake". Tom Oumma na". ina fadin haka na dauki Buta don yin Alwala,bayan na gama ne na nufi da na nayo Sallah.

Fitowa nayi bayan na idda sannan nashiga dakin Oumma na".

Sosai na firgita da Maganar da Oumma na ta mun,wai acewanta Bata yarda na bar aiki gidan Hjy.Zaituna ba". Kuma tayaba da Hankali na Khaleed, bata yarda ta kuma jin wata baraka daga gareni ba". Sosai Oumma ta dinga yimun fada hadi da zagi na,wanda daga karshe ne Tafara lallami na akan nayi hakuri na so Khaleed, ni danake Marainiyya mara gata Talaka,amma irin wannan mai Arxiki yazo yace yana sona nakiya". Don haka nan tace mun na kuma tunani,amma ita tana mai son sanar mun da ajiya tayi masa Alkawarin zata Aurar dani ga Shi Khaleed din,ko naso shi kona kishi wannan duk ni nasani". Nan tace na tashi na bata Wuri,haka jiki na sarai ya mutu da mgnar Oumma na,daki na na shiga don naga Oumma na Ranta ya baci, Tabbas a raina inajin Kaunar Sir Khaleed, amma ni gani nayi ni bakowa bace,bana da Uba da Asali,anyah zai kaunace ni,amma sai naga akasin haka,don a bayanan Oumma na cemun take,wai Khaleed ne Abun tausayi tunda ya kamu da son Ice matacciya wanda batason maiye so ba".

Kuka ne ya kwacemun,tuno da tijaran Hajy.Zaituna, don wlh nasan baxata taba kauna ta naba,Wanda ni kaina a halin yanxu tausayin Sir Khaleed nakeji na kurewa" Yana neman ma kansa illah duk ta kaina,yaya zanyi ni hakanan zan kokari naga hankalin sa ya natsu kaman da". Haka zan amince da shi koda ko Hjy. Zaituna kasheni ne zatayi,tunda Oumma na na kaunar sa dole ne naso shi nima". Tabbas na yarda Sir Khaleed bason yaudara yakemun ba tundaga kan Abun da yafaru a jiya".

Shiru nayi ina a Zaune naji Muryan Sulaym tana Gaisar da Oumma na,wanda kaman ba ita ta gama zagina ba,cike da harka ta amshi Oummu Sulaym hadi da sanar mata da inda nake".

Ae da Sauri ta kutso kanta daki na,muna hada ido muka saka dariya duk da damuwan dake cin Zuciya ta".
Mun ga takanmu Suhaimart, kinga wannan mai mukayi kenan,munyi gaba mun dawo baya".
Murmushi nayi mata kan daga bisani nace,tom ya zanyi Sulaym,yanxu Oumma na tace sai na koma bakin aekin gidan Hjy. Zaituna ".

Na fadi cike da nuna damuwa kan fuskata". Tom meye,ae dama komawan mu dole,wai na tambaye ki tsoron Hjy.Zaituna kk ne? Wlh Suhaimart ki natsu,shin da itah zakuyi soyayya ko da d'an ta"? don haka ki share komai,wlh jiya Sir Khaleed ya ban Tausayi yanda yake Rokona akan nasa ki Kaunace shi,Har Kwallah sai da ya kwanta akan idon sa". Haba Suhaimart a wannan Zamani ki samu mai maki Wannan zafin son!?.

Don Allah ki yarda ki amince da Sir Khaleed, a ranar biki mucashe mu jagije".

Dariya nayi mata ina mai cewa" Oummu na Amince da Sir Khaleed dama tuni,amma ni tsoron Hjy.Zaituna nakeyi Wlh ". Na fadi hawaye na sakkomun kan fuska ta". saurin sharemun hawayen Sulaym tayi kan tace" Ni ina ji ajikana babu abun da zai faru,ki natsu ki maida Hankalin ki akan Sir Khaleed, don na gaya maki wani gulma,itafah wannan Iftyhal din ashe son Sir Khaleed takeyi,da yake ita yar wahala ce".
Zaro ido nayi ina cewa" kinganki ko Sulaym wlh tsiwanki shi zai jahxamana fitina".

Taba baki Sulaym tayi kan daga bisani tace" Wlh bakomai,ni wai ina tsoro ne,abun da na fada bayan idon ka shi zan maimaita koda kuwa itace a gaba na,ai kin sanni basai nace maki komai ba".

Dariya nayi ina mai cewa" Kwarai kuwa Aminiya ta kuma".

Haka dai mukayi ta firar mu muna Dariya cike da nishadi kaman kar mu rabu da junan mu".

Bangaren Huday kuwa,a wannan dare yanda yaga rana haka ya ganta,sam ya gaxa rintsawa,wanda daga karshe mikewa yy hadi da nufan Toilet ya dauro Alwala hadi da yin nafila,yana a zaune bayan idar wansa sosai yake addu'a kan Za6in Allah kuma nagari. sannan ya mike hadi da nufan falon gidan nasu". don a gidan Momy Huwailah ya kwana".

Zaxo wuce Dairning Area ne nan take idon shi ya sauka akan fuskar ta,wanda take dauke da ,sanye kuma cikin Uniform din ta mai launin skirt Dark brown da farin riga". kafe ta yayi da ido,wanda nan take lokaci daya yafara tunanin Ta a Zuciyan shi". A sarari kam furta wa yayi I really miss u my little". Cike da jin matsanancin kyewanta ya nufi Dakin ta da yake a gyefen na Momy,kutsa kan sa yayi ciki yana mai tunano abububuwa da yawa,Zazzakan muryan ta na masa amo a kunnen sa Hamma na yau Daddy na zai dawo,kuma Daddy yace next Mounth zamu bar nageria mu koma Abroad da zama,saboda Momy zata tafi karo Couse acan". Plz Hamma Huday kar mu tafi ni bana son na Rabu da Nanny na".
Kallon ta yy hadi da rungumo ta yana kallon ta da A lokacin bata fi shekaru 4 a duniya ba". No my little zamu tafi,amma baxamu dade ba xamu dawo".kuma idan ma kinason wata Nanny ne Daddy zai dauko maki wata mai kula dake,kaman wannan".
A'ahhh...Uhmmmm....Niiiiii Uh"umm. nan tafara kuka hadi da saka masa rigima akan A'a.

Jin yayi bige wani abu kaman Glass yasa shi dawowa daga duniyar tunanin da ya lulah,saurin kallon Wurin yayi yana mai saka Hannun sa yana daukan wani Cup da yake irin na glass ne,amma gyefe guda dauke da Hoton ta da ya zana ta tun a shekarun baya". Kwallah ne ya ciko masa ido kissing din Pic din nata yafara yi yana fadin kalmar I miss u my.....

Niko maman teddy bin ko'ina na dakin nayi da kallo,wanda ta ko'ina hotunan wata diyace y'ar shekara 4\5 a jikin bango dama ko wani Wuri in idona ya sauka akai. ni kaina kyaunta sai da ya fixgeni,yarinya ce kyau har kyau ko Y'ay'an turawa Albarka,nikam mashaallah kawai nake furtawa".

Kan tarkato na fito ina mai son Kawo maku Rahoto dangane da wannan yarinya amma ina gani nake babu isashen lokaci".
Amma maji a gaba".

Tun safe na tashi nayi shiri na tsaff sannan na nufi dakin Oumma nayi mata sallama akan zan tafi aiki na. da Addu'a ta bini dashi,sannan na fice ina mai jin dadi matuka da Yanda Oumma na

sam bata gajiyawa da mun Addu'a hadi da samun Albarka".

Iyaye mata plz we have to take note,idan yaran mu zasu fita zasu bar gida,mu ringa kokari muna bin su da addu'a ahaka har su dawo,inshaallh zasu da cikin yardan Allah batare da wani abu ya cutar da su ba". Musamman mun san Bakin Uwa akan y'ay'anta". Don haka mu ringa daurewa munayi,in ma bazaki iyah ba,ki kokarta kisa ko shi yaron yy Addu'a kan ya fita,kaman Ayatul kursiyu,Nasi,ihlas da falak. wa'annan ma sun wadatar.

Tun da na shiga gidan Hjy Zaituna kowa ke bina da kallon Wani iri,nikam ban fi ta kansu ba,duk da na dadaru,amma haka na daure don ko Part din Hajy. Zaituna banyi ba,da ko nazo wajen wata da'ake kira da Hanne ne ta kalle ni tana cewa" Allah kam ya kyauta sai kace wata mayya??? Mtswww turrr wlh.

Tsayawa nayi na kallesu sai na girgixa kai kurum ina mai nufan Bangaren Sir Khaleed ".

Sai da nayi kuka na na gaji dana shiga kitchen,sannan bayan  na yi har na gaji ne,na wanke fuska na sannan na fara aikina".

Yana kwance tundaga bedroom nasa ya fara jiyo daddadan kamshi,wanda yasa shi lumshe ido bai shirya ba". Cikin sauri ya mike hadi da fara shiryawa don da jin kamshin ya san Suhaimart din sa ta dawo gareshi,wanda a yanxu ne yake jin zai fara tsara soyayya tsaftacciya mai kuma ban sha'awa da birge duk wani mai kallo".
Niko ina aikin kaiwa da komowa ne najiyo muryan shugaban mu Mhiss Caterine cike da Harka wanda bata ta6a yi mun shi ba ta hau cewa" Suhaimart har ki karako,shine ba k zo mun gaisa ba".

Cikin sauri kuma cike da dan jin nauyin ta na ajiye wani foodflask akan Dirning Sannan nace amun Afuwa Ranki yadade,wlh naso nayi Latti ne,kuma nasan Sir Khaleed da wuri yake fita shiyasa na bari na kammala masa sai na karako".

Ehh gsky ne my dear,hakan yy kyau,kiyi komai a natse kinji"!?.
Tom nace da itah kan na cigaba da shirya Dirning din ita kuma ta fice daga Falon.

Ina a haka ne na fara shako kamshin turaren sa dayake sani karajin wani Iri,kirjina ne lokaci daya ya buga,amma sai na dake tuno da mgnar Oummu Sulaym akan na yarda na amince ma Khaleed kodon na faranta ran Oumma na,kuma kar na ta6a kosawa dashi ko gudun masa".
komai yace mun na bisa da Ehhh ne".
Wannan yasani cike da natsuwa na cigaba da aiki na ina mai jin takon sa har ya iso gareni".
Cikin wata irin murya mai cike da nuna So da kulawa yace mun" Barka da Safiya Hayatee na".
Dagowa nayi na kalleshi hadi da sakar masa da wani kayataccen murmushi na da ya bayyana siririn Hyshurya ta da ya karamun kyau nan nace" Yauwa Barkan ka da dai Yallabai".
Dariya yasa hadi da cemun wato yau din sokana kk jin mun,wato Yalla6ai?"

Murmushi nasa masa ina mai jah masa kujera alaman ya zauna sai da ya zauna ne nace tuba nake Ranka yaded'e Afuwan mantuwa nayi fah kace kai ba Yalla6ai bane a baya".

Hmmm Ashe kin damu dani har kin rike nace banson kalmar nan". Kallon sa nayi hadi da masa murmushi kan daga bisani nace tom ni na isah nace ban damu da Oga na ba". ae dole duk abun da ya fadi na rike,da da hali ma har rubuce shi zanyi a takarda gudun mantuwa".

Na fadi ina mai jawo wani flask hadi da dauko Mug ina fara hada masa tea".
Ae koda kin manta Ni bakya laifi a waje na,kinsan shi so hana ganin Laifi".

D'an murmushi nayi cike da jin kunyan sa kan furucin sa na sunkuyar da kaina kasa.ina mai cigaba da Hada masa break din. shiko Ganin na sunkuyar da kai yasa shi dariya wanda ya kuma bayyana mun haiban sa da kamala,nan yace" Hayateee na kince ni Ogan ki ne,bayan Oga kuma fah".Kallon sa nayi sarai na fahimci mao yake nufi amma sai na dake ta hanyar cewa" Kaman ya kenan,ban fahimta ba Sir Khaleed ".

Cips din gabansa yasa ka fork yafa ci kan daga bisani yace kinga kaman ni kina da matsayi masu yawa a tare dani,daya daga ciki kuwa shine U ar my luv. inason ki Suhaimart".

Saurin dukar da kai nayi ina murmushi ina mai wasa da yatsuna,Hanne ce ta taho hadi da sanar mun da Mhiss caterine nason gani na ina kammala".

Kauda kai yy gyefe cike da Daure fuska,kaman bashi ne yake dariya ba,nan take bani kaina ba har Hanne ta tsoron sa ya kamamu". baki na har dan rawa yake cikin Sauri nace mata tom".

Muryan sa naji yana cemun tom mene? ,sai kuma ya juya yana mai kallon wannan Hanne fuska daure yace fita ki bani wuri idan kingan mu tare ba kyaba bana son ganin kowa". jiki na rawa Hanne ta fice,niko binta da kallo nayi ina tunano zagin da tamun".

Sorry Suhaimart dina,kuma mata na". Murmushi nayi cike da kunyan sa nace" Sir Khaleed yakamata kaci abinci kar lokaci ya kure maka".

Dariya yayi kan yace bakyaso nayi late ne?"
Daga masa kai nayi ina mai ci gaba da serving nasa".

Murmushi yy break din yakeyi kaman wanda ya shekara baici abinciba,tausayin kanmu ne ya kamani,don tabbas na fahimta rabon shi da cin wani abu tun randa wannan abu ya faru". Kallo na yy gami dacewa Matan kinsan meye?
Girgixa masa kai nayi alamar A'a. ajiye Spoon din sa yy yana mai cemun" na dade banci abinci mai dadin wannan ba".

Zaro ido nayi waje,ina dariya gami dacewa" A'a Rankayadade kar ka yabeni don ka burgeni fah".

Da gaske Suhaimart kin...Lovers"masoya kenan... wlh kuna birgeni fah,Aysha ce mai wannan maganan ta fadi tana mai zama gyefen Su ta hanyar jan kujera tana zama".

murmushi yy kan yace Aysha kin tashi kenan". Ehhh Hamma Khaleed, Allah ya tashemu". tom Mashaallh.ni bari na Wuce Yafadi yana goge bakin shi da Tissue yana mikewa daga zaune.

Adawo Ify Hamma". Aysha tace tana mai murmushi. Allah yasa yace gami da kallon Na danayi shiru,kallon ke maizaki cemun yamun,nan nayi dan murmushi hadi da cewa" A dawo Ify Sir Khaleed ".

Nan ya kuma budada murmushin sa yana mai cewa" Ngd Dear". Sannan cike da tokon sa na ingarman Namiji yafara takawa har ya bar falon.

itako Aysha wani irin sanyi ne takejin yana ratsata ko ba komai ta fahimci da mun fahimci junan mu". Mikewa nayi don na fara kwashe kayan kan dirning din,amma nan tafara jana da fira,wanda sam ban san lokacin da na zauna ba,a haka muka bata fiye da Awanni,sai da nace mata inada aiki da yawa ne sannan ta barni,dana fara kwashe kayan kuwa nasha mmki,don aiyah sanina Aysha macace maiji da issah don bata yarda da Raini ba sam,wai amma a yau ita take tayani kwashe flask da su bowl da mukayi amfani dashi.

Bayan mun gama ne tace mun na shirya yau zan rakata Shopping Mall tana son tayi siyayyan biki". Da tom na bita har ta fice".

Bayan Yan mintoci ne sai gata hannun ta dauke da jaka da kuma key na moto. Matan Hamma bismillah mu tafi".

Murmushi nayi mata asannan muka fito filin farfajiyan gidan,munafukai kam ansamu abun yi,nikam bamai bin ta kan mutane bane shiyasa na shiga moton kai tsaye Abu na,duk da saida tayi mun Shakiyanci wai ita zata bude mun moto,zata fara biyayya tunda yanxu,nidai Murmushi kawai nake har muka bar harabar gidan.

Wani Malla muka shiga da yake can wuraren Kongo,wanda nasha mmkin kayan da Aysha tasiya wai duk na bikin ne". Sai dai me duk abun da tasiya biyu take siya ana tacewan nawa ne da nata, Don har wani Gown mai launin dark blue ta siya mana guda biyu wai za'asa a ranan Brider's show.

Haka dai tayi tayi har muka gama sannan muka fito. Taso bani kayan amma sai tayi tunanin mubari sai an fara shagalin bikin sannan.

A wannan rana in kaganmu da Aysha ka rantse mu irin Aminan nan ne wanda suka shekaru a tare". Sosai na saki da itah muna fira,wanda sulaym taji dadi matuka data ga hakan".

A washe gari kam haka ta faru dani da Sir Khaleed don yanda yy ta mun surutu haka yau ma yy mun,hadi da fadin kalamomin so akaina sam baya ko jin kunya a bunshi,sai dai ni naji masa". Wannan karan ma cigaba da zai tafi Companyn sa cewa yy sai munje Part din Hjy. Zaituna mun gaisa daganan shima ya gaida ta". Sosai naji tsoro kuma naso nokewa,amma sai yasamun magiya akan yanzu Mom ta amince da soyayyar su,nan yafada mun duk yanda sukayi da Dad. Da haka nasamu karfin gwiwan bin bayan sa muka nufi Part din Hjy.Zaituna.

Da shiganmu Makeken falon ta na hango ta Zaune cike da mulki kunsan ta dai,nan take tsoro ya kamani,yau ni nakawo kai na,fahimta kam da yy da hakan yasa shi girgixamun kai Alamar ba komai.

Haka dai na dake na bi bayan sa,itakam Aysha dake gyefen Hjy. Zaituna ne ta daka tsalle tana ihun murna da cewa " Mom ga surukan ki taxo gaishe ki".

Nan ta nufo ni da duk na dadara tana rungumeni hadi da jawo ni,
gyara zama Hjy.Zaituna tayi tana mai Murmushi n yake naciki na ciki,a'ahhhh sannun ku da zuwa. Khaleed kune??"

Zama nayi kusa da Aysha yyn da Naji yana cema ta" Ehhh mom kin tashi Ify"?.

Lfyl Son" How was ur night?.

kan ya bata amsa ne nace Barka da Safiya". Ba yabo babu fallasa tace Barka". tunda ga nan bata kara cewa komai ba".
Mikewa Khaleed yy yana cewa" Mom na Wuce".

Ohk my Son take care!"
tafadi cike da kulawa. Ohk mom".

Da fitan sa dai² Wayan Aysha na ringing,ganin mai kirar yasata dagawa da Sauri tana furta Hello Hamma Abdoul nayi fushi". sai kuma ta mike hadi da shigewa Wani daki".

Aiko Dama Hjy Zaituna dama take jira da fitansu duka ta wani kalleni hadi da bina da kallon Banxa,kan tace mun kehhhh look Up".

Dagowa nayi a sanyaye na kalle ta".
Ta wani ya tsina baki kana tace" Concrate Worning nake maki,ki fita harkan Khaleed, if not kuma kisani kin shirya ganin Karshen kakka6in dangin ki da sukayi saura,don wlh sai na karar dasu duka,kuma Abun da kk so vaxaki samu ba,shine Aurar Khaleed ko?.

Kyale Yar matsayi ta Mom,wai ita tana ganin zata Auri Khaleed, saboda hauka dakikiya

jahila,anje anbi yan tsibbu,tom duk abinki ki sani Khaleed is mine,nawa ne ni kadai. a wani matsayi kk a karatu. nidai A yanxu im Digree Holder And You?. Ta fadi cike da son jin na baki na".

Duka da kai nayi inajin babu dadi,amma ya zanyi ".
Wani dariya tayi cike da kurewa tace min,kin shirya Ganin Gawar Wannan Mahaukaciyan Iwar taki da take yawo a kwarkwaro naira 10 aka bata amsa zatayi tana gdy". Hhhhh duk iftyhal ce mai wannan maganar cike da gatsali.

Niko Sunan Abun yy mun zafi sai na dake,ban nuna mata ba sam. Mom ne ta cigaba da cewa" Becouse she is mad,shiyasa har take tunanin Zama da Yaro ne, ibeg will you go Outtt". ta fadamun hasale".

Wani Murmushi nayi na tusa ma kowa da Aniyan sa,wanda dai ² Aysha na fito nikuma ina mikewa". Suhaimart tafi zakiyi gashi ban shirya balle na taho side din naku".

Murmushi na mata kan nace a'a sha zamanki,kiyi komai a hankali a natse idan kin kammala ina jiran ki".

Ina fadin haka na juya yyn da cke da rashin fahimtan komai Aysha tabi Iftyhal da Kallon Banza kan ta haye Upstair.

Zama Iftyhal tayi yaraffff,Haka Hjy Zaituna data kwashi mmkin Suhaimart, duk tujaran da suka mata ko a gyefen mayafin ta,lallai wannan yarinya ta shirya".

Kowa da Abun da yake sakawa a zuciyan sa Tsawon mintoci".

Maryam ne sanye cikin shgar ta na Riga da Skirt ta Atampha Super mai Bala'in kyau. Saukowa Kasa tayi hadi da nufo Ammien ta tana fadin Ammie ya kk ganni?.

ta fadi tana mata juyi,dariya Ammin nata tayi kan cike da gogewan Duniya tace" Wow My baby Wannan Duk Huday akayi mawa ne?.

Dariya Maryam tasa kan tace ehhh,Ammai yanxu ma yana jirana daga waje shida su Khaleed da Abdoul,bari nayi sauri don nasan maganan Bikin ne ta kawo su".

Tom Adawo Ify,a ringa dai lafazi mai dadi". Dariya Maryam tayi kan tace tom Oumma na".

*Wace ce Maryam*
Maryam ta kasance Y'a ce ga Alh.Idriss Tabawa,wanda ya kasance Attajirin mai kudi da duk

fadin Nageria da kyewaye babu wanda bai san da zaman sa ba. Hjy. Saimah wato mahaifiyar Maryam itace matanshi kaadai,sannan su cikkakun Hausa Fulani ne". Allah ya albarkaci iyayenta da yara 4 rak,uku mata sai Autansu na Miji mai bin ma Maryam da yake malasia yana karatu a can. sauran yayyaun ta kuma duk sunyi Aure,kowa kaji mijin ta kasan wani ne a gomnati".

Wannan kenan.

Niko Suhaimart tun da na bar Part din Hjy Zaituna nan ina tafe ina tunanin Wulakancin da sukayi mun,kawai sai Kuka ya kwacemun... tsayawa nayi ina mai sharce hawaye na,wanda banyi aune ba naji muryanshi yana furta Suhaimart ".

Saurin jiyowa nayi nan kuwa shi dinne Ya Huday".
Kallon sa nayi kawai sai wasu hawayen sababbi yafa mun sintiri.

Da ganin haka yasa nan take Huday jikin shi yy sanyi a dan rude don sosai yaji badadi duk da bai san dalilin kuk'an ba".

Muryan sa har hardewa yake da kyar ya iya furtamun Suhaimart muje na kai ki gida". Ganin banda za6i yasani Nufan Farfajiyan gidan,yyn da Cikin sauri ya bude mun Moton nasa na shiga,sannan ya koma ma zaunin sa ya bar gidan cikin sauri".

Tafy mukeyi sosai Wanda a halin yanxu har na tsagaita da kukan ganin yanda yake bina da Magiya da ban Hakuri". Cike da mmki nake bin Huday da kallo,ganin hanyan da ya dauke dani ba Hanyan gidan mu bane".

A sanyaye da kuma da sashiyar murya ta nace Yah Huday ina zamu je ne!.
Bai bani amsa ba abun ka ga miskilin mutum kuma bai kalleni ba,har sai da muka dan kara tfy,sannan yayi parking a bakin Hanyah.

Juyowa yayi gami da Kallo na,sannan ya fara cemun" Suhaimart meya faru naga kina kuka,anyi maki wani abune? Mai Mom tayi maki?.

Dukar da kai na kasa nayi kan daga bisani nace" Bakomai".

Bakomai? Hmmm Kalle ni". Ya fadi yana mai kafeni da Wa'annan lumsassun Idon nasa mai kama dana mai jin Bacci,kina so kije gida ko?"
Ya fadi yana Kallo na".

Saurin daga masa kaina nayi alamar ehhh". Nan yasaki mun murmushin da ban gabe manufar sa ba,cemun yayi Tom baxan kai ki gida ba,sai kin fadamun dalilin zuban Hawayen ki".Idan kuma ba haka ba,tom zamu kwana anan".

Hanjin ciki na ne ya kada,salati na farayi a zuciya ta ina furta kalmar sunan Oumma na". Nan ko yy murmushi gami dacemun Oumma ko? yau kam indai baki fadi mun ba baxakiga Oumma ba".

Jin haka yasa idona nan yayi narai² hawaye ya kwanta mun a ciki,baki na na rawa badon naso sanar masa da tijaran da Hjyy.Zaituna tayi mun ba nafada masa,wanda ina fada masa ne Amma Hawaye tuni ya gama jika fuska ta".

Kasa cemun Uffun yy koda nayi shiru,Wanda fiye da minti 15 yana a haka,kan daga bisani ya dago Kai cikin Jarumta kunsan Abunka ga mai Suna Aliyu". Suhaimart ki Aure ni,zan Aureki Ina tausayin ki sosai".

Cike da matsanancin Firgici na zaro ido na waje,hawaye na kuma bin Kunci na,yau ni Huday ya kallah yace yaba so ya Aurah,saboda a rashin sanin koni wace ce a wurin shi,wani irin kuka na fashe dashi mai ban tausayi da tsuma Zuciya".

Ganin ko Haka yasa Huday nan take jikin shi yy sanyi,har ga Allah tun farkon ganin suhaimart yake jin wani abu dangane da itah,kuma a Yau ne ya fiddo shi,baiki a mutu ko ayi rai ba". Abun kuma da yasani kawai shine yana mugun tausaya ma Yarinyan,jin son ta yake kaman jinin shi,shiyasa sam bai yarda a Toxarta ta".

Ganin takasa mgn sai kuka yasa shi cike da damuwa muryan sa a hargitse ya ke wa" Plz Suhaimart ki yarda ki amincemun,wlh baxan Baki kunyah ba,kuma Momy na zata soki,baxata k'iki ba". kawai dai ni abun da nakeso ki amince mun".

Ganin yanda ya wani koma ne yasani cike sa kidima nayi saurin girgixa masa kai ina fadin Yah Huday kaifah yaya na ne". Kuma ko ba wannan ba ina Auran ka da Maryam,don duk naji komai a bakin Aysha".

Wani kasaitaccen Murmushi yy kan daga bisani kan shi tsaye yace" Sai na fasa,ni kece nake burin ki zama Uwar y'ay'ana".

Idan ku ma kina ganin Vazaki amince mub bane,suhaimart baxan damu ba,amma kisani ina maki so mara karko,kuma zan hakuri na cigaba da sonki a Zuciya ta,wanda baxan dai nashi ba har karshen Rayuwa ta". Kuka nasa masa ina girgixa kai dacewa" A'a Ya Huday,Wlh ina sonka,ni kaina fara so Arayuwa ta".

Saurin kallon ta yy yayin da maganganun ta yake dawo masa a kwakwalwa,ni kaina fara so A rayuwa ta". A yaushe kenan,nan wata zuciya tace masa,kodon taga Matsancin Son ta ne a idon ka yasa tace ma haka don kwantar da hankalin ka".

Nan ya kalleni hadi da sakar mun da murmushi kan daga bisani yace"Na gode Suhaimart Amma inason ki natsu ne bayanxu ba,koda Bazaki iya sanarmun da kin amince ba,ki rubuto mun Paper. Na lura a yanxu Natsuwar ki baya tare dake". Daga masa kai nayi,kan yy mun wani

kayataccen Murmushi y ana fadin tom sheremun Hawayenki ko naji sanyi a Zuciya ta,sannan bana son naga kina wannan kukan fah.

Dariya nasa kunsan ni da Harka da kamun da ta wuce nan nace" Tom Yah Huday". Haka yajah moton don nufah dani gida".

Tun daga wannan Rana yan kunya tashiga tsakani na da Huday,danaji Isowan sa gidan Hjy.Zaituna nake guduwa na boye,yyn da A yanxu soyayya ta da Sir Khaleed kullum dada karuwa take,sona kam a yanxu ya riga da yaxama jinin jikin sa,Shi kam da Aysha zuwa gidan mu Wajen Oumma na suke basa da shamaki.

Nuna mun kam so da tattali yinsa yake a gaban kowa,har Hjy.Zaituna don tanan ne ta gane Warning din da tamun ban dauka ba".

Shi kam Huday kullum da soyayya ta yake kwana yake tashi gashi biki kullum dada matsowa yake,don A yanxu saura kwana 8. Maryam gaba daya tagama birkicewa don ta rasa gabe kan gadon Huday din. tsakanin su babu wata mgnan Arxiki,sai aikin miskilanci da mulki da yake mata". Shiyasa kulum ka ganta a halin yanxu cikin kuka a cewanta Huday ya sauya mata baki daya,haka Iftyhal zatayi ya bata Hakuri akan ae ankusa bikin kowa ya Huta,girman kan nan nasa kuwa duk sauke shi zaiyi a kanta.

Da wannan yasa Hankalin Iftyhal Rabuwa gida biyu". san bata ta kaina a yanxu amma kuma ina nan kasan zuciyan ta".

A wata Ranar Asabar ne,Sir Khaleed ina cikin masa aikin Part din sa yaxo hadi da shaidamun da Zu muje wani wuri da shi dakuma Aysha". Nayi mmiki matuka don bamu tava fita wani wuri tare ba,duk zafin son da yake mun a gisa ne,ko kuma inyaxo gidan Oumma na".

Sosai nayi mmki musamman yanda naga bayan fitan mu,wani Mall muka wuce,kaya kam Shi da Aysha suka dinga siyanmun ciki kam harda wanda za'a saka da bikin Huday".
Bayan nan ne da kansa ya zaba mun wata Gown nai Ruwar Pink daga kasa da gyefe an mata adon golden,sai da ya gama tsoka nata sannan muka dauki hanyan shiga G.R.A,wanda a dai² Shogon wata me makeup muka tsaya". da isan mu kan mu fito matan da sauri ta fito daga shogon ta tana mana barka sa zuwa". yyn da nikam da fitowa na ya nuna mata ni,ae konan tajah hannuna na muka nufi shagon tana mun Murmushi da cewa" Ur ar welcm dear"

Na sha mmki matuka ganin matannan yanda tasani na cire hijab din aiki na,nan tasaka ni A inji tafara wanke mun kaina tass,hadi da tsane shi,shagon kuwa matan dake ciki ne kowa sai bin gashina da kallo take ganin yanda ya sauka har gadon baya".

Wasu kuma ina kallon su suna nuno Ni hadi da magana da nuna inda Moton Sir Khaleed yake sukeyi,sam ban fahimci mai suke nufi ba,har sai da wata cikakkiyar magulmaciya ta taho inda

naje tana mai cemun Sannun ki Baiwar Allah".

Kallon ta nayi kan nace Yowa".
A hankali cike da rada² tace wai don Allah kece Yar aikin da Arch.Khaleed aka ce ya mutu a So".

Shiru na mata ina tunanin yanxu har wannan maganan ta wade Gari ni yau ba shiga Uku".

Muryan Aysha da ita har ta saka Gown dina ta irin wanda Sir Khalees ya samun sosai tayi kyau cike da tsiwa tace" Hohoho,Baiwar Allah itace,shikenan tom tashi kije.

Jiiki a sanyaye matan ta mike don ta lura Ayshan itama  daidai da itace".

Itakam mai Makeup murmushi tayi don sosai na burgeta,don na gwada mata Ajin da ni kaina bansan ina dashi ba". Sosai ta zauna ta tsalamun makeup,gashi dai simple ne,amma kyaun danayi ya baci". Ni kaina dana kalli kaina ajikin madubin da ke kallo na sai da nafara wasiwasi nice kuwa dai Suhaimah???.

Aysha kam da dadi yagama cika ta,tun a wurin take daukana pics nikam nokewa nakeyi avun ka daba asaba ba".

Haka Matannan ta Rakoni har bakin moton Sir Khaleed da tunda muka fito yake bina da kallo da ktar ya iya gane ni fah😜.

Da sauri ya fito daga moton nashi yana nufomu hadi da cemun Da girman kujeran kiAnyah yau zan iya Driving kuwa".

Dariya dikan mu mukasa kan yy saurin
budemun gaban moton ina mai zama". A raina kam sosai nakw mmkin Kaunar da Khaleed ke nuna mun".

Haka mika bar G.R.A.muka kama hanyan da bansan inda muka nufa ba...

Shiru ni dai nayi bance komai ba nabar mawa Allah sanin sa da inda zamuje a yanxu,shiko Ogan naku da ya kalleni sai ya saki wani murmushi mai Dauke da tsantsan nishadi da jin Dad'i... Bakin sa kam sa yaki Rufuwa har mmki nakoma wai dama duk cewan da'ake mawa mutane Miskilai  suna fira kaman da Sir Khaleed dani?" Gsky kam indai haka ne ni ayanxu zan iyah zama dasu ba kamanda da dana ke gudun Miskilin Mutum ba".

A dai² Tukur² Zaria a gaban wani irin Gida mai Mahaukacin Girma da yagama tsaruwa kaman na turawa,komai da kaganshi kasan da tsari a kayi shi".

Horn yy ma mai gadin gidan,wanda cikin Sauri ya fito mutumin Hadi da bude wagegen Get din gidan.

Hmm sai da muka shiga ne daga ciki,nan naga ashe ciki ne Aljannar Duniyar...A zuciya ta kam furta mashaallh kawai nakeyi".

Bude Moton zanyi na fita,amma sai yayi saurin dakatar dani ta hanyar D'aga mun hannu". Nan ko na koma na zauna,Shi da kansa ya Zagayo ya budemun Moton wanda ba Maryam kadai ba,har su Abdoul manan Salon Soyayyar tamu ta matukar burge su".
Wani kayattacen Murmushi na sakin Masa kan Mujiyo Muryan Aysha tana ni Nafito Hamma Khaleed tun da bani Masoyin da zai budemun".

Cike da dan jin nauyin ta don har ya manta da ita ya sosa kyeya yana Furta sorry my Eash,kafin na bude maki ne kk fito,Afuwan!!.

Dariya Abdoul Manan da Maryam da suke can nesa damu kuma suna jiyo mu suka saka". yyn da cike da Rashin nuna kaman bakomai a ranta Maryam ta nufoni tana wani Rungumoni da cewa" Oyoyo sisy na". Kai gsky Khaleed baka tabamun Abun da naji dadi kaman wannan ba". Ta fadi tana jawoni,Murmushi nasarka mata cike da Raahin Sanin Kudirinta da mugun nufin ta a kaina". Shiko Huday da yake can inda yake sam bai karoko wurun ba,don ada kishin Sir Khaleed ne ya Rufe Shi, a yanxu kuma ne yakuma tsorata da lamarin Maryam din, lallai wannan shi ake cema mutum a fuska". Itakam Iftyhal da sunan tana gidan su ne,amma tuni tun kan komai kasancewar tasan baxata halarci wurin ba yasata Baza ko ina lungu da sako da cameran da yake dauko mata komai da maganar kowa,wannan kam shiryawa sukayi da Maryam yin haka".

Wani Dariya tasa daga Zaune tana nanata Sunan Maryam,da cewa ae wannan tafi duniya,amma ganin yanda Cameran ya hasko mata Fuskan Suhaimart da yanda ta koma kaman Kyawawa indian nan yasata jin wani mahaukacin kishi,don basai anfada mata Cewa Suhaimart ta fita ba,a'a ita kanta tasani".

A sarari kam furta cewa tayi dole ki kwacemun Khaleed, amma bazai kwatu maki ba,wlh sai kinyi nadama matuka".

Nikam Marainiyar Allah kuma Baiwar Allah da bansan komai ba,Murmushi kawai nake sakin mata a haka ta kama hannu na muka kutsa kai har cikin wata Falo".

Bin ko inah nake da kallo, falon nan kam sosai ya tsaru gashi an bishi da yarfi² na flowers masu kyau pink. Sai a sannan na kalli Huday ina Gaisar dashi don ban yarda na hada ido dashi ba". Dan Murmushi yy kan daga bisani yace" Lfyl Suhaimart".

Sosai Maryam taji wani iri,don sam tunda suka zo nan bai mgn mai tsayi haka ba,daga ehhh sai

a'a. sai aikin Isah yake mata".

Kauda wani tunani tayi a ranta. nan Aysha ta tsaya gyefen Abdoul Manan,sai kuma Nida Sir Khaleed a gyefe guda. su mazan duka shigar Suit sukayi,sai kuma mu duka shigar wannan Gown din da sunan Ga Amarya ce,amma nafi ta komai".

A hankali ta kai Hannun ta hadi da hadewa dana Huday  cike da sanin duniya ta sakar masa wani irin Murmushi n kaman kissah,nikam sakin Baki nayi,ina furta a zuciya ta Lallai duniya kam tazo karshe,Suhaimart kiyi Gaggawar barin Wurin kar a rubata maku Zuni bi tare,shi Allah ba Ruwan shi da Rako kikazo".🤣

Nidai haka nayi shiru ina zaro ido don ganin wai wannan duk taron menene,Amma abun Haushi sai naji an saka wani irin cool music yana tashi yyn da nan Aysha ce tafara takawa tana juyawa,Nikam sam bana Rawa kuma ban ma iyah ba Sulaym ce mazari,amma nasan ko itane tazo nan bazatayi Rawar ba,kallon Sir Khaleed nayi a raina ina furta,komai nasu dabi'ar nasara,wlh wannan baiyi ba".

Kallo na yayi gami da kokarin rikemun Hannu,aeko nayi Saurin kaucewa,dama kunsan Sir Khaleed Dai ba sai nakuma fada maku halin sa ba". Shidama dan zuwa Club ne,haka kullum yake, amma na lura yanxu sam baya zuwa matan Banxan ma na Rage ganin su,ko sunxo korar Kare yake bin su da Shi ".

Matsowa yy daf dani hadi da mun mgn da babu mai jin ta da cewa" Bakya Rawa ne?"

Daga masa kai nayi saurin yi don na tsira da mutunci na". Tom bari na koya maki,yafadi yana kuma son kara riiko hannu na". Cikin Sauri nace" A'a nifah ba Maharramar ka bane a yanxu,ka barni kawai kai dai kayimun nagani". Shiru yy tabbas mgnan ta Gsky ne, Shiko Huday zame Hannun sa daga na Maryam yy yana mata Kallon kinji gsky nan".

Dariya Khaleed yy kan yace naki Wayon,shikenan Amma ranar namu ae zakiyi ko"?

Murmushi nakuma sannan na daga masa kai Alamar Ehh".

Dani dashi ne duk muka samu wuri muka zauna muna kallon su,yyn da Aysha kam rawar ta takeyi don ita fah ko ainah taji kida sai ta taka,dariya takemun hadi da cewa" Suhaimart sai na Ranan bikin ki,ai ba'a ma mgn".

Haka muka saka Dariya don shi dama Abdoul Manan Mulki da Sarauta baya barin sa yin Rawa tun Asalin sa". Shima zama yy,yyn da Huday ya janye hadi da nufo mu shima ya zauna".

Sosai Maryam taji Haushi,amma sai ta dake bata nuna komai ba".

Niko Jin Ankirani a yar Baby Nokia ta yasani mikewa hadi da nufan Wani dan Wuri mai kama da

Coridour,ina wayan ne banyi aune na kuma bansan tayaya ya zo ba najishi a Baya na".

Juyowa nayi ina kallon Huday,takardan dake a Hannu na dama Oready na Rubuta shi tun tuni kawai na kasa basa ne. Saurin kara kai ya tsuna nayi don rinst shi,amma kuma banyi aune ba takardan ya sulube a hannuna,Kashe wayan nawa nayi nayi saurin bin takardan da iska ke kadasa a haka yana kallo na,har ta kardan tazo gaban shi,aiko nan yy saurin saka Hannu ya Dauka yana mai budewa". Cikin Sauri da kyarman Murya nafara masa magiya akan ya bani bana sa bane,amma yakiya,ganin haka yasa nayi saurin barin Gurin da Gumi tuni ya fara karyomun".

Bude takardan yy gami da kallo yana karanta rubutun dana masa,da I luv u tooo Ya Huday".

Cike da wani matsannancin Farin ciki ya ke kara karanta takardan,yyn da Oftyhal tayi saurin Zuming din cameran don kara ganin Abun da Takardan ta kusa".

Sakin baki tayi galala,tana mmki da ta'ajibi, Wani Dariya tasa hadi da cewa" Duka zaki biyu biyu,don kin rasasu har Abada". Sai nabi bayan ka Yah Huday na Raboka da wannan Takarda,sannan ana gobe daurin Aure zan lalata komai naki Suhaimart,nasan dole ki Halarci Wajen Taron Mother's Day,anan zan amsa Speaker na bude takardan na karanta ma kowa daga ranar Mujiya sai tafiki fari.............

Muje zuwa niko Maman teddy nace koya zata kaya a wannan Waje.shin zata lalata komai iftyhal din kuwa????..

Hmmm Tom Allah yasa Kar dai ta lalata ma Suhaimart din kaman yanda tace,Amma kuma nikam nace kila Reshe ne zai juye ma mujiya,wato Kar ta lalata bikin Maryam da Hannun ta".🤣😅

Muje dai zuwa💃
naji Adduoin ku ina gdy sosai da yabawan ku fa kuma nuna soyayyan ku ga wannan Littafi nawa Mai Suna ZUMA DA MADACI, Allah yavar kauna much luv...

Naso na kammala Free page a wannan pagen wato page15. Amma saboda wasu dan Uxurori na mai dashi zan kammala inshaaallh a Pagen na gobe,wato page 16.

Littafin kaman yanda kuka sani ta kudi ce, don haka gamai bukatan wannan littafi zai turo #200 NORMAL,idan VIP nema duka #200 ,SPC kuma #300 Ta wannan Number

08081202932/09137392680.

*#SHARE TO ANOTHER GROUPS*

*Maman teddy🧸*
*Typing...✍🏻*

🎋🎋🎋🎋🎋🎋🎋
🌹🌹🌹🌹
🌿🌿
*ZUMA DA MAD'ACI*
_*(True love never end...)*_

Na
*Maman teddy🧸*

*Last free page 16*

*______________________________*

*ALHERI WRITERS ASSO.📘🖊️*

*A.W.A*

```Kungiya daya tamkar da dubu,kungiya masu aiki da nazari da ilimi,Alheri sai d'an Alheri💪🏻```

*________________________________*

*بسم الله الر حمن الر خيم*

_Dedicated to my teddy🧸Wannan pagen taki ce y'a d'aya tilo😂._
```

*_Domun samun Littafin Zuma da mad'aci tun daga farkon sa har karshe zaki tuntubi wannan number 09137392680/08081202932._*

Niko da isana falon ne jiki na har dan rawa yake nake cewaa" Sir Khaleed ina son na koma gida yanxu,Oumma na nason gani na".
Ganin yanda nake magana Amma hankali na gaba daya ya tashi kuma buri na kawai na tafi gida yasa Sir Khaleed Saurin mikewa,Yayin da nan Abdoul Manan Yace" Batasan da Zuwan ki ba ko?. Kafin na basa amsa ne Aysha tayi saurin cewa" Wlh kam Hamma bata sani ba,Ai kam Hamma Khaleed kayi maza ka maida ta,gida kaga lokacin tashin su yy shine yasa Oumma kirah".

Murmushi yy mun wanda kan yy mun mgn nayi saurin ficewa daga Falon ina mai nufan Farfajiyan gidan". Haka ya biyo bayana da son ganin ya faranta mun,wato ya mayarda ni gida a wannan lokaci".

Sam ban tsaya bin ta Maryam da gaba daya ranta ya gama kololuwar baci,Amma ya zatayi dole ne ta nuna komai bakomai ba,har Allah ya nuna mata Ranar da zata Mallaki Huday,A lokacin kam ne zata gasa mai Ayah a Hannun sa".

Shiko Huday sai da ya6ata Kusan 30 munite yana mai kallon takardan,yyn da bayan ya fito ne dayaji Suhaimart ta tafi gida,Dariya ya kusa kamasa,don mene yasan Guduwa ne tayi, bawata Oumma da ta kira ta".

---

*MASARAUTAR GOMBE*

Cike da muna funki da tsantsan yaudara da Ha'inci naji muryan Jakadiyya ba cewa" Wannan kuma Ranki yadade,Uwar daki na,za'a sanya masa ne A abincin da In yadawo Zai ci". indai yaci tom zai kwanta jinya mai tsawo wanda babu Uhm,bare Uhu"um don sam baxai iya mgn ba". Kuma bazai kara kwanaki 30 ba,za'ayi basa".

Wani murmushi Fulani ta saki,kan daga bisani takara kishingida tana mai jin dadin maganganun Jakadiyya". Itako Jakadiyya ganin haka yasata cigaba da koro mata Bayani hadi da dauko wata Kwarya datake a Rufe,wannan Kuma zamuyi ma Yarima Abdoul Maman ki ranye ne,wanda damun masa sau uku,gaba daya hankalin sa zai bar jikin sa,kuma komai yake can zai dawo,savoda tsaban saurin yadawo Masarautan tom A hanya za'ayi bashi,don hankalin sa tashin da zai yi,tukin moton nasa vaxai iyah ba,kinga ko ae dole a saki birki akan Kwalta". Murmushin Mugun ta Jakadiyya ta kuma yi,yyn da fulani tace tom in ankirasa ae sai ya amsa in bai kuma amsa ba fah?"

Ranki yadade ko a inah yake karfin wannan magani dole ne ya amsa ko kin mance Uwar sa ce".

Wani kayataccen Murmushi Fulani tayi,tuno da abubuwan dasuka faru shekaru 30 kenan da wanxuwan hakan".

Ganin haka yasa Jakadiyya cewa" Tom dolen sa ya amsa koda kuwa yana kwana kan buzu".

D'an shiru Fulani tayi hadi da tunanin Anyah kaunar da take ma Abdoul Manan zata iya bari a cutar dashi haka? Don Allah yasa kamata Azababben Son Yarima Abdoul din,wanda ita kanta bata son mai yasa take kaunar Yaron kaman jinin ta ba".

Kar kumanta daga wannan Page din Free page ya kare,maza hanxarta wajen biyan kudin ki ki karanta cikin kwanciyar hankali babu Zaullumi, don haka zaki tuntubi wannan Number 08081202932.

Niko Suhaimart tun bayan koma wata gida na rasa Sukuni,sai a yanxu nakejin sam ban kyauta ba,wanda ni har ga Allah bawai na ce inason Huday da wani nufi bane,a'a ni ba wannan son danake mawa Khaleed naje nufin muyi da Huday ba,kuma idan nayi tunani ae wannan bashi ne d first time dana fara fada masa kalmar so ba a rayuwa".
Haka na Zauna na Rafka ta gumi,gashi daya bangaren ta Zuciya ta ina tunanin irin Kaunar da son danaga Maryam na mawa Huday,anyah ban yi cuta ba nace zan Rabasu,nidai gsky ba dani ba". Dole na samar nawa Kaina mafita".

A washe gari kam sam ban isah gidan Hajy.Zaituna da Wuri ba sai da naje Asbiti don duba Ifyn jiki na,wanda sosai Hankali na ya tashi kan maganganun da Doctor Zainab ta fadamun,don a halin yanxu ciwon nawa yafara cin karfin jikina,kuma ta sanar mun da nan da Watanni 1 na kawo kudin Aiki na,idan ba haka ba komai xai iyah faruwa,walau Rayuwata ko mutuwa,don idan sa'in ta Wuce koda da kudin aikin sai dai muyi don jahadin kila yayi kila kuma mutuwar ki". Ta fadi tana kallo na". Kasa magana nayi jiki na lubus yy sanyi,yyn da nan na fada Duniyar tunanin ina zan sami wannan Zunzurutun kudi? Har kusan miliyan da rabi,ina yar talaka".

Tana a Zaune ne sai ga wata nurse tazo anan take sanar mata da shigowar wani Babban likita,aiko cikin sauri tace naje na same shi,don dama tayi masa baya ni nah".

Godiya nayi mata jiki babu kwari na nufi Office din wannan likita danaji ana kirar sa da Dr. Vivan.

Abun da yabani Haushi ya kuma daga mun hankalin, buden bakin sa cemun yy" U must die,saboda ciwon ki ko a yau aka kawo komai da komai da matsalar,sai dai muyi aikin cikin kasada". Nan take naji kirjina ta buga,nidama tuni na cire mawa Kaina Rayuwa,Kallon sa nayi kan nace" Dr. a halin yanxu babu wani magani da xa'abani na ringa sha,saboda Sassauci?.

Bai bani amsa ba,illah fitowa da yayi yana cemun na biyo sa,A haka na dinga bin bayan sa Har muka isa Gaden na Asibitin inda muna A tsaye wani mai ba Flawer ruwa yazo wuce da wani Flower a hannun sa matacciya". Yarda Flowern yy cikin dattin Asibitin yyn da naji muryan Dr. Vivan na cewa" Idan kina son kiga zaki Rayu ko mutuwa,ki dauki wannan matacciyar Flowern ki Tayarda da ita har tafara fitar da iri,da ga wannan lokaci kisani tabbas zaki warke,idan kuma ta mace mgnan dana maki ne".

Yana fadin haka ya juya hadi da bari na anan,Hawaye ne yafara bin kunci na,sai kuma cike da jin Haushuin Dr. nace halan kai Allah ne da kaasan zan mutu ko zan Rayu? tuno dani kaina nasan ciwo na ya tsananta matuka yasani saurin nufan Flowern na kuma dauka na fara takowa ina tuno da abubuwa da yawa a rayuwa ta".

A yanxu na daina zullumin komai namika ma Allah komai nawa,komai ya sameni dama Allah ya Kaddara mun ne". Saka takardan Bayanan da Dr.Zainab tayimun nayi a Jakata,a haka na isa gidan Hjy.Zaituna don babu danan komawa gida na ajiye Flowern. Tun da na shuga Part din nasa na hangosa ta saman Benen sa yana kallo na, wanda tun da na kalleshi yana mun Murmushi na kawar da kaina,ina mai kokarin sassauta natsuwa ta".

A falon shi muka hadu,don zuwan da banyi da wuri bane,duk ya damu haka,saurin sa Hannu yy yana karban  Flowern hannu na dacemun,mai zakiyi da wannan Ai ya riga da ya mutu,Murmushi nayi masa,kan nace inason shine,kuma inason ya tashi daga matacce Zuwa Rayayye".

Kara bin Flowern yy da kallo kan yace mun" Ki bari muje a kawo maki irin wannan komai da kaman sa".

Nan nayi dan Murmushi kan daga bisani nace masa" A'a Sir Khaleed ga Flowern nan na bari a hannun ka,idai kana sona tsakani da Allah,inaso ka Raine ta kuma ka tadamun da ita".

Cike da Rashin fahimtan komai yace mun" Ina kaunar ki Suhaimarh,kuma inshaallah zan tada maki da Wannan Fulawan,babu abun da zai kuma matar dashi ". Nan nasaki murmushi ina cewa" Na gode fah,kaga bari nayi sauri na fara yin aiki na'. Shima nan yace tom nima bari naje nafara aiki na".

Kallon sa nayi saurin yi kan nace"Aiki kuma? wani aiki kenan?"

Nuna mun Flowern dana basa yy,kawai sai nasa Dariya hadi da nufan Coridourn sa,shima dary yy hadi da nufan Gaden nasa dake ta baya".....

Tun daga wannan Rana Kullum Sir Khaleed yana aikin vaima Flowern nan Ruwa,don masu kula da itah yasamar mata". nikam kullum boye damuwa ta nakeyi kar wani yasani kuma ya fahimta,wanda a iyah yanxu har Oumma na tafara dago ni".

Amma haka nake dannewa na nuna mata bakomai".

A wata rana ne,ina a zaune a falon gidan Sir Khaleed ina hutawa,don kammala aikina kenan,Aysha ce tayi saurin shigowa tana kwala kira na".
Tana gani na anan ta zauna tana cewa" Munga ta kanmu Suhaimah wai shin kiniji Yah Huday yace" Zai hakura da Aurar Maryam,nan take naji kirjina ya buga salati na farayi ,wanda kan na bata amsa naji muryan shi a bayan mu yana cewa" Kehh Aysha dama haka kike,tashi ki bani Wuri"!

Jikin Aysha ne ya hau rawa,nan tarasa inda zata nufah,kawai sai ta kutsa kai Bedroom din Sir Khaleed da yau Weekend vai fita ko inah a wannan Rana".

Zama yy akan daya daga cikin Kujerun falon,yyn da ban san lokacin dana zube a gaban sa ba,hawaye na bin kunci na,nan na fara ce masa" Don Allah yah Huday kayi hakuri,kar ka Ki Aurar Maryam, na tuba wlh wasa nake bada gske bane abun dana Rubuta. Indai ni kana sona ka Auri Maryam,baka sani ba ni Rayayya ce ko matacciya,kila ma Bazanga Bikin ba,ammma ina Rokon ka da Allah ka Auri Maryam, taban Tausayi komai zai iya faruwa da ita idan taji wannan Maganan.

Kauda kai yy bai cemun komai ba,muna a haka sai ga Sir Khaleed da Aysha,aiko nan itama Aysha ta zube gaban sa ganin yanda nayi tana kuma basa Hakuri,don ita batasan Dalilina na hakan ba,ta dauka haka kawai ne nake basa hakurin".

Cike da muryan kwantar da Hankali Khaleed ya fara masa mgn,da basa Baki don ganin ya sauko dashi daga abun da ya doru.

Shiko gaba daya Hankalin sa na kaina,ganin yanda nadaga Hankalin a ne ya kalli Khaleed da cewa" Khaleed naji kuma na amince zan Auri Maryam, amma badon ina son ta ba,ko kuma kaunar zama da itah ba". Kawai dai na amince da hakan saboda wata mahanga tawa".

Murmushi duka mukayi yyn da kaman wani Uban mu nida Maryam muka hau yi masa gdy,hadi da tashi muka basu wuri".

Tun daga wannan Rana sam ban kuma hada ido da Huday ba,shiko yy kukan Zuci,musamman idan yana a dakin shi ya dago haton Little din sa,Duk Jarumta irin na mai Suna Aliyu,baya sanin Lokacun da Kwallah yake sauko masa,sai a yanxu ne yake jin wani irin matsanancin Kewarta da Rashinta da yayi".

Haka Momy ta lura da hakan sosai,amma inta tambaye shi sai yace mata" Ya tuno da Little ne,nan Momy itama zata tuno da tsohuwar famin dake a zuciyar ta,haka zata yini tana Zubar hawaye hadi da mata Addu'a".

A kwana a tashi babu wuya gamai yawon Rai,don ana gobe bikin Huday da Maryam ne,iyaye da Yan Uwa na nesa da kusa,duka sun gama kammalah,Hjy. Zaituna kam itace Hajiyoyi don sune manyan iyaye,a wannan kuma Rana aka shurya Mother's Day da duk wasu manyan Hajiyoyi da Kawayen Su da yan Uwa sun Halirta wannan Wuri,wanda tsara shi kam ya tsaru,komai na wajen Abun burgewa ne". Kowa sanye cikin wata Material mai Launin Ash colour. Abun kam yy matukar tsari, Nikam da Aysha bamu halarci wurin ba sai karfe 4pm. Wanda wurin ya cika ya batse,daga nina Iftyhal tasaki wani Murmushi mai kayatarwa hadi da Saurin nufan Part din Da Huday yake".

Don Tun A ranar taga inda ya ajiye wannan Takadda,kuma haka tayi tasaka ido taki dauka ta bari sai yau, don a cewanta idan ya bude ido yaga babu xai tunanin tabbas da akwai wanda ya dauka shiyasa ta bar shi bata dauka ba".

Gaba daya mutanen Wurin bina da Kallo suke kaman wata yar wata da wani, Don kowa tambayar kansa yake ni wacece yar waye ne??.

Haka kam yan matannan kowa ta nufo mu musamman yanda Aysha ta kasance First lady,shi yasa kowa kaga ya taho wurin mu daga nan sai kaji ance ana sona da kawa,haka dai nake ta murmushi,Duk wannan taron banga Amarya ba,sai daga baya har mun samu wuri mun zauna muka fara ganin shigowan Abokan Ango,wanda cike da mmki a xuciyata nake cewa" Dama maxa na halirta kodai sune da iyayi?"

Sai can daga baya bayan anga komai kowa ya natsu ne,sannan wasu gijagijan iyaye mata wanda sun kai su 8 su hudu a gaba hudu a baya suka sako Ango da Amarya".

Duka mikewa akayi ana tafi,hadi da barin Amarya da Ango su Zauna a mazaunin su da'aka tana dar masu,sannan kowa ya Zauna ".

Bin su da kallo nayi,don sosai suka harsa,bakaramun kyau sukayi ba,Maryam kam sai Walwalin zunarai ake".

M.C ne ya fara magana ta hanyar cewa sunai ma kowa mata Akhairy da godiya,kan daga nan don Allah suna bukatar hankulan kowa,don K'anwar Ango nason yima kowa Barka da zuwa da nuna farincikin ta kan duk wanda ya Halarci wannan Taron".

Aiko nan kowa ya kuma yin shuru aba jiran fitowan gimbiyan wato Iftyhal. shiko Ogan nawa Huday sai a yanxu ya hangoni,aiko sai Murmushi yake mun,nima haka nayi ta mayar masa,Khaleed kam nufomu yy yayin da inajin Yan matan Wurin na kirar sunan sa kasa². Har ya karako,don A wurinnan Sosai Yan mata sukayo kamu".

Sanye yake cikin shigar sa ta wata Sky blue din yadi mai laushi da tsadan gske,hadi da saka hular kube,kai nikaina sai danace mashaallh,don bakaramun kyau yy ba,da isowan sa yace Hayatee na kece haka,shine baki varni na fara ganin ki ba,sai da wasu suka gane mun ke??

Murmushi nayi masa,don kunyah ta hanani cewa komai,Sai Aysha ne ta amshe da Amana Afuwa,Sauri ne ya hanamu amma ae ban yarda da kowa yaga fuskannan ba,kaine kafara ganin kwalliyar. Dariya yy hadi da ceewa" Ai kam har kinsa naji sanyi a zuciya ta". Hamma na ka koma bangaren ku nan namu ne na mata". Kan ya bata amsa ne Abdoul Manan da zuwan sa kenan ya jah hannun sa yana cewa" Ai shi yasa Nazo na tafi maku dashi,aiko nan muka sa Dariya, muryan Iftyhal naji yana amo da ya cike Wurin,Godiya tayi ma kowa na halirtan wurin,kan daga bisani tafara da cewa" A yau inaso na sanar da ku wata muhimmiyar magana, akan tmyaudara da cin Amana da Ha'inci,wanda a haka nayi ta barin ma ciki na damuwata har ba bari sai a wannan lokacin zan Amayar".

tako tayi daga inda take hadi da motsawa ta chanja wuri hadi da tsayawa inda zata iyah hangoni da kyau,sai kuma tayi wawan Dariya hadi dacewa" Da akwai wata yarinya wai ita Suhaimah makira mayaudariyya yar gidan talakawan tilis,amma a haka take juya kwakwalan masu ilimi da Arxiki saboda sakarcin su".kowa ana yasan Khaleed da Huday aminai ne,amma a haka sai da tasa Khaleed ya sota,kai bama wannan ba,har ta shi Huday din soyayya suke,don wannan Auren Allah ne ya nufah za'ayi shi".

Hayaniyan maganganun mutane ne ya kwace a wurin,sao kuma Iftyhal tace wannan takadda da kk gani shaida ce na duk maganan danake fada a yanxu". Niko kan wannan lokaci tuni nafara kukan nadaman Halarta wannan Wuri,cikin sauri ta bude Wannan takadda ta soma karantawa,da Ni Suhaimah na yarda kuma na amince da Soyayyar ya Huday, I luv u too". Sai kawai ta sheke da dariya,bakowa bace wannan yarinya illah wancan mai kyaun Aljanun". ta fadi hadi da nuno inda muke zaune da nuno ni,ae tunda tace mai kyaun Aljanu ko hankalin sa ya tarkata a Kaina anan take abun ka ga taron Mata aka fara gulma da nuno ni,itako Aysha da hankalin ta yagama tashi nan tafara lallashi na hankali tashe,tana son gaskata maganan ko sharrin Iftyhal ne, Amma sai muka tsinkayi muryan Yah Huday yana mai cewa" Dul abun da Iftyhal tafadi haka yake,ni nace inason Suhaimart,kuma a yanxu ma na fasa Auren Maryam,bana Ra'ayi kuma babu mai mun dole,dama itace Suhaimah tace nayi Hakuri ba Aure ta,yanxu kuma banayi,ita itadai Suhaiman nake kauna".

Ihu Maryanmm tasa hadi da mikewa kawai sai ta xube anan Wurin,niko da Da gudu na bar Wurin ina mai wani irin kuka mai taba zuciya da ban tausayi,a yau nagama nadaman Amince ma Wa Yah Huday danayi,yanxun ban da makama".

Shiko Khaleed da yakejin kansa kaman ba'a duniyan yake ba ne,yyy saurin biyo ni amma ina kafinnan tuni Na bace na ganin su ".

Haka shima Huday bai tsaya bin takan mutane ba,duka suka biyo bayana,amma sam basu samu nasarar ganin inda na dosa ba".

A haka nasamu na tara mai Adaidaita wanda da isana gida,Oumma na bata nan,kawai sai na shige daki na ina mai kwanciya kan yar filungen katifah na,ina mai xubar da Hawaye da tuno da

komai na Rayuwa ta tundaga Fari..."

*WACECE SUHAIMART*

Wata yarinya ce yar kimanin shekaru 4  a duniya ta fito da gudu tana ihun Murna da kwala kirar Sunan Momy...momy...."

Cikin Sauri Momy Huwaila ta fito daga kitchen don hadin breakfast take masu don tafy school".

Rungumo ta nayi da gudu,yyn da take furta Washhhh Suhaimah so kk ki karya Momyn naki".

Cike da yarinta na d'an turo mata yar micilan baki na,ina mai cewa" Momy Yah Huday ne,ki 6oye wannan kar ya gani...!

Tun da ga kan stairs yake furta plz my littele ki baniiii......

Tsalle nake ina dariya da cewa" No mom"
kar ki bashi duba kiga wai shi yace yafi ni iyawa".

Tomfah muje zuwa,laifin dadi karewa,a yau ne na kammala free page.

Domun samin cigaban Labarin zaki turoNORMAL #200 MTN, Idan kuma SPC kk so #300 ta wannan number
Whatsapp number👇🏻 08081202932.

CALL
09137392680

#Shere to another grps

Mmn teddy🧸